Captain sadiq complete*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*writing by*
*Salma mas'ud nadabo*


*Edit by*
*boold sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

1_2

Yarinya ce yar shekara 10 na hango, tana tafe tana rusa kuka kamar anmata mutuwa.Fara ce sosai, ita ba siriri ya ba, ita ba lukuta ba, Dan kwallinta ne a hannu ta, hakan ya sa na kalli gashin kanta, baki ne sosai amma saboda tsabar datti yayi jawur,kallo daya na mai na gane mai laushi ne,rashin kullawa ne yasa yayi haka, Hancin ta yayi jaga-jaga da majina, gata da manyan ido, tana tafe tana kukan, dan ba dainawa tayi ba, dai-dai wani madaidaicin gida ta tsaya chak, gidan kasane na tallakawa sosai,dan ko kofar gidan bata samu ishashiyar kofa ba.Ihu ta Kara saki kamar an watsa mata ruwan zafi,inna da ke kurya daki ta fito tana gyara zani, inda sabo to ya kamata ta saba da halin fatuha,amma ba yadda ta iya dole ta fito inba fitowa tayi ba to wallahi sai  dai maqota su fito,ganin inna ta leko yasa fatuha tuna a kasa tana ihu,inna ta gyara tsayuwa. "ohni fatuha nabani yau kuma wakika tsokana kika ci bugu? fatuha ciki mirya tsiwa irin na yara masu wayau masu rashin ji ta ce "inna wallahi tallahi kwarankwatsi dubu bani na tsokane shi ba inna. Ta kara rushewa da kuka,inna ta san halin ta sarai shiyasa ta ja bakin ta tayi shuru, to fatuha waya bige ki?"wallah Inna Rabi'u ne  ya bigeni har da taka min ruwan ciki,ta Kara rushewa da saban kuka,"kuma inna billahilazi ba zan yadda ba,ta inda zancan tana katse majina hancin ta.saboda inna ta San karya fatuha take ba yadda za'ayi rabi'u ya bige ta har ya taka mata ruwan ciki, sai dai in laifi ta mai kuma ko bugun ta yayi bai taka mata ruwan ciki qila ma satan mangwaro taje  ya kamata,  "yi hakuri fatuha ki kyale shi kin ji kuma kiga Rabi'u ba sa'an ki bane kin ji diyar baffan ta" "kambuuuu!!! ta zaro manya idanuwan ta "qur'an inna ban hakura  haba" "fatuha yi hakuri Zan baki biyar kin ji"  washe baki tayi kamar ba ita ke ihu da koke-koke ba, "to inna na hakura kwarankwatsi" Inna ta washe baki fatuha ko ba wai har cikin zuciyar ta, ta hakura ba, dan ta dau alwashi se ta Rama bugun da Rabi'u ya Mata haka ta bi inna cikin uwar daka tana matse kwalla da katse majina.

Misalin karfe hudu na yamma fatuha ce zaune tsakar gida wadda take share kwal ba dani ko daya da yake inna akwai san tsafta duk yadda ta so ta gyara fatuha da fita zata Dawo kamar

almajira ko sabuwar mahauciya, saboda tsaban rashin ji ko wanka se anyi da gaske inna ke samu ta dirje ta, fura take sha hankali kwance daga gani fura na kai mata karo dan sai rausaya kai take kamar kadangaruwa, inna ce ta leko daga uwar daka tace, "fatuha yi Sauri ki shirya ki tai makaranta allo" baki ta turo gaba kamar wadda ta tunkudi birji "gaskeya yau inna ban zuwa inna na gaji qur'an kullun Malam dalha sai ya bigeni" ta inda zancan tana matsar kwalla "to fatuha in baki je makarantar ba inaa zaki sauke baki so na siya maki shanun a yanka ranar sauka" washe baki tayi tace, "to inna zani wallahi ko dan ki yanka min shanuwa babba tafi tasu fatsima kwarankwatsi" "yawa yar albarka maza ki shirya hijabin ta dake saman igiya ta janyo ta zura ta fita da gudu inna ta girgiza kai ta dau kwana fura ta Kai madafi ta aje.

Fatuha da ke tafe tana yan surutai wanda ko ni salma bajin ta nake ba, chan ta tsinkayo muryar malam dalha taja birki ta tsaya tana raba ido dan tasan kashin ta ya bushe, dan Ba karamar makara tayi ba, Malam dalha ne ya juyo sukayi ido 4 da fatuha ya kwallo ido "keeeeeeeee!!! fatuha dan uban ki yanzu ne lokacin zuwa makaranta? "shegiya mai Kama da mayu duk kauyan nan kin raina uban kowa" yana huci yace, "yau zaki ci kwafar ubanki wallahi," fatuha dake ta raba ido ta duqa da niyar rarumar takalmin ta ta ruga, muryar Malam dalha ce ta tsinke Mata tunani "wallahi kika ruga sai na sa basiru ya dauko min ke akai" kasancewa tasan basiru Ba karamin kato bane yasa taja ta tsaya chaf ka daya Malam dalha ya Mata yana muzurai kuka ta farayi tana yarfe hannu tana bashi hakuri, Allah annabi amma yayi biris ya fisgota ya fara kila kamar an aiko shi ihu take tana jera mai Allah ya isa bugun ta yake amma bakin yaki mutuwa, dan kan shi ya gaji da dukan ta ya hakura fatsima da ke gefe sai matsar kwalla take tana yimai daquwa ta hijabi ta, lalabowa tayi gefe fatuha ta zauna Malam dalha be ganta ba tace, "yi hakuri fatuha kin ji Allah sai ya saka maki" fatuha dake matsar kwalla ta turo baki gaba "billahilazi sai na rama fatsima ba yana zuwa gidan qilu zance ba da yamma ba kwarankwatsin dubu sai nayi maganin shi fatsima" "Kai fatuha ki kyale shi Dan wallahi ki kai mai iskanci har gida zai biki dan Malam dalha ba wayau garashi ba ya hadaki da baffa" "yo ni ma wayau ne ya isheni" ta karashe zancan tana washe baki fatsima taja bakin ta tayi shuru, haka suka cigaba da karatun su dai-dai gwargwado fatuha na da kokari sai dai bata jin magana KO kadan ba wanda bai san ta akauyan su ba.

Mayan motoci ne kira bentley guda 5 suka nufi wani katafarin gate kallo daya nayi ma motocin na hadiye miyau dai-dai katafarin gida motocin suka kunna Kai wurin parking suka nufa suna gama parking da sauri wasu sojoji guda 4 suka fito daga ciki motar babba at the same time, sojojin 4 na cikin mota baya suka nufi motar tsakiya ahankali daya daga cikin sojojin ya bude mai murfin motar tsakiya wani hadaddden kafa nagani mai sanye da booth yana cikin kakin shi na sojoji karfafe namijine kyakyawa wow fari ne Sol idan sa sanye yake da glass fari wadda ya fido da zala kyan shi, da qwarjinin shi dogo ni sosai jikin shi murde yana da fadandan kirji gashin kanshi mai laushi ne duk da gashi na cikin hula shi na uniform hakan be hana gashinshi bayyana na ba, ga sajan shi kwance da hancin shi kamar pencil dan tsini, briefcase din shi ya amsa hannu daya daga cikin yaran sa fuskarsa murtuke Ba alamar dariya kamar an aiko mai da wahayin mutuwa, na ce ohni Salma da guy dinan zeyi dariya da ba karamin kyau

zeyi ba, haka yaran suka bashi guri ya wuce, Kai tsaya man palour ya nufa wow fadi tsaruwar palour bata lokaci ne saboda ba karamin haduwa yayi ba  baba jummai da ke gafe cikin washe baki ta tsugunna tana kwasar gaishuwa cikin isa kamar mai koyan magana ya amsa tare da cewa, "mom fa? "ah mai gida tana sama" Kara daurewa yayi Dan wannan suna kona mai rai yake a hankali yake taka matataka cikin isa  Kai tsaye dakin mom  ya shiga hadaddan daki mai kyau sanyin AC sai ratsa dakin yake hajiya da ke zaune saman kujera dressing mirror tana shafa turare Tasha hadadden leshin ta mai kyau, fara ce ba fulata na kallo daya zaka mata kasan Hutu ya zauna mata ahankalin ya karaso yayi huging nata cikin fara'a ta juyo Dan tasan ba mai mata haka se son, kiss ya mata yace, "mom I miss u"  "miss u more son welcome back dear, baby ka kara girma kamar ba Kai ba" turo baki yayi ya langwabe Kai alamar shagwaba "Kai mom ni dai  gaskiya ban girma ba" "ka ji da shi dai kaje kayi wanka ka dawo your food is ready a dinning area" "ok mom" ya fice yana murmushi kamar bashine Wanda ke daurewa ba dazu Ba.

*Taku har kullu Salma mas'ud nadabo**CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM🐄*

3_4

Kaitsaye bedroom nashi ya wuce komai na bedroom din golden color ne wani makeken gado ne atsakiya daki Wanda ke kama da ba a kwanciya a saman shi, dan komai na daki very neat ne dressing mirron din shima abin kallo ne kayan shafa ne kamar suyi magana dan yawa, perfume kam ba'a magana da man gyara gashi tsayawa lusafa maku haduwar dakin bata lokaci ne kayan shi ya fara cirewa,
ya shige toilet wow toilet din ma abin kallo ne dan ya hadu iya haduwa baifi  30 minutes ba ya fito daure da towel a qugun shi daya kuma yana goge gashin kanshi da shi, dressing mirror ya nufa ya shafe jikin shi da mayuka masu kamshi tare da gyara sumar sa da sajan shi wardrobe nashi ya bude wow wardrobe din ma abin kallo ne saboda kaya ne a ciki kamar gurin saida kaya, suit kala-kala da uniforms din shi na sojoji kamar suyi magana da yake shi mutun ne ba mai yawan sa manyan kaya bane dan haka kanana kaya sunfi yawa, hannu yasa ya ciro T-shirt din shi white mai gajeran hannu da 3qwatan shi black yasa ba karamin kyau yayi ba haka yasa kyan shi ya bayana sosai agogo ya makala ma hannu shi mai tsada silver na azurfa, har ya kai bakin kofa phone nashi ya fara ringing, wayar kira iPhone 7 white chak ya jaa ya tsaya hannu

ya kai saman dressing mirror nashi sweet mom ne rubuce a screem din phone din ahankali yasa hannu ya dauka, "hello mom" "son na dauka bacci ya dauke ka? "no mom yanzu zan fito" "ok" ta datse kiran daga dayan bangaran cikin isa yake saukowa daga sterp hannu sa daya cikin aljihu Jidda dake dining ce ta rugu da gudu da rungume shi tace, "daddy welcome back daga ta sama yayi yana mata wasa tana dariya har suka qarasu dining tana rike a hannu shi mom sai murmushi take ita tayi serving din su shinkafa ce da miya wadda taji kaji da namomi da ganyaye cikin kwanciyar hankali suke cin abincin wadda sadiq da kanshi yake feeding Jidda itama tana feeding nashi, yarin ya ce wadda baza ta wuce 4 year ba chocolate Colo ce mai kyau da ita gashin kanta yasha gyara sanye take da gwon pink mai dan siririn hannu yadda sadiq ke bata kuluwa hakan zai gwada ma ba karamin ji yake da ita ba, mom dake zauna tana Kallan su se taji tausayin Jidda ya kamata da shi kanshi dan nata Jidda ce ta katse shuru da cewa cikin muryar ta mai tsamin, "daddy Ina tsaraba na? kallan ta yayi yana murmushi ya lakace mata hanci "sweetheart ki bari daddy ya gama lunch mana" baki ta turo gaba "um daddy na kosa naga tsaraba ne" "um na sani swetheat bari mu gama tukun"mom ce ta washe bakin tace, "ke dai baki gajiya duk san da yayi tafiya fa sai ya maki tsaraba" "to ai grandma Ina so ne" ta ida zancan tana turo baki "ke ko Allah ya shirye ki" duk hiran da suke idan sadiq nakan little daughter din shi wadda ya ke jin ta har cikin ranshi, "oya cigaba da cin abinci sweetheart mu gama na baki tsaraba ki sannan muje shan ice cream ko dear" "yes daddy" haka cikin wayau ya samu yayi feeding nata.

Fatsima da fatuha ne tafe antaso daga makarantar allo suna tafe suna tsokana dan wannan ya zamar masu jazaman in antashi daga makaranta se sunyi tsokana san ransu suke komawa gida wata Rana da kuka wata rana da gudu suke kuma wa gida yau kam a guje suka koma gida fatsima ta shige gida fatuha ta shige gidan su baffa ne zaune bisa tabar ma Inna na gefe tana zuba mai ruwa abuta saboda magrib ya kusa fatuha ta kunna kai tare da sallama ta yadda hijabin ta kasa baffa ya bita da kallo washe baki tayi ta ce baffa sannu da gida yauwa yar albarka an dawo daga makaranta kenan eh baffa yauwa ya karatun lahiya lau baffa taje ta amshi buta da ke hannu inna ta kawo ma baffa yayi alwala ya wuce masallaci bashi ya dawo ba sai bayan isha'i inna da fatuha na zaune suna cin tuwan dawa ta miyar kubewa wadda tasha man shanu baffa ya shigo da sallama fatuha ta ruga da guda ta rungume shi ah ah zaki karya ni fatuha wai ke baki san kin girma ba baki ta turo gaskiya baffa ban girma ba to naji ya ja hannu ta suka zauna bisa tabarmar da Inna ke zaune murmushi inna tayi ta tatashi ta shige madafi ta dauko kwana abinci Malam ta aje mai yana samata albarka bayan sun kamala cin abinci fatuha ta kwashe kwanin ta dawo ta zauna kusa baffa baffa na'am fatuha baffa Ina so gobe na bika gona dan Allah makaranta fa fatuha baki turo gaba ai gobe litinin baffa ba ta sahe inna da ke gefe ta ce toh fatuha kin san sai 5:00 Malam ke dawowa ki bari sai ranar alhamis ki bishi kin ji kwalla ta Fara matsewa baffa ya ce yi hakuri ki shirya goban se muje ko washe baki tayi dan ita akwai abinda take san daukowa a gona shiyasa zata bishi inna ce ta katse mata tunanin da cewa haba Malam wai me yasa kake biyewa fatuha dan Allah taita sangarcewa kinga ladingo bana san haka haba dan Allah Allah ya bamu yarin ya sai baza mu faranta mata ba mun dade muna san yara Allah be bamu ba sai yanzu yanzu kuma ya bamu sai muki faran ta mata

gaskiya bazaiyu  ba ladingo ke ma kin fara daukar magana mutanan waje toh yayi ni dai ba maimatsa ma diyata akauyanan kyale shi ladingo tayi ya ida zan can tare da daukar fatuha wadda tuni bacci ya kwashe ta inna ta bishi da ido tare da kwashe tabarmar tsakar gida

After dinner mom da sadiq ne zaune a palour suna kallan news Jidda na kwance  jikin shi da alama tana wasa bacci ya dauke ta Teddy's din ta a baje cikin palour baba jinmai ce ta leko daga dakin ta ta zo ta fara kwashe kayan wasan tana kaiwa dakin jidda dakine mai kyau fadi tsaruwa dakin bata lokaci ne sai da ta gama kwashewa ta zo daukar jidda dake makale da baban ta sadiq ne ya ce ah baba barta yau tare zamu kwana to shikenan maigida bari na mata kwanka nasamata kayan bacci to shikenan ya miqa Jidda  mom ta juyu ta kalle shi tana sanyi magana amma ba tasan bacin ran son shiyasa taja bakin ta tayi shuru can ta ce ni ko baby aikin da baba jinmai take be mata yawa ba gashi ba yarin ya ba ce haka ne mom tunda Mary ta tafi Ba a kawo wata ba ni wallahi mom tsoran daukowa sweetheart wata yar aikin nake wallahi ya ida zan can yana bata fuska  ya zamuyi dole a samo wata  saboda aikin ya Mata yawa to shikenan duk yadda kukayi ki fada min to kun koyi waya da abban ka yes munyi jiya lokacin yana airport yace sai yayi 2weeks zai dawo eh haka kasan har yanzu suna magana kan kwangillannan ne eyya Allah ya taimaka mom ta ce ameen gobe Kai da Jidda in ka dawo daga wajan aiki ka kaita gidan sister ka ya kamata ka leka ka bama su hanan tsaraba su ko tam bari mu gani inna dawo da wuri  sai muje sai ga baba jinmai dauke da Jidda ya amshe yayi  mom sai da safe

*Taku har kullu salma mas'ud nadabo*

*Alheri hausa novel group love u fan's*❤
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM🐄*

5_6

Asuba ta gari fatuha ce ta tashi tunda safe ta fitu daga dan akurkin dakin ta wanda ko lafiyaya katifa bai samu ba inna dake gefe ta na hura wuta ta gaishe ta tare da daukar tulun da ke kusa ta inna ta fice zuwa di ban ruwa rafi gidan su fatsima ta wuce kai tsaye dai dai bakin kofa suka

ci karo ah ta washe baki kai fatsima qur'an na dauka baki tashi ba da billahilazi na higo ruwa zan heqamaki aiko da anyi heqa  heqa  suna tafe suna tsokana magidanta da suka fita siyaya safe har su qarasa rafi yan'mata ne da sa'anin su birjik suna diban ruwa haka suma kusa qarasa duk yarin ya data gansu indai sa'ar su ce sai ta matsa saboda tasan hali in bata matsa ba ta ci na jaki fatsima ce ta hango Rabi'u shi da larai suna tadi fatuha ta zuguru ta nuna mata da baki kin tuna abin da ya mana jiya qur'an ina sane wallahi ai ban yafe mai ba kawo kunnan ki kiji abinda zan mai magana su kayi a kunne wadda ko ni salma banji sannan suka kwashe da dariya kai fatuha billahilazi hiyasa nake sanki wallahi kin san maganin dan iska ta ida zan can tana daukar tulun ta fatuha tayi gaba haka suka jero suna tsokana sannan kowa ce tayi gidan su

Tana  shiga gida inna har ta sheka koko nata na cikin kwannan samira ta Kafa kai ta shanye baffa ya fitu daga uwar daka washe da baki yauwa yar albarka har kin gama dibar ruwan eh baffa na gama kai nake jira mu tafi to bari na dauko fatanya na a buka sai mu wuce to ta ruga da gudu ta dauko hijabin ta suka ma inna sallama suka fita

Sadiq ne  ya futo daga toilet sanye da bathrobe a  jikin shi ahankali ya leka fuskar Jidda da ke bacci yana shafa kanta ahankali ya kai mata kiss a goshi ta bude ido tayi ta sakar mai murmushi daddy good morning morning sweetheart oya tashi muje ayi wanka tam papa daukar ta yayi suka shiga toilet ya wanke ta tas suka fito yana mata tsakulkuli tana gantsarewa tana dariya daddy please stop naqi dear ba daddy zaki ma wayau ba no daddy ba wayau zan ma ba fa to menene to um wani abu ta ida tana hada hancin ta dana sadiq tayi yayi kamar an mintsilai ya ce oya tashi na  shirya ki tam papa mai ya shafa mata ya sa Mata jeans blue n pink T-shirt mai kyau da manyan flowers ya raba mata gashin ta gida biyu ba karamin kyau tayi ba Masha Allah pack ya mata oya wuce wajan grandma ganin zuwa dana gama shiryawa to daddy ta fita da gudu ya bita da kallo shiryawa yayi cikin kakinshi na sojoji tare da gyara sumar sa ba Karamin kyau yayi ba wow duk inda namiji ya ke to sadiq ya kai briefcase nashi ya dauko wanda ke gefen gado tare da ficewa dinning area ya nufa mom good morning morning son how was your night cool mom and your's tare da Kai mata pack same good atsaitsaye yayi break saboda ya kusa makara ya fita yaran shi suka fara qamewa tare da  miqa gaisuwa motar shi wadda Tasha wanki benz fara mai daukar ido ya shige yaran shi ya rufe suka fice daga gidan

Baffa da fatuha ne a gona sai aiki suke cikin jin dadi fatuha na ma baffa hira sosai ya ke jin fatuha a ranshi fatuha ce ta katse shurun da cewa baffa zanyi fitsari to fatuha ki qarasa can gefe kiyi kin ji ki kulla da kafar ki to baffa ta kutsa kai cikin gona sai da tabatar baffa baya hangen ta sannan ta lalaba ta qara shigewa jejin tayi wani sasake naga tana diba ta dana kulewa a leda tana dariya ta matse azanin ta baffa da yaji shure ne ya fara kwala mata kira da gudu ta qara so baffa gani tana hanki yauwa yar albarka yo Ina kika shige yin fitsarin baki ta washe ta qara gyara zanin ta hannuta ya ja suka zauna suna cin dumaman tuwon da inna ta aiko masu da shi suna gama ci bacci ya kwashe fatuha baffa ya ce ikwan Allah har kinyi bacci

kenan ya tashi ya cigaba da aikin shi

Cikin natsuwa yake aikin shi a office din Masha Allah sanyi AC sai ratsawa yake sosai abokin shi majid ne ya shigo ah big man ashe ka shigo yap tun 8:00 hannu ya mika mai suka gaisa ya samu guri ya zauna big man ya mom and sweetheart lafiya lau yauma rigima tamin zata biyo ni taga uncle majid Allah sarki me yasa baka zo min da ita ba haba wallahi tana zuwa nan zata cikani da to much of surutu um kai dai ka sani mutun sai muskilan ci naji din inwannan surutun ya kawo ka to ka fita to ban fita tunda ba kaika kawo ni ba sadiq shuru yayi ya cigaba da aikin shi kiran sallah la'asar ne yasa suka fito su Kayi sallah suka koma bashi ya dawo gida ba sai 5:30 part nashi ya shige ya yayi wanka ya wuce bedroom din mom zaune take sama sofa tana karanta azikar yayi sallama ya Mata pack Jidda ce ta rugu ta bashi hug dady I miss u miss u more dear

After ya gama lunch ya shirya Jidda da kanshi ya ja hannu ta suka je parking space yaran shi har sun taso ya daga masu hannu alama su ka dai zasu kaitsaye gidan Anuty bilki ya nufa

Dai dai wani ma daidaicin gida su kayi parking mai gadi ya wangale masu gate Masha Allah gidan ya hadu sosai plat ne mai kyau su hannan na filin gida suna wasa ganin uncle sadiq ya sasu rugawa aguje suna mai oyoyo ya chabe su yana masu wasa tare suka karasa palour Maman hannan na ganin shi ta washe baki ta qwalawa talatu kira ta kawo mai abin motsa baki dangin su fruit da sauran su har kasa talatu ta duka ta gaishe shi ah baby yau kai na a gidan nawa hala mom ce tace ka zo ah yayi smile oh kina nufi ban zuminci ko kamar hakan dai a'a aunty ke ma kin san bana zaman a naija sosai but now na dawo Nigeria zanrinqa zuwa har saiki gaji dani toh shikenan Allah yas da gaske kake haba anuty billy ya ida yana shagwabe fuska ohni baby wai yaushe zaka daina shagwaba duba fa har da diyar ka budurwa dariya ya fashe da ita ni dai sister kin samin ido wallahi sannan ya kora lemo toh naji na daina um wai ina mai gidan ah bayanan yana dubai ok sai end of is week zai dawo Allah ya maido shi lafiya ameen hira sukai sosai da yar 'uwarsa Kira kirayan sallah magrib ne yasa suka tashi sadiq ya wuce masalaci

Misali karfe 5:30 baffa ya gama komai da yake a gona fatuha kwance kamar meyin bacci dare saboda yasan halin ta in ta kwanta bacci bata San a tashe ta yasasa daukar ta har suka iso gida inna na ganin su ta washe baki tare dayi malam sannu da zuwa tare karbar fatuha da ke sharar bacci baffa daura alwala yayi ya tafi masalaci bashi ya dawo ba sai bayan isha'i lokaci fatuha ta tashi tana cin abinci hira suka dan taba sama sama sannan suka wuce ma kwantan su Inda fatuha ta matsu gobe tayi dan ta aikata abinda ke ran ta

Bayan isha'i sadiq ya dawo yayi salama da sister nashi sannan ya raba ma su hannan

tsarabar su karku  so kuga murna wajan su bayan sun fito haka ya biya da Jidda wajan shan ice cream ya mata siyaya sosai sannan suka dawo tun akan hanya ma bacci ya dauke jidda dan haka tana kwance a kafadar shi cikin sallama ya shigo mom na palour tana kallo ita da baba jinmai  baba jinmai ta tashi washe da baki tare da amsar jidda shi kuma ya wuce dakin shi yasa ice creams din a firijin

Baba jinmai tana zuwa daki tayi ma jidda wanka ta samata night dress nata blue rigar dai dai gwiwa shima yana zuwa daki wanka yayi saboda ya gaji sosai ko da ya fito mom har ta shinfide jidda saman bed kayan bacci shi yasa tare da jawo laptop din shi yana shan coffee ya dade yana aiki sannan bacci ya dauke shi

Kira kiran sallah asuba ne ya tada fatuha baki ta washe kai narantsa da Allah jiya da kyar bacci ya suran yadda na matsu yau tayi wallahi talihi yau Rabi'u sai ya gane kuran shi qur'an ciki sauri tatashi  tayi sallah

Yau dai ba laifi fatuha ta taya inna aiki sosai ba dan komai ba sai Dan tabarta ta fita saida suka gama komai ta gyara zaman zanin ta wadda kullun jiya na leda na habar zanin san ta ce inna zani gidan su fatsima to fatuha karki dade  to inna ta fita da gudu gidan su fatsima ta shige inna fatsima na tsakar gida tana wanke wanke gaisheta tayi ta amsa fatuha ya inna inna lahiya lau ki ce ina gaishe inkin koma gida  to za ta ji inna ina fatsima tana uwar daka to fatsima da ke shara bacci saman tabarma fatuha ta daka mata bugu ke tashi firgigit ta tashi kai fatuha ke banza tashi muje oh na tuna fa Qur'an ban san sanda bacci ya sure ni ba dankwalinta ta daura suka fita suna tafe suna tsoka dai dai wata gona suka ci birki Rabi'u ne gindin bishiyar mangwaro da alamar rake ya gama sha bacci ya sureshi saboda duk ga abin rake zube fatuha lafe jikin bishiyar bedi ita da fatsima suna lekan shi fatsima bilahillazi yayi bacci ta kwashe da dariya ai sai ya ci uba nai quli leda ta ciro daga habar zanin ta tufi Rabi'u cikin sanda ta bude ledar ta busa mai garin ta ruga da guda bayan bedi Rabi'u da ke bacci cikin bacci ya fara jin radadi da susa Ba arziki ya tashi yana sushe sushe yayi zuru zuru su fatuha da ke bayan bishi sai dariya suke sannan suka fito daga nesa ta tsaya Rabi'u ta kwalamai Kira ya waigo ai dama na fada ma kwarankwatsin ba'a buguna na hakura fatsima ta bushe dariya ka je gida mai tafasa tama magani kaji rabe ya dago idanun shi sunyi jaaa bala'iiiii Zan ci uban Ku dama  kune kuka fesa min asosa narantse na sha magani sai na zo har gida na ci uban ku yo Zan can banza ko ka zo mukarama wani injin fatuha taja hannu fatsima suka bargun suna dariya shikuma Rabi'u na soshe soshe

*Taku har kullu Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*

*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
(We the best)

7_8

Soshe soshe Rabi'u ke yasha wuya sosai idanunan sunyi jawur sai ihu yake ado ne zai wuce ya hango shi yana birgima ya qaraso subhalillah lahiya Rabi'u me ya faru wallahi fatuha yana ihu haka malam ado ya taimaka mai ya kai shi gida jikin nan nashi yayi jawur abunka da ba fulantanin mutun inna maitafasa tana gyaran tafasa taji sallamar Malam ado ta tsame hannu ta dake cikin tafasa ta yafa mayafi lahiya Malam ado me ya sami Rabi'u ni dai wallahi ban Sani ba amma da alama sosa ce toh fa kai ko Rabi'u mai ya hada ka da sosa garin ya haka ta faru ta ida zan can tare da riqe haba zani tana matse kwalla cikin murya wanda yasha wahala ya ce inna wallahi fatu ce da wannan iskancin kambuuu alqawalin Allah ban yadda yau sai naga uban ta jauro billahilazi ta idaa zancan tana yarfa hannu sama Malam ado ya ce a daiyi hakuri yarin ya ce yarin ya uban wa tana dafe qirji yarin da aure yau haihuwa badi shegiya yarin ya mai Kama da mayu wallahi Malam ado ban hakura shigo da shi namai magani na je na samu uban nata haka aka shigo da Rabi'u yayi zuru zuru aka shinfide shi bisa tabarma

Qur'an fatuha baki da mutunci yo ni ta wasa ce ai dama na fada maki saura malam dalha ai qule nake da shi kwarankwatsi hehe kai qawata ina san ki qur'an fatuha ta washe hakura nima haka billahilazi haka suka dawo gida ko da suka dawo gida fatsima gida ta wuce gidan su fatuha ta shigo gida da sallama yau zuciyar ta fes take da farin ciki inna da ke shara ta amsa sallama ta kauda kai yanzu Dan Allah fatuha kin kyauta kenan tunda safe da kika fita sai yanzu zaki dawo bata idaa rufe bakin ta ba mai tafasa tayi sallama cikin tsiwa inna ta amsa keeeee!! ta cakumo wuyan fatuha inna ta ce lahiya mai tafasa lahiya lahiya kenan bari uban ta jauro ya zo billahilazi yau ban yadda kuma duk abinda ya samu daa na ke ce ni zaki kashe ma daa har kin isa inna sai bata hakuri take amma taqi sakin fatuha wanda tayi wiki wiki da ido dan tasan tayi baki ta turo gaba ke ki cika ni tare da finci ke kanta daga ruqwan da maitafa ta Mata yo ba dan naki bane jiya ya bige ni ba kuma na Rama yau ta ida zancan ta murguda baki dan uban ki in zaki rama saiki samai a sosa inna ta ce fatuha ince jiya ban maki magana ba yo inna jinayi ban iya hakuri ta fada cikin tsiwa haka maitafasa ta gama zage zagen ta da kumfar baki ta tafi acewarta in Malam jauro ya dawo zata zo ta same shi

Daddy please muje shan ice cream sweetheart akwai a fridge muje na baki ok papa thank you ya lakace mata hanci that is my angel ta washe hakura part nashi ya kaita ya bata ice cream shi kuma ya shige gym room nashi ya dade yana gym sannan ya fito riqe da towel a hannu shi yana goge zufar fuskar shi gefen da Jidda take ya kalla har tayi bacci ahankali ya

karasa saitin fuskarta yayi kala tausayi my angel I now you miss your mom why kausa me yasa kika tafi kika barni nida Jidda why kausar yana maganar kamar zautace yana share hawayan fuskarshi I miss u more my wife naso ace yanzu kina ganin angel my wife dake take Kama sosai naso ace tare zamu bata good caring ya kai lips din shi dai2 goshin Jidda ya mata pack

*Asalin labari*

Malam idi zaunan dan kauyan Kano ne wato rano su fulanine sosai Allah yayi ma malam idi rufin asiri dai2 gwargwado yana kiwon shanu sosai har ma da kaji gashi mutu min kirki shiyasa kowa ya sanshi a kauyan rano yana da mata tani sosai yake san tani Allah ya basu ya'ya 3 maza 2 mace 1 kabiru shine babba mai bimai Ibrahim sai rukayya

Zaune suke zaman lafiya cikin kauyan inda lokacin kabiru ke aji shida na secondary shi kuma Ibrahim aji 5 rukayya na aji 3 sosai suke karatun su saboda Malam idi mai san karatune

Akwana atashi ba wuya wajan Allah yau garin rano zaman lafiya yayi qaran ci saboda barayi na zuwa su kwashe ma mutun dabobi sannan su kashe ka kai da iyalan ka Malam idi ne ya shigo gida cikin sallamar shi tani da ke wanke wanke ta amsa ince dai malam lafiya wallahi tani kauyan nan ba lafiya kabiru da ke uwar daka ya leko sukayi tsaitsaye can idi ya yanke shawarar saida dabobin shi su koma birni cikin garin Kano ba yadda idi ya iya haka ya saida shanun shi cikin ikwan Allah ya samu kudi mai yawa ya sama masu ma dai2 cikin gida a rijiyar zaki sannan yaba abokin shi Malam tanko kudi Wanda ke birni ya samai shago a kasuwa kwari a zuba komai ciki ya tataro iyalan shi suka dawo cikin garin kano lokacin Ibrahim ya gama secondary da yake Ibrahim yaro ne mai San karatu result nasu na fitowa ya sami admission a biyuke idan yake karanta business admin shikuma kabiru ya cigaba da kasuwan ci tare da mahaifin su sosai suke samun rufin asirin su

Kwanci tashi asarar mai rai yau Ibrahim ya gama karatun shi inda ya samu aikin kwangila sosai yake samun cigaba inda ya hadu da Hauwa'u auran soyayya ankai amarya rijiya zaki kusa da gidan kabiru inda yake zaune da matarshi Aisha tsakanin amarya da Ango soyayya sosai suke zubawa bayan wata biyu hauwa'u ta fara laulayi sosai take samun kullawa wajan mijin ta da surukar ta har ma da Aisha matar kabiru lokacin rukayya na FCE cikinta ya shiga watan haihuwa bata wani sha wahala ba sosai ta haihu dan ta mai kyau sosai ibrahim yayi murna sosai

Kwana bakwai da haihuwa akayi suna inda yaro yaci suna idiris wato suna Malam idi Ana mai lakabi da jawad sosai Rana suna anyi shagali bayan she kara biyu ta kara samun wani cikin lokaci Ibrahim yayi kudi sosai ya qara murjewa shi da Hauwa'u daka gansu kaga Hutu inda yake

ba Hauwa'u kulawa sosai har ta haifi diyar ta lafiyaya rana suna taci Bilkisu sosai suke samun kulawa wajan iyayan su

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏽‍♂️

*writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM 🐄*

9_10

Yau kusan shekara 2 da haihuwar bilkisu inda Alhaji ke sa ran Hauwa'u zata samu wani cikin amma shuru hakan yasa hankalin shi ya tashi musanma shi alhaji Ibrahim mutun ne mai san haihuwa ne haka suka cigaba da rayuwa cikin so da kauna inda alhaji Ibrahim yake faranta ran Hauwa'u amma cikin zuciyar shi nan maqale da San yaga ta qara haihuwa gidan su ko na rijiyar zaki sun rushe shi sun ginawa iyayan nasu katafarin gida mai kyau family house

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin jin dadi da san juna yau shekarar Hauwa'u 3 ba ciki kuma yau ne tatashi da wani irin zazabi da ciwo kai sosai hankali alhaji ya tashi haka ya kai ta asibiti akai mata yangwaje gwaje inda aka shedawa alhaji Hauwa'u na dauke da juna biyu zo kuga murna wajan alhaji baki har kunne ya daura cikin san duniya haka suma ya'ya nashi saboda basu da burin da ya wuce momin su ta haihu su shasuna locakin itama Anuty aisha nada ciki matar kabiru zo kuga yadda surukar su ke basu kulawa da nuna masu soyayya duniya ta zamar masu sabuwa yayin da mazan nasu ke rawar kafa kan cikin

Cikin su na da wata 7 akayi bikin rukayya da mijin ta aliyu ansha shagali anyi bidiri sosai ankai amarya kaduna GRA

Akwana atashi ba wuya wajan Allah yau safiyar lahadi Hauwa'u tatashi da naquda kaitsaye asibiti suka wuce tahaifi tsalalen dan ta namiji kyakyawa murna wajan alhaji Ibrahim ba'a

magana d Aisha ta zo barka da tsoho cikin ita da kabiru sun dade sosai asibtin ita ma aisha tunda safe take jin naquda tana daurewa kasan cewa ita haihuwar farko ne saboda sun dade basu haihu ba basu suka fara shirin barin asibitin ba sai dare a dai 2 bakin kofa ta fara naquda nurses suka aka batataimakwan gagawa Alhamdullilah itama ta Haifi san talelen Dan ta namiji zo kuga murna wajan su ba'a magana ba a salame su ba sai washe gari da fase  Murna wajan family ba'a magana kamar ranar aka fara haihuwa 7 da haihuwa akayi gagari min suna a family house nasu inda dan Ibrahim yaci sunan kakan shi na wajan mahaifiyar shi wato *Abubakar sadiq* ana mai lakabi da baby shi kuma dan kabiru *Abdulmajid* sosai anyi bidiri anzubar da kudi yadda ya kamata bayan suna da kwana daya alhaji Ibrahim ya koma katafarin gidan shi daya tsara a sultan road sosai gida ya hadu inda duk wani abin morewa na rayuwa akwai agidan sosai kowa ya tayasu murna

Bayan she kara biyu sadiq yayi wayau sosai bashi da aboki sama da majid inda aka dau San duniya aka daura mai yaro kullun kara kyau yake kamar dan laraba kowa bama sha'awa yake amma sai Allah ya daura mai qiwuya kamar me gashi abu kadan bai isa yasasa dariya ba idan kaga yana dariya to yana hannu mom ko abba to wannan dariya har qyaqyatawa

20year letter wani kyakyanwan saurayi ne shida wani shima ba laifi ya hadu Ba kowa bane sai sadiq da majid awajan shakatawa sosai suke hira cikin jin dadi lokaci sun gama makaran ta har sun fara aiki su na sojoji sosai suke jin dadi wasu yan 'Mata ne nesa dasu sai Kallan su suke ba kowa ba ce sai kausar da kawayan ta suma sunzo san iska nana ce ta zuguro ta wow kawata kalli wayan  can guys din sun hadu sosai kamar bazata juyo Ba tana juyowa sukayi ido hudu da sadiq takenan zuciyar ta fara har bawa wani irin sansa da kaunar sane suka kama zuciyar ta lokaci daya haka suka bar gun tana cike da kaunarsa da begen san shi shiku be ma San tanayi ba gida suka koma suma tun daga ranar kausar ta rasa na tsowarta duk wata hanya da tasan zata ga sadiq ita take bi ta sha wahala sosai kamin ta samu number shi tun tana kira be dauka har ya fara dauka suna dan taba shi

Haka rayuwa ta cigaba ta tafiya soyayya mai karfi ta shiga tsakanin kausar da sadiq har ta kai ga iyayan su sosai iyayan sun ji dadin haka murna wajan kausar da sadiq ba'a magana musanma kausar da ita ta cusa kanta ga sadiq din shirye shirye biki ake sosai inda kowa ni gida ka leka abubuwa ake gudanarwa sosai ranar asabar aka daura auran *kausar Umar and sadiq Ibrahim* sosai kowa yayi murna ankai amarya gidan mijin ta dakee sultan road gida mai kyau sosai wanda daga gidan su ba nisa zuwa gidan su sadiq

Sosai sun raya wannan dare nasu da sunna manzan Allah (S A W) bayan komai ya wakana tayi kuka ranar har ta gaji saboda sadiq ba qaramin namiji bane dan ya dirje ta yadda ya kamata shida kanshi ya taimaka Mata tayi wanka sannan ya bata tayi na tsari ranar ko yasha shagwaba har ya gaji sosai yake Samata albarka kasan cewa ta zo mai da budircin ta har gidan

shi sosai yake jin kaunar ta wani irin so suke ma juna su kamar su cinye juna

2years letter kausar ce asibiti ita da doctor kuka take mai sosai wallahi doctor bazan iya jurewa rashin haihuwa ba saboda ko ban haihufa ba wannan ciwon zai iya kashe ni kowani lokaci wannan cuta anemia inasan na haihu doctor bana naso sadiq yasan cewa Ina da wannan ciwo why kausar ya kamata ki sanar da mijin ki ko shine yaji haka zai tausaya maki be taba yadda ki zauna da wannan cikin saboda wannan cikin ajalin ki ne bawai nasan gaibu bane amma duk wani mai cutar anemia bai iya daukar ciki ki duba ki gani ke kanki duk month sai anmaki karin jini bale kuma yanzu har da baby a jikin ki wani irin kuka mai ban tausayi ta Saki gaskiya doctor bana iya zubar da cikina doctor bana iya zubar da jinin sadiq no I can't doctor turo kofar da akayi ne yasa doctor saurin miqewa kausar kuma tayi sauri fara goge hawayanta da bayan hannu ta tare girgizawa doctor kai alamar karya tona Mata asiri washe bakin karfin hali yayi congratulation sadiq matar ka na da juna biyu what ya zaro ido yana washe baki thank you god tare da kai ma kausar hot kiss a lips dinta yana shafa cikinta murna yake sosai inda doctor ke ta binsu da kallan tausayi sosai sadiq yayima doctor tukwici kaitsaye gidan mom suka wuce suna shiga da sallamar su kausar sai sunne kai take kafadar mom ya daura kan shi tare da lunshe ido jawad da ke zaune da yake ya zo da iyalan shi Nigeria kasan cewa shi ba kasa yake zaune ba yana zaune a London da matar shi da danshi jawahir Wanda ke da shekara3 yana zaune saman three star wai yaushe zaka girma ne baby hhh sai ranar da my wife ta haihu ka fara qirga month daga yau am going to be a father wani irin dadi ne ya lilibe mom ita ko kausar sai sunne kai take da jin kunyar abinda sadiq keyi da tausayin kanta kuma Bilkisu ce ta dungure mai kai ita lokacin hanan na da 6year kai dai baka da kunya wallahi ah ki kyale min da tome dan ya fadi min yauwa mom love u ya kaimata pack a cheeks mom ko ta zage sai nan take da kausar ita da Bilkisu da matar jawad sosai suke gwada mata soyayya hakan yasa ta shige toilet tayi kuka ta gaji tabas tasan tayi dace da dangin miji burinta bai wuce ta haihu ba tasan zasu riqe mata amanar babyta tare da shafa cikin ta tana share hawayanta da bayan hannu ta

Sosai take samun kulawa da so da kauna wajan sadiq inda yake gwada mata tsantsar soyayya har take jin dama karta mutu ta dangwama dashi a gidan duniya in ta tuna haka kuka take sha sosai sannan ta share hawayan ta cikin ta har ya kai wata 5 bata samun wata matsala ga kuma sadiq da ke tatalin ta kamar akwai

Sadiq ne yana facing dress mirror yana shiryawa cikin uniform nashi ba karamin kyau yayi ba kausar ta qaraso wajan shi tana sanye da night dress nata Fara dai2 gwiwa habibina na'am honey um tana gyara masa mabalin rigarshi gaskiya kayi kyau sosai ko eh mana ta shagwabe fuska Allah yasa kar yan'mata su kalle min kai hancin ta ya ja honey bame kalle miki miji kinji tam ya kai hannu ya shafa cikin ta ya lafiya babyna lafiya shi lau habibi smile ya saki mai sanyi yayi kissing goshin ta da cikin ta mika mai briefcase nashi yana fita da gudu ta shige toilet ta

fara aman jini jini ta hancin ta jini ta bakin ta jiri take gani sosai har bata iya ganin gaban ta a dadafe ta rarafa ta hau gado tana nunfashi sama sama

Har yayi nisa da gida ya tuna yayi mantuwa ribas ya ci ya dawo ko da yayi sallama bai ji motsin kausar ba daki ya nufa a tunanin shi bacci ya dauke ta musanman yadda ya lura cikin mai sata baçci ne lulufe take cikin blanket sai kyarma take ya shigo dakin har zai fita ya dawo yaye blanket din mai zai gani kausar ce a sume sai hancin ta da jini ke biyowa sosai hankalin shi ya tashi daukarta yayi kamar baby duk ya rode ya sakata cikin mota kai tsaye asibitin wajan aikin shi suka wuce wato na sojoji ya isa nurses suka fito suka basu taimkwan gagawa shiku sai zarya yake doctors sun dukufa akanta domin ceto ranta mom ya Kira yana kuka kamar qaramin yaro yana fada Mata yadda akayi aiko mom ta shirya ita da baba jinmai suka taho asibitin sosai mom ke kwantar mai da hankali kausar wajan laida biyar tasha na jini biyu na sadiq biyu na jawad daya na majid sosai hankalin su ya tashi doctor ne ya fito daga dakin yana goge zufar fuskar shi da sauri suka karasa doctor lafiya dai ko lafiya lau munshawo kanta da kyar yanzu tana samun Hutu ne shikenan sadiq ya Kira da yayi zuru zuru harda yar rama yini daya yayi ya ce yace ka same ni a office to yakub cikin sauri ya bishi suna shiga yakub ya cire glass nashi gaskiya sadiq ka bani mamaki ya za'ayi ka yadda matar ka ta samu ciki bayan kasan tana da *amenia* why sadiq what zunbur sadiq ya mike yakub ban gane mai kake fadi ba Ina tunanin kunnena bai ji dai2 oh karka raina min hankali mana kana nufin bakasan tana da shiba ko mai wasu hawaye ne masu zafi zuka zubo mai why kausar me yasa zakin min haka kuka yake sosai har saida yakub ya tausaya mashi ya rugume shi yana shafa mai baya alamar lalashi ahankali yake magana cikin sarkewa harshe yakub I don't no kausar na da *anemia* ban sani ba me yasa daza boye min why yakub she no I love her Allah nafi Santa akan baby serious yakub please ka cire Mata cikin please bana iya rayuwa bada kausar ya Kara rushewa da wani kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro sosai yakub ke lalashin shi har ya samu ya samu natsuwa ya bashi fresh milk mai sanyi yasha ya rage kuna da zuciyar shi ke kamai ahankali ya fita daga office din ya shige dakin da akwantar da kausar tana kwance fuskar nan tata tayi fayau alamar ciwo ya cita sosai kallo daya yamata idanunin shi suka ciciko da kwalla jikin Mom ya fada cikin dashashiyar murya ya Fara ba mom labarin abin da ya faru sosai mom ta girgisa itama har da yar kwalata mom me yasa kausar zatamin haka mom ya Kara rushewa da wani saban kuka kamar karamin yaro

*ALHERI HAUSA NOVEL*📚📚📚. *thanks for your comments love u all fan's*

*Taku har kullu Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister jeeda*

📘 *REAL HAUSA WRITER'S FORUM*🐄

*👏🏼Godiya ta musanman ga rahama nalele marubuciyar YAR BIRNI KO YAR KAUYE 😍data bani qwaringwiwa wajan rabuta wanan novel din Allah ya bar zuminci* 💃💃

11_12

Turo kofar da akayi ne yasa.. "Sadiq tsagaita kukan da yake... "Abba ne tsaye bakin kofa cikin sasafar ya qarasa wajan abba ya qara sakin wani aban kukan.." "Abbane ya rugume shi alamar lalashi ."shhh!! Sorry son be are strong man sai ka ce ba soja insha Allah she will be fine... "Jawad ka kaishi gida ya samu hutu kaji.." Daddy.. Shhhh.. Ya isa kaji jawad ka kai shi gida kawai..

Haka ko akayi jawad ne ke driving nasu cikin motar ba wanda yayi ma wani magana sadiq idanun shi a lumshe har suka iso gida bala mai gadi ne ya bude masu gate tare da jajanta masu parking space yayi parking.. suka fito a tare..bedroom din sadiq suka shiga ya kwanta saman bed tare da lumshi idanun shi zuciyar na wani irin suya take mai musanman inya tuna da halin da abin kaunasa ke ciki... Jawad ne ya katse mai tunani ta hanyar shafa sumar kansa.... "Ahankali ya ware sexy eye's ball's din shi kan jawad riqe yake da glass cup da fresh milk a ciki.. " Sadiq please ka daure ka ci wani abu nasan tun breakfast din safe baka qara sa komai a cikin ka ba" please ka gama ka sha magani headachen nasan yana damun ka... "Numfashi ya ja yace...insha Allah wife naka zata samu sauki kaji baby.. " kamar Ba zai sha fresh milk din ba amma saboda be ga wasa a idan yayan nashi ba ya amsa... "Sha biyu zuwa uku yayi ya aje saman stool ya qara lumshe idan shi maganin headache jawad ya badu tare da ruwa ya bashi ya sha.. "Sannan ya lulube shi da blanket ya fita...

Bacci ne mai nauyi ne ya dauke shi.. " bashi ya tashi ba sai yama liqis wanka yayi yasa Jean's n t-shirt bleu mai dogan hannu sannan yayi sallah la'asar... "ba qaramin kyau yayi ba sai dai fuskannan fayau saboda kukan da yaci sannan cike take da alamar damuwa car key nashi

da ke saman stool ya dauka ya fita.."kaitsaye asibiti ya wuce yana parking motar shi a harabar asibitin aka fara kiraye kirayan sallah magrib.. Masallaci ya shiga yayi sallah zai futo kenan suka hadu da abba kausar.. " hakuri yake ta bashi ankan cewa bai San kausar bafa fada mai larurata ba..'ah ba komai abba... "Toh shikenan Allah ya bata lafiya..." Ameen.!! Kai tsaye dakin da a kwantar da kausar ya shiga mom na saman daduma tana lazimi.. Gaisheta yayi ta amsa.. " sosai taji dadin ganin sadiq haka ba kamar dazu Ba. Kausar ya kalla Wanda ke kwance saman gado kamar gawa oxygen ne ahanci ta sai jini da ake qara mata idanuwan sane suka ciciko da kwalla tabas yasan ya rasa kausar ya rasa mata.. Tagari why me yasa zaki mana haka kausar hawayan da ke Neman zubumai ya hadiye... "Mom ce ta katse mai tunani da cewa.. Baby ni zan wuce ka kulla da ita anjima matar jawad shukura zata kawo maku dinner .." Son please ka rage damu wannan tare da shafa mai gefe fuska kamar jira ya ke hawaye suka fara mai zarya..shhh!! Ya isa mana inkana kuka ita kuma me zatayi sokake ka tada ma kausar hankaline baby.. Girgiza kai yayi tare da daura hannushi kan na mom.. "Toh ko Kai fa inkasan kuka zaka cigaba dayi to sai mu koma gida Bilkisu ta kwana da ita.. "Um mom bazan sake kuka ba wasu sabin hawaye ne suka zuba mashi..." Mom nara yanda zanyi control kai nane mom nasan sarai na rasa my wife saboda wannan cikin... Ya ja numfashi mom kausar bata iya rainun cikin nan mom ki duba ki gani ita kanta duk month tana buqatar jini bale kuma yanzu data ke tare da cikin ya ida zancen hawaye na zubu mai... Mom ce ta share kwalla idan ta.." son ya isa haka kayi Mata addu'a insha Allah lafiya lau zata raini cikin ta har ta haihu kaji" kai ya gyada' mata.."pack ta mai agoshi sannan tamai sai da safe

Gashin kanta ya shafa ahankali tare da kai mata pack.. "Allah ya baki lafiya mai wife sannan ya daura kanshi saman gadan.. ahankali take bude eye's balls din ta.. " tasauke su kan sadiq da idanun shi ke lumshe kamar meyin bacci" A hankali takai hannu ta saman sumar shi tanajin wani san mijin ta na qara narke mata a zuciya..hankali ya dago sexy eye's ball's din shi ya sauke a kan wife din shi .. Murmushi ta saki tana qoqarin tashi zaune.."no ki koma ki kwanta kiji my wife ya ida zancen yana shafa cheek nata.. "My wife me yasa kika boye min sick naki why? Idanun tane suka ciko da kwalla ta bude baki zatayi magana.." Shhhh ya hada bakin su waje daya yana Mata salan sa mai kashe Mata jiki..

Rayuwa haka ta cigaba da tafiya sosai kausar ke samun kulawa wajan sadiq inda suka bude babina soyayya.."soyayya suke sosai kamar su cinye juna su inda duk month sadiq sai ya kaita asibiti an qara Mata jini..

Misalin qarfe 3 na dare sadiq kwance kausar na manne aqirjin shi.. ahankali yasa hannu yana cire Mata hula da ke kanta Wanda bata bari ya cire mata..."wasu siraran hawaye ne suka zubo mai saboda kusan rabin gashin ta ya zube saboda wannan ciwon..."kuka ya sha sosai cikin daran sannan ya tashi yayi sallah ya nemamata samun sauqi wajan Allah .. Tabas yasan ya rasa kausar ya rasa wani Bari na rayuwarsa da irin wannan tunanin bacci ya dauke shi!!

Akwana atashi ba wuya wajan Allah yau kausar cikin ta ya kai 9month..sadiq ne akwance yana bacci ya fara jin.. Wash sadiq zunbur ya tashi hankali tashe... Kai tsaye asibiti suka wuce nurses suka kawo masu taimakwan gagawa.. Gaba ki da'ya sadiq ya rude har da yar kwallan shi.."waya ya curo ya kira mom ya fada Mata cikin muryar kuka.. Zirga2 sadiq ke yi ya kasa zaune ya kasa tsaye.. "Majid ne ya dafa shi cool down sadiq tare da rugume shi alamar lalashi.." Doctor's ne kan kausar sosai suke aikin su dan suga ta haihu da kanta amma abin ya gagara.!!

Doctor yakub ne ya fitu yana goge sumar face nashi.. da sauri sadiq ya karasa wajan su da mom da majind..a tare suka jefa ma doctor yakub tanbaya.. Ya kausar da sauki..muna kan bakin qoqarin mu ga wannan paper *captain sadiq* kasa hannu kausar ta kasa haihuwa da kanta.. "Jikin shi narawa ya amshi paper yasa hannu aka shiga *tiyata* tun dare ake abu daya sai da safe suka fito daga mom har sadiq ba Wanda ya rintsa addu'a kawai suke.. Bayan ta haihu doctor ya sheda masu ta haifi baby girl murna wajan su mom ba'a magana da sadiq

Kwance take a daki ita kadai tasan radadin ta take ji wasu hawaye ne masu zafi suka zubu Mata tasa bayan hannu ta goge.. Gefe da baby take ta kalla jin an bude kofar ya sata da'go eye's ball din ta wani lalausan murmushi ta saki tana qoqarin tashi... "Ya qaraso my wife tare da kai Mata pack a goshi yana qoqarin maida hawayan shi.."Habibina cikin sanyin murya" Baby bin sadiq ya dauko ...Masha Allah baby mai kyau da ita habibina.. Na'am" ga amanar baby mun na baka please ka kula da ita..."shhh insha Allah tare zamu raini baby mu yana qoqari boye hawayan da ke maqale a idan shi .."um ta kai hannu ta shafa sajan shi mai laushi tace.. Wani suna zamu sama baby mu.. Lalausan murmushi yayi yace..Hauwa'u suna mom za'a riqa Mata laqabi da Jidda... Fada'da' murmushinta tayi tace Jidda ta shafa cheek din baby.. Hannu ta ya riqe ya sunbata.."tarine ya subuce mata jinine ya fara bi Mata ta hanci da baki da sauri sadiq ya mike zai Kira doctor..hannu sa ta riqe tana girgiza tana motsa baki can yaji jikinta yayi sanyi......"Nooooo.. ya fadi kasa sumame

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

15_16

Shirye shirye ake sosai kasan cewar yau ALHAJI Ibrahim zai dawo daga UK... Sosai mom ke gyara kanta kasan cewar mom irin matan nan wanda girman be hana su gyara kansu wajan miji..."abinci ne kala kala anyi domin abirge Alhaji yau kusan 2week baya nageria..

Daddy daddy please wake up daddy....saman ruwan cikin sadiq jidda ke tsale tana kiran suna shi..."oh no angel so kike daddy yayi ciwo ciki ah bakya ji ko.... Tsakulkuli ya ke mata tana dariya...."daddy stop please..ta ida zancan tana mai da numfashi... Tsakaitawa yayi da yimata tsakulkuli... Um my angel me ya tashe ki haka da wuri har kina so ki hana daddy bacci bayan kin san today is weekend ya ida zancan yana langwabe kai ala dole yima jidda shagwaba yake... ohni salma shi dai shagwababe ne ko da yake dan auta ne... Lol" um'um daddy grandpa ne fa zai dawo yau tana maganar tana wasa da maba'lin rigar sadiq na bacci... Inyee little princess of grandpa ya laka ce mata hanci..dady I miss grandpa.. "I now angel yau zakiga grandpa har ki gaji ko angel...yes daddy.."oya tashi muje na maki wanka na maki make up kifi hanna kyau ko...washe baki tayi.."good girl ya dauke ta suka wuce bathroom.....

Inna.. inna.. Na'am.."ohni fatuha wai yau she zaki girma ne Dan Allah mutun shekara goma shadaya amma mutun kullun girma yake yana cin qasa....yi hakuri inna wallahi zanina nake nema inna wanda baba jinmai ta siyo min abirni...ah yau antuno da baba jinmai kenan to zanin yana uwar daka... "Washe baki tayi.." eh inna Qur'an na matso ta zo kwarankwatsi inna...."ai zata zo insha Allah aikin san duk qarshan shekara ta ke zuwa..."amshi kwanan ki kaima baffa kinji .."to inna.. Baffa na zaune saman tabarma ta aje mai kwanan tare da gaishe shi washe da baki ya amsa.... "Fatuha yan'mata rufe fuskarta tayi ita ala dole kunyar baffa take ji ....."Qur'an baffa ni ba yan'mata ba ce su tanine yan'mata....." Hhhhh alalai diyar baffan ta ke ma ai yan'mata ce matso mu ci abincin tare nasan baki ci ba saboda baki iya cin abinci ke ka dai kuma inna nasan batayi Kala ci ba..toh baffa matsowa tayi tana cin abincin inna ta shigo washe da baki ..Kai dai Malam baka gajiya da shagwaba fatuha da girman ta amma har yanzu tare kuke kalaci baka bari muci tare....ah ke ma in zaki ci ki zo muci nasan kishi kike mun ware ki ke ka dai...murmushi inna tayi ta zauna suka cigaba da kalaci...

Misalin karfe 1:00pm fillet din su Alhaji ya sauka a hankali yake takowa ta matatatkal jirgin da kagan shi kaga babba mutun sanye yake da shada blue babba riga anmata aiki da dark blue zare sosai dikin ya haushi sosai.....sadiq ne jingi ne jikin motar shi Benz black qadan qadan ya duba agogo... Dago kai yayi yana kale kale can ya hango abba washe baki yayi ya qara sa da

sauri ya rugume shi abba..."abba I miss u... "Miss u more son tare da shafa mai gefan fuskar shi... Bude mai moto yayi ya shige shima ya zagaya ya shige driver ya jasu....

Mom ce zaune a bedroom saman sofa tasha danqareran leshin ta green mai ratsin white flower anmata bubu da leshin mai kyau tasha dauri ture kaga tsiya gashin ta ya leqo sai kamshi ke tashi ba qaramin kyau tayi ba...dai dai parking space driver yayi parking.... Alhaji ya fito shida sadiq yaran sadiq sai qamewa suke tare da kwasar gaisuwa wajan Alhaji... Washe da baki suka shigo gidan cikin sallamar su..... Jidda da ke zaune a palour suna wasa da Jamal qanin hannan d'an Bilkisu....da gudu Jidda ta rugu wajan grandpa ta rungume shi ita da jamal daukar su yayi yana cewa.. Ah'ah my little grandchildren kun girma musanman angel.. Angel me daddy ke baki kin qara girma... Dariya tayi ta ce grandpa kullun daddy sai ya bani fresh milk da safe....good girl yanzu kin fara cin abinci kenan ..washe baki tayi...mom ce ke taka downstairs ahankali washe ta baki.. Ahankali alhaji ya daga kai ya hadiya wani muyau yana binta da mayan kallan...ohni salma tsohuwar Zuma tatashi lol.. Katse mai tunani tayi ta hanyar cewa..." Abban sadiq sannu da zuwa... Yauwa ya hanya ..."Alhamdulallah ..."kun zo kun fara cika grandpa da surutu ko ....."washe baki su kayi su duka Anuty bilki ta ce...oya ku wuce kuyi wasa Hanna ce ta zunboro baki... Momi nafa girme su ni ai bana wasa... Toh yayi uwar mata ..."mom ta bushe da dariya tare da jan hannu alhaji suka wuce bedroom

Ita da kanta ta taimaka mai ya cire kayan shi ya shige wanka inda yake ta zuba Mata soyayyya ...after 1hour Alhaji ne ke sa kowa daga stairs shi da mom sanye yake da jalabiya milk ya fito sak bafulatani glass manne a fuskar shi dining area suka wuce lokacin kowa ya halara... Mom ta jaa ma abba kujera ya zauna itama ta zauna... Mom ta fara serving nasu lunch cuscus ne da miyar dankali taji kaji sosai aciki sai lafiyanyan sob'o mai sanyi ta zuba ma abba.."ahankali suke lunch inda sadiq ke feeding Jidda da Jamal....

Bayan sun gama kalaci fatuha ta kwashe kwani kan ta wanke... Ta wuce gidan su fatsima suka wuce rafi... Tafe suke suna tsoka dan har yanzu da suka fara irgandangi ba dai tsokanar su kayi ba .... Fatuha kalli wancan ba dan megari bane da kandala..."Qur'an shine tap aiko ya ja ma kanshi tona asiri taho mu qarasa.... Dan mai garine da kantala suna ta aika masha'a bayan bishiya...ohni asirin ku ya toni bilahilazi kamar a gaban mai gari inji fatuha.....bala cikin Sauri ya Fara maida zariyarar wandan shi yana zare ido kandala ta fara gyara Riga zata dau tulun ......Qur'an ba inda zaku mun Kama kwartaye...hehe ...."keeee!! Ni sa'an kine zanci uban kuma fa yana magana cikin borin kunya...hehe bilahillahi.. Bala ka raina mana wayau mun Kama ku kuna iskanci shine dan baka da kunya zaka zagemu toh Qur'an sai mun tona...dama ranar kandala na dau gyadar ta tamin raini wayau to zan je na fada malam abinda kike in kin fito talla... Kwala ta Fara matsewa tana ba ma fatuha hakuri shima bala haka har ya masu Alqawarin zai basu murtala sannan suka hakura ..suka tafi suna dariya

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*

*👏🏼Godiya ta musanman ga masoya❤ wannan novel din CAPTAIN SADIQ👮🏼‍♂️ Ina jin dadin comment naku💃 Allah bar zuminci*😘

13_14

Innalillahi wa'innailaihi raju'un duk wani mai rai mamaci ne yau dai kausar ta rigamu zuwa gidan gaskiya..inda aka wuce da sadiq emergency dan be san inda kan shi ya ke Ba... dangi sunyi kuka sosai saboda kausar mutuni yar kirki ce

Yau kusan sati daya kenan da rasuwar kausar sadiq na asibiti sosai yake samun kulawa wajan su jawad da majid wanda be ma san suna yi ba... Jawad ne zaune dakin asibiti saman three star yana shan coffee... "Ahankali yake bade sexy eye's ball din shi..." Ahankali yake tuna duk abubuwan da suka faru wani irin kuka ya fashe da shi mai tsuma zuciya yana qoqarin tashi ya cire dirif din da ke makale a hannu shi.. Jawad ne ya taso ya rungume shi alamar lalashi kuka ya qara fashe wa da shi yana fisfis kamar zarare... "Bros I can't live wit out my wife please bros ka barni na bita ya qara fashewa da wani saban kukan...ganin abin nashi kamar ba kai daya ba ya sa jawad yayi ma daya daga cikin yaranshi da ke tsare kofa.. Kiran Dr yakub.. Dr yakub ne ya shigo shi da nurse tana dauke da tray alururi... Dr da jawad da kyar suka samu suka danne sadiq aka mai alura bacci..sai da yayi kusan 30 minutes yana sanbatu sannan bacci ya dauke shi..."Jawad ne ya ce" Dr Ina fatan dai sadiq ba brain nashi bane ya sami problem Ba ya ida zancan yana matsar kwalla.."karka damu kawai mutuwar ta firgi tashi ne amma insha Allah ze sami sauki daya tashi komai zeyi normal Allah bashi lafiya.. Ameen Dr.

2weeks letter

Sosai Jidda ke samun kulawa wajan mom da baba jinmai da mai aikin ta Mary..." sadiq ko duk wata walwala ya daina idan kaga yana smile to Jidda na hannu shi inda ya daura mata san duniyanan wani bangare na zuciyar shi kuwa ji yake Nigeria ma ta isheshi saboda ya rasa abin kaunar sa inda ya yanke shawawar barin kasar be samu wata matsala Ba wajan aikin shi ya dau Hutu sheraka daya...mom ce zaune a palou sadiq na riqe da jidda Wanda bacci ya dauke ta acinyar shi...cikin sanyi murya kamar mai koyan magana da yanzu magana ma wuya take mai yace...mom Ina san nabi jawad londan inzai koma.."toh shikenan son..amma mom Ina San in zan koma na koma da Jidda saboda sai hankali na yafi kwanciya... Mom ce ta daka tsale ta dire tace...bata San zancan ba" ba inda ze je da ita ba yanda ya iya ya hakura wannan kenan

*Cigaban labari*

Ahankali ya dau jidda wanda ke bacci ya kaita bedroom ya kwantar da ita ya shiga wanka.." inda yake jin mutuwar kausar ta dawo mai sabuwa sai da ya zubar da kwalla sosai.... 30 minutes yayi wanka ya fito sanye ya ke da bathrobe.."Ahankali ya kai lips din shi goshin Jidda ya Mata pack.!! "ahankali ta ware manyan eye's ball din ta..."Daddy" oya tashi ayi wanka muje yawo wajan hajiya da Umma.. Baki ta washe.."ok daddy.daukarta yayi ya kaita bathroom ya wanke ta tas inda suna wanka suna wasan ruwa

Yanzu saboda Allah fatuha kin kyauta kenan..ince bana ce ki kyala Rabi'u ba eh.."yo inna ji nayi kwarankwatsi bana iya hakura.. Aikin kyauta tunda kin sa maitafasa tamin tanadi kinji dadi saiki zubar da ruwa a qasa kisha..baki ta turo gaba.. Gaskiya inna baki suna kwarankwatsi baffa yafi sona ta ida zancan tana matsar kwalla.. Fatu kenan kin taba ganin inda uwa ta haifi da tace bata so .. Kawai dai halin kine ban so fatuha ki daina tsokana.. baki ta washe .."yo ahe kina so na kwarankwatsi na daina tsokana amma bilahilazi duk Wanda ya shiga gona ta sai ya ci wuya Qur'an.. Sannan ta zuri takalman tace... Inna na tafi makarantar allo.. Toh Allah ya shirye ki.."ameen inna

Bayan sun fito daga bathroom ya shirya ta cikin gown maron mai d'an siririn hannu sai mai dugwan hannu a ciki ya ygara Mata gashin ta.. Masha Allah sosai Jidda tayi kyau kamar diyar larabawa.. Pack ya Mata a cheek ita ma ta mai..."oy je ki wajan grandma ganin zuwa... OK daddy ta ruga da gudu ta fita ya bita da kallo yana smile...shima shirywa yayi cikin jeans black and red T-shirt mai ratsin black me dugan hannu sannan ya maqala hannu shi agogo black

sannan yasa takalman sa black ba qara min kyau yayi ba abin ka  da farar fata dan hutu sajan nan nashi yayi liflif...ahankali yake sakowa daga downstairs mom a palou zaune Jidda na zuba Mata surutu..cikin natsowa ya gaishe ta ta amsa sannan yaja hannu Jidda suka fita mom ta masu a dawo lafiya

Zauna suke suna karatu fatuha tace... kwarankwatsi na gaji... yo hi haka akeyi ya tasamu gaba Ana abu daya.. Rabu da shi Qur'an nan kadai ya iya a karatun dariya suka kwashe da ita...Ashe Malam dalha ya ji dariyar ya fido so waje yana zare masu idanu... Dan buhun uban ku kun raina muta ne ko yau  zaku ci uban kune... Sai da ya zane masu jikin radau sannan ya kyale sun inda suka rinqa jeramai Allah ya isa

Dai dai parking space yayi parking ya fitu riqe da hannu Jidda part din hajiya suka fara shiga... cikin sallama suka shiga"hajiya da ke zaune saman two star ta washe hakura.."Ah'ah yau kaine a gidan namu amma yau batan kai kayi maigida... Smile yayi ya langwabe kai .. Kai hajiya sokike ki ce bana zuminci ko" sannan ya samu waje ya sauna...  "Dama yi kake ta ida zancan tare da qwalawa Asiya mai aikin ta  ta kawo masu kayan motsa baki.."oh ashe da wannan yan neman ka zo tare da jan Jidda ta  daura a cinya.. Kawo ta nayi ta maki bana.ah tap aiko da  taci na jaki su duka suka kwashe da dariya.. Sun dade sosai suna hira sannan suka wuce  part din umma cikin. "Sallama suka shiga Umma dake kitchen ta leko..ah'ah yau za'ayi ruwa da qanqara.... Jidda ta ruga da gudu ta  rungume umma... Shagwabe fuskayayi  tare da zama.." Umma har da ke cikin masu ce min bana zuminci..  Daga bayan shi ya ji ance.. Toh yin zuminci kakeyi ..juyawa yayi dallama majid harara.. Sanye ya ke da kayan ball green da alama daga ball yake  ..Toh dan Hana ruwa gudu...hehe yana dariya ya hau upstairs...basma ce ta fitu qanwar majid baza ta wuce 15years ba ta gaishe da sadiq ya amsa ta ja hannu Jidda suka je dakin ta...sun dade sosai suna hira da Umman sannan ya biya majid... dakin majid ya shiga ya zauna saman sofa lokacin majid na wanka... Sanye da bathrobe ya fito.. Ashe ka biyo ni harara ya balla mai...ah bani na Kai zoman Ba  rataya aka bani  ka zo sai yi ma mutane borin kunya kake ya ida zancan yana dariyar shaqiyan ci..basu suka bar gidan Umma ba sai isha lokacin rai su Alhaji sun dawo da kauya

Fatuha da fatsima ne bakin rafi suna shan mangwaro..tap bilahillazi mangwaran ga zaqi garai.. sosaima Qur'an inji fatsima..kin San wani Abu na matsu baba jinmai ta zo mu ci dadi nifa tsarabar nake mawa.. ke dai bari fatuha ni wallahi duk cikin tsara wannan bakin abin yafin dad I ta washe baki wato(chocolate) lol

*Fan's kuyi hakuri da wannan page din har na gama typing ya goge sai dai wani na sake*

*Taku har kullu Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*

👮🏼

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

*yabo da jinjina👍🏽 nake wa masoya❤ wannan littafin📖 gaskayi Ina jin dadi yadda kuke comment kan littafin nan💃💃 Allah ya bar soyayya*😘

17_18

After lunch sadiq ya kwashi su jidda da hannan da Jamal zuwa shan ice cream sosai sunje yawo daga nan ya wuce dasu munjibir park..cikin jin dadi suke wasan su duk inda ka kalla a wajan yara ne da manya ke hutawa har ma turawa...resting chair ya samu ya zauna yana Kallan su Jidda yadda suke wasannin su cikin ni shadi... Daga nesa kuwa yan'mata sai yaba kyan shi suke da tsarin shi wasu mamaki su kar dai ace duk yaranan nashi ne iya kar hadu sadiq ya hadu wasu ma sai jan su hannan suke a jiki dan su samu damar yi ma sadiq magana ganin ba wasa a fuskar shi ya suka hakura basu suka bar munjibir park ba sai gab da magrib...

Dai dai parking space yayi parking ya fito riqe da hannu jidda..Jamal kuma na kafadar sa yaran shi yayi ma alamar su kwaso kayan da ke cikin motar su biyo shi da su haka ko akayi suka kwaso kayan ba komai bane sai kayan zaqi kala Kala da teddy da kayan wasa da ya saima su.... Anuty bilki na zaune a parlou saman three star Hannah ta rugo momi...yeee yan'matan Momi sun dawo bata ida rufe bakin ta ba sadiq ya shigo... Ah sister ke kadai ce a parlou Mom fa..."tana part din abba.."ok ina baba jinmai.. Tana kitchen.." ok hannan Kira min rabi'a ta amshi kayanan ta kai maku su dakin angel... "OK uncle rugawa tayi kitchen ta Kira rabi'a.. sanye take da farar riga mai dogwan hannu sai mini skirt da alama wannan kayan unform ne na yan'aiki....

Har qasa ta duqa ta gaishe shi tare da amsar kayan ta wuce da su bedroom din Jidda.."sister ni Zan wuce masallaci may be sanda zan dawo kin tafi...Ai kwana zanyi a gida..waro ido yayi ya ce.. Gidan naki fa ...hehe ka manta me gidan be nan sai gobe zan koma...oh haka har yanzu be dawo ba ..."eh sannan ya sa kai ya fi ce zuwa masallaci

Duk wata gona dake da bishiyar mangwaro sai da suka leqa suka tsunko nunanu daga nan suka biya wajan shafi'u mai rake suka amso bashi acewar duk sanda bala dan mai gari ya basu Murtala zasu miyashi..."Kai wallahi na gaji..."ai sai da nace maki mu zubar da ruwan tulun mu zuba mangwarayan mu cikin tulun in mun koma gida sai muce biyo mu akayi muka fasa dibar ruwan.." kwarankwatsi ke dai fatuha wayau gare ki amma kinsan wani Abu..a'a saikin fada qara muje da ruwan Qur'an saboda mun dade... Haka kuma fa ga wancan Malam dalha din sai sauri ya ke yaje ya Fara zalinci...ke dai bari ta qara gyara tsayuwar tulun ta..kinko iya qarin jiya fatuha..hehe yo tun yaushe na iya shi... Ke nifa Malam dalha ne bemun ba shiyasa bana bashi hada amma Qur'an na iya..."toh bilahillazi yau sai kin bashi saboda yau ban shirya ma bugu ba..

"Ko bishiyar nan da muka hau na maqale duwawuna sai zinga yake.. Fatuha ta kwashe da dariya.. Sai ki je gida kiyi gashi da ruwan dumi.. Inmaki na maitafasa..

Cikin sallama ta shigo gida inna ta amsa.. Inda Sabo ya kamata ta saba da wannan baqin hanlin na fatuha in ta je diban ruwa sai ta shekara bata dawo Ba

Inna Ina abinci na yana madafi kwanan samira ta jawo tuwo ne miya kuka yasha manshanu sai kamshi yake loma daya zuwa biyu fatsima tayi sallama cikin shirin ta na zuwa makarantar allo... Tare suka zauna suka ida cin tuwo zanta dau hijabin ta kenan inna ta leko daga uwar daka...

"Yanzu saboda Allah fatuha sai na ce kiyi wanka zakiyi kome raban ki da wanka tun shekaran jiya wuce kiyi wanka nan ku tai makarantar... Baki ta turo gaba tana dire dire gaskiya inna ki bari sai na dawo nayi... Aifa baki fita sai kinyi wanka..

Da kuka da komai fatuha tayi wanka sannan ta fito suka wuce makaranatar allo

Zaune suke a parlou suna hira cikin ni shadi su Jidda sai wasa suke..

Ku dai baku gajiya da wasa ko inji Anuty bilki... Ince dazu ba manjibir park kuka je da uncle ba duk wasan da kukayi be ishe Ku ba ko..."Oya ku wuce Ku shige bedroom kuyi bacci...su duka suka hada baki.. " sorry Momi tare da lagwabe kai duka parlou aka fashe da dariya...

"Yauwa gobe Ina so ku shirya da wuri inji Alhaji... zamu je family house meeting... "Toh Allah

ya kai mu Alhaji inji mom..sun dade sosai suna hira a parlou sannan kowa ya tafi part nashi.. Inda su Jidda suka maqale ba su kwana ko Ina sai part din sadiq haka ko akayi da yake shi mutun ne mai san yara

Bangaran su alhaji ko sosai suke zuba soyayya tare da gwada wa juna su yadda sukayi kewa...sosai alhaji ke gwada ma Momi salan sa daga nan suka lula duniyar ma aurata

Zaune suke Malam dalha sai amsar hada yake da zabgegiyar bulala shi a hannu burin shi bai wuce ya ga su fatuha sun kasa ba ya wanke su da bulalar... Ke tashi ki bani taki hada cikin tsiwa fatuha ta tashi ta fara karanta wa Masha Allah cikin muryar mai sanyi da dadi ni kaina sai danayi mamaki wai dama fatuha ta iya karatu haka..Malam dalha ko sakin baki yayi har ta gama sannau ya koma ya zauna gwiwa sage...lol

Tsale tsale suke kamar ba dare ba cikin bedroom din sadiq...wasan pillow suke haka shima ya shiga cikin su wasan su ke cikin nishadi haka shima sadiq ya biye masu shima kamar qaramin yaro suna haka har bacci ya kwashe su

Ahankali yasa hannu ya bude wardrobe ya Ciro pic din shi da kausar na maqale a qirjin shi ahankali wasu hawaye mash zafi suka zubo mai yasa bayan hannu shi ya goge...bazai taba mance wannan ranar ba bayan sun gama wasan pillow shi da kausar suka je waje suna wasan ruwa anan su kayi pic din da camera...I miss u my wife.. yana rungume da pic din har bacci ya dauke shi..

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
(We are the best)
19_20

Duk yadda Malam dalha yaso ya daki su fatuha yau dai bai samu hanya ba har aka tashi..

Cikin sallama ta shigo gida... baffa na tsugunne yana shanya zogala... Washe da baki ta gaishe shi.."yar Albarka har kin dawo kenan.."Eh baffa na dawo...Masha Allah ana dai karatu dai ko...."Eh baffa.. Ai haka ake so...qoqarin cire hijabinta take tace... Baffa ina inna..ayo ai yanzu inna ki ta leqa gida su fatsima baki hadu da ita Ba..Eh" bata ida rufe bakin ta ba sai ga inna ta shigo...sun dade suna hira sama sama daga nan Inna ta shige madafi...

Bathrobes ne sanye a jikin su jidda suna ta tsale tsale a cikin dakin sadiq...ahankali shima ya fito daga toilet kamar Wanda ke jin tausayin kasa babu alamar walwala a tatare da shi kasan cewa yau ji yake mutuwar kausar ta dawo mai sabuwa....daddy morning..morning too my little children .. Fridge ya bude ya Ciro fresh milk ya zuba masu a cup's kowa ya sha ...Anuty bilkisu ce ta shigo part din cikin sallamarta ita rabi'a...sadiq na qoqarin ya shirya su Anuty Bilkisu ta shigo..."ah bros yaran nan sun hana ka hutawa ko ....nop ...oya Ku wuce muje baba jinmai na bedroom dina tana jiran ko...ok Momi suka fita a goje ....

Gyaran murya Anuty bilkisu tayi a hankali ta shafa gefen fuskar sadiq wanda ya lula cikin duniyar tunani.... A hankali ya dago sexy eye's ball's din shi ya ja numfashi... Sister tare da daura hannun shi saman nata....baby wai meke damun ka ne um gaba daya ka chanza yau a ganka da walwala gobe a ganka ba walwala.... hawayan da ke maqale a idanun shi yayi qoqarin mai dawa ya qaqaro murmushi Wanda iya karshi lips din shi...."sister ni fa ba abinda ke damu na... "Toh shikenan naji me yasa kake Kora masu kula da jidda why?.. Kafi so ka cigaba da kula da ita da kanka bayan kasan hakan ba zai yuyu ba saboda kana zuwa aiki.... "Ka gani baba jinmai ba yarin ya ba ce bata iya dawainiyar ku kai da Jidda sai dai na mom...um gyaran bedroom naka ka hana kowa yama sai ita me yasa baby ka chanza ta ida magana cikin rawar murya .....langwabe Kai yayi kamar qaramin yaro...sis ni fa ban chanza ba kawai dai yan' aikin ne basu ji sis shiyasa dana aje kudi sai su dauka baba jinmai ce d'ai bata daukar abinda ba'a bata ba....." Toh naji yanzu dai ga rabi'a tana parlou ka zata fara gyara ma daki daga yau kafin baba jinmai ta je kauye ta samoma good girl Wanda batada d'an hali..." B'ata fuska yayi ya ce sis kin..... Shhhh please kayi hakauri for some days baby.... toh sis pack ya mata a hannu ta mashi a goshi

Um kayi sauri ka shirya kasan yau akwai family meeting..I now ganinan fitowa ..OK

Rabi'a na takure saman one star cikin yin uniform din ta na yan aiki Wanda bata tunanin...sadiq ko giya wake yasha be yadda ta mai aiki saboda so biyu yana kamata zata mai sata... Anuty bilki ta qaraso washe da baki tace... Rabi'a daga yau zaki Fara aiki anan part din na wani dan lokaci please ki kula saboda na lura ba San aikin naki ya ke ba...to ta ce tana

maida numfashi tare washe baki toh anuty.....Anuty bilki tasa kai ta fice

Fatuha!!! Fatuha!!..." Na'am inna...." zo nan wayan nan kayan wakika barmawa su raban ki da wanki har kin manta wai yaushe zaki fara tsaf ta ne fatuha eeeeh..."kin fara girma amma kullun rashin jin ki daduwa yake.... Yi maza ki wanke su tas ki shanya.... Kuka tasa har da birgima Qur'an inna ban iya wankin alqawalin Allah... Bakin ta inna ta bige ta ce.. wallahi in bakiyi wankin nan ba baki zuwa gada' tunda baki san kin girma ba kuma indai baba jinmai ta zo kina ji kina gani zan bayar da tsarabar data yi maki... Matse kwalla tayi ta ce.. Toh inna zanyi Qur'an...Ah karma kiyi ai ba dole.. Inna ta fara tatara kayan zata shige da su daki..jiki a sabule fatuha ta amshi kayan ta fara wankin

Tsaye yake gaban dressing mirror yana feshe jikin shi da turaran intense mai sanyayan kamshi sanye yake da t-shirt blue mai dogwan hannu sai jeans dark blue hannu shi maqale da agogo silver na azurfa farin glass din shi yasa ya fito kamar balarabe ba qaramin kyau yayi ba amma fuskar nan daure.... Qwanqwasa kofar dakin shi akayi ya juyo...yes come in rabi'a ce jiki ba kwari kallo daya ya Mata ya watsar cikin kakausar murya ya ce what.. Um kai nake jira ka fita na gyara bedroom din..wani irin kallo ya qara wurga mata ya matso gap da ita... Kinsan Allah Zan fita ne na Dawo wallahi na shigo daki na naga banga tsinke ba..huh you will see...fuuu ya ja ya fita ya barta sai b'ari take

Ahankaliya ya ke saukowa downstairs fuskarnan tamau dinning area ya wuce kowa ya halara za'a fara breakfast gaishe da iyayan nashi yayi tare da yi masu pack a goshi sannan ya samu waje ya zauna

Anuty bilki ce tayi serving din kowa suka fara cin abincin..mom na lura da sadiq dan ba wani cin abincin yake ba ga fuskar shi daure haka shima abban nashi yake lura.. Inda sabo ya kamata su saba da irin wannan halin nashi yau da fara'a gobe babu....a hankali ya ke cin abinci loma uku zuwa hudu ya miqe.. Son" yes mom... Har ka qoshi.. Eh na qoshi.. Amma kasan ba zamu shirya ba ko wannan ai ba abinci ka cin ba... Abba ya amshe zancan da cewa...shiyasa Jidda bata San cin abinci shiya ke koya mata hakan... Shagwabe fuska yayi.. Abba na sha fresh milk a daki da yawa shiya bana jin yunwa..um lalai dama fresh milk abinci ne inji Anuty bilki.. b'ata fuska ya kuma yi to ni Ina sha na ko shi... Langwabe Kai yayi ya ce.. Angel wai daddy ne ya koya maki rashin cin abinci...no daddy Kai da kake jin plate biyu...kowa na dining sai da yayi dariya har sadiq din Wanda tun tashin shi beyi dariya ba..."Ohni Jidda wato kare daddy ki zakiyi ko ..mom ta ida zancan tana lakace Mata hanci...

Ba ita ta gama wakin ba sai yama likis ta wanke su tas suka fita... inna washe da baki ta

ce....ko ke fa diyar baffan ta..turo baki tayi gama tare zubar da ruwan daurayar a maguji... Oh fushi ake dani dan nace ayi tsaf ta sallamar baffa ce ta katse Mata zancan washe da baki ya shigo hade da sallama

Leda dake hannu baffa fatuha ta amsa..ah yar albarka yau wanki akayi kenan... inna ta amshe zancan da cewa kasan ko  faman dana sha da ita sannan tayi wanki...ki ce min dai matsa mata kikayi...ai dama Kai baka ganin laifin ta...."Um fatuha dama Ledanan tsarabar  yallo ce na makin ..washe hakura tayi tace.. Toh baffa na gode.. Yauwa yar albarka ..inna ta shige qurya ta kwasu ma baffa abincin shi

Cikin jin dadi ta gama wanke yallon da zubo masu inna na su sannan ta dau nata dana fatsima ta fice

After sun gama breakfast kaitsaye family house suka wuce

karku so kuga soyayya dangi ba tsangwama ba tsana sai tsantsan soyayya wanda uwar mazajan su ke gwada masu ba tare data banbanta wani ba

Wani kata farin parlou ne Wanda ya amsa suna shi yasha red carpet mai laushi sai manyan kujeru red n black sosai tsarin parlou ya hadu..Alhaji kabiru ne ya Fara magana cikin muryar shi ta manya da  natsuwa yana fadin irin kadarurin da suka samu a kasuwan cin su inda baban nasu ya yanke hukunci za'a raba kudin kashi  biyar..kashi 5 nasu kashi  biyar na taimakwan Alumma ... Kashi 2 za'a kai gidan marayu kashi 1 asibiti kashi 2 taimaka  mamara karfi sosai sunji dadin yadda baban nasu ya tsara abin bayan sun gama tattaunawa akayi addu'a aka tashi kowa ya koma harkar gaban shi

Big man wai lafiya yau sai wani cin magani kake inji majid ya ce..."Alalai ma to wazan ci ma magani kai wallahi ka bani sai shege surutu ya ida zancan ya furzar da iskar bakin shi... Naje nayi surutun in fitsari arhane wani yayi mu gani wani saboda tsabar rashin yin magana shi bakin shi wari ya ke ya ida magana yana  dariya ..."oh dani kake ko da gudu majid ya  ruga part din ammi sadiq ya bishi...ammi da ke hira da surukanta...
majid ya zo ya  boye bayan ta...." Lafiya kai kuma wallahi hajiya ... bai ida zancan ba sadiq ya shigo fuska daure.. Ayo ai sai ka ce min wannan me bakin ran ka tsokano kowa na dakin sai da ya murmusa ... langwabe Kai yayi ya ce..ammi yanzu nine mai bakin rai kin san me yamin kuwa....Alhaji yace" rabu da su aikai d'a wuri nane kaji... Majid ko gwalo ya mai be San ammi ta ganshi  ba..to ja'iri Ashe Kai ke Jan shi tashi ka ban guri dariya kowa na parlou yayi... Sosai jin

dadi suke family inda suke hira cikin ni shadi

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN  SADIQ*
👮🏽‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Éditing Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

*this page is for you my fan's*

23_24

Tashi tayi daga jikin inna tana zunburo baki gaba,  Inna tace "Yar nema ba'a isa ayi maki magana bane ko me?" Haba ladingo  wai me yasa kike so ki rinka takura wa yarin yannan ne? Baba jinmai ce tasa baki tace, "Ah kuyi hakuri dai. Indai jiki nane ai ta sauka ko? Inna ta murmusa batace komai ba.

Duk wata tsaraba data kawo haka ta bajewa fatuha kayan zaqi  fatuha ko baki har kunne dan dadi saboda har da bakar alawa, wato (chocolate) haka shima dan uwan nata da matar sa ta basu nasu tsarabar sosai sunji dadi musanman ladingo wanda take ganin baba jinmai ta dauke ta tamkar ciki daya suka fito, so da yawa tana fifitata kan jauro din ma saboda karamci irin na baba jinmai da sani darajar Dan adam, sosai suka ji dadin wannan tsarabar.

A guge fatuha ta qaraso gidan su fatsima kawo mata nata tsarabar saboda dama ta mata alqawari duk sanda baba jinmai ta zo, to zata kawo mata bakar alawa"(chocolate) .

Washe da baki ta qarasa..tace  "Fatsima! Fatsima!ohni fatuha lafiya nagan ki haka? ko yauma tsokana kukayi inji gwagon fatsima" washe baki tayi ta ce "Wallahi gwogo baba jinmai ce ta zo yau shine na kawo wa fatsima tsarabar ta."Ayya ki ce min mutan birni sun zo, Aiko fatsima na kewaye ki jira ta tafito, bata ida rufe bakin ta ba fatsima ta fito washe da baki." Tace "Fatuha, na'am tare da qarasawa wajan ta" ke baba jinmai fa ta zo Qur'an... Dan girman Allah? washe

baki ta kuma yi ta ce ."Tayi tsarabar baka alawa " Eh Qur'an gama taki nan na kawo maki, Ah kai amma naji dadi ,haka suka shige akurkin dakin fatsima suna ta hira tare da sharan ce muta ne' inna da ke tsakar gida sai cewa ta ke Allah ya shirye su...

A gajiye ya dawo gida briefcase din shi da ke hannu yaran shi *ola* ya amsa" cikin sallama ya shigo falon, Mom ne zaune a parlou tana kallo angel na kusa da ita tana bacci, A hankali ya qaraso yayi hug din mom ta baya... Yace "Wash mom am tied." Juyowa tayi suna facing din juna Ta Amsa mai da cewa "Sorry son ka je part dinka kayi taking shower lunch inka na jiran ka.." Ok, face din Jidda ya dan shafa.. sannan ya haura upstairs..

Yana shiga part na shi bathroom ya wuce yayi wanka ya fitu sanye da bedrobe White.. Ahankali ya nufi dress mirror ya fara shafa lotion mai kamshi yabi ko ina na jikin shi da shi,kai tsaye Wardrobe dinshi ya nufa ya curo three quarte black sai armless t-shirt ya sa , ba qaramin kyau yayi ba masha Allah.

Cikin na tsuwa ya ke sakowa daga downstairs ya qaraso parlour inda ya bar mom har yanzu nan take... Dining area ya nufa, ya ja kujera ya zauna rabi'a na gefe ahankali ta fara saving na shi Tuwan shinkafa miyar agushi wanda taji kaji da yan ciki kamshi sai tayi yake ,Sai data gama serving nashi sannan ta mike, harara ya dala mata dan shi kwata kwata yan' aikin kona mai rai suke musanman yan'mata wanda ba abinda suka sa gaba sai halin bera, wani wawan tsoki ya kuma ja wanda yasa rabi'a kyarma, dagowa yayi da sexy eye's ball's din shi yace... "Keeee!Tunda kin gama zubamin abincin ai sai ki tafi ko? ko sai kin gama qaremin kallo eeeeeeeye."

Mom dake parlour sai data ji tsawar da Sadiq ya daka ma rabi'a juyowa tayi ta ce..."Why son! Wai me yasa kai kullun sai an jika da masu aiki ne baby? gashi nan yanzu garin fadan ka ka tada angel daga bacci...." Bata fuska yayi kamar qaramin yaro ya ce..."Mom ni wallahi bana san yan'aikin nan wallahi yawancin su duk barayi ne mom ya ida zancan yana tsame hannu shi daga cikin plate din abinci...." Tare da dalla wa rabi'a harara ai saiki zo ki kwashe ragowar abinci ki cinye Maya mutunci kawai ya qara jan tsoki mtssss ya dawo parlour ya zauna tare da daura Jidda a cinyar shi..." Dadday please muje shan ice cream.."Ok angel bari na dako car key sai mu fita" aje Jidda yayi saman three star sannan ya haura sama....

Sai da suka kusan cinye rabi alawar sannan suka saurara mata sai dai muce Allah ya tsare kar ayi zawo.

Sai yama likis fatuha ta waiwayi gida shima din dan zata canza kaya dan ta je gada.... Washe da baki fatuha ta qaraso gida..Inna da baba jinmai sai labari suke saman tabarma ta zo ta wuce su...baba jinmai washe da baki tace... "Fatuha yan'mata" murmushi tayi tare da shigewa uwar daka...baba jinmai ce ta qare mata kallo tsab tace "Masha Allah fatuha kyakyawa sai dai rashin jita baya bari a gani" tana da dan tsohu dai dai gwargwado ita ba gajera ba kuma baza'a kirata doguwa ba, tana da karan hanci kamar biro, bakin ta dan qararami ne pink...ba laifi tana da hips saidai yanzu ne ta Fara kirgan dangi , wannan kenan...baba jinmai ce ta numfasa tace..."Ni ko ladingo ina so inzan koma zan tafi da fatuha" dama hajiya tace na nema mata wanda zata dinga taimakama yar jikarta saboda yarin ya ce shine da na yanke shawara in jauro ya dawo daga gona sai mu tattauna kan zancan..Tap baba jinmai bana jin malam zai yadda da batun ki, saboda baya bari taje ko ina iyakar ta cikin kauyan nan, baba jinmai da malam zai yadda da haka nima da zan so hakan, ko dan fatuha ta gyaru tunda nasan birni da kauye ba daya bane dole inta je can ta natsu... Nisawa baba jinmai tayi ta ce..." Bari jauran ya dawo ni na mai magana...toh Allah yasa ya amince..

Fatuha ce ta fito washe da baki daga uwar daka, tasha jan baki a dole yau itama gada zata..tace "Inna nayi kyau ?"murmushi inna tayi ita da baba jinmai suka hada baki suka ce..." Kinyi kyau fatuha..." Qara washe baki tayi sannan ta sa kai ta fice...

Riqe da car key ya dawo men parlour tare da daukar Jidda..yace "Mom zamu fita shan ice cream may be mu biya gidan Anuty bilkisu.... OK a dawo lafiya angel amin tsaraba fa.toh grandma Sannan suka fita.

Ko da suka fi anwanke mai motar shi CRB black.... Kaitsaye wanja motar suka wuce... *ola* ya bude mashi murfin motar dana Jidda tare dayi ma Jidda wasa...sannan suka sa kai suka fita, Sosai yayi yawo da Jidda... Daga nan suka wuce gidan Anuty bilki...

Cikin jin dadi ta tarbe su inda ta cika Sadiq da kayan fruit Jidda ko sai wasan su suke ita da jamal.. washe da baki Anuty bilki tace..."Ohni baby yanzu an fara zuminci tana fadin hakan ne cikin zollaya..."harara ya wurga mata....oh you mean da bana zuminci ko tunda haka kika ce bari na tashi na tafi....,hararar wasa ita ma ta mai' tap naga yadda zaka fita daga gidan kuwa...hira suka sha sosai daga nan suka wuce family house.

Part din ammi ya fara zuwa tana zaune saman one star tana kallan film din India wanda ko za'a kashe ta bata san me suke cewa Ba, washe da baki ta juyo tace "Ah'ah yau mai gidana da kanshi? ya fatima ita da Ibrahim din?" "lafiya lau ya ce tare da zama..." Ka ce min da sarkin surutu ka zomin yanzu ta fara min wannan yaran na yahudawa. Murmushi Sadiq yayi yace."Kisha kurimin ki ammi ai koya maki take..." Ah ni ina zan iya wannan gwalangwatsin

wannan sai Ku, Asiya ta kwallawa kira, cikin sauri ta qaraso  tare da gaishe da sadiq... Ciki ciki ya amsa kamar me koyan magana... Yauwa yan'nan kawo wa mai gida fura dana dama dazu tana cikin fridge  , toh ammi ta mike ta wuce kicin.

Haka akayi ta kawo mai fura ya sha sosai, Saboda shi Sadiq mutun ne mai san fura sai da ya sha ya koshi sannan suka wuce part din Umma,

Suna shiga part din da basma suka ci karo, sanye take da riga da wando riga mai dan gajeran hannu pink mai manya flowers tayi kyau sosai duk da yarin yace,hakan yasa sheep din ta fitowa.... Kallo daya Sadiq ya mata ya watsar Gaishe shi tayi tare da jan hannun Jidda tana mata wasa,tace "Basma ina umma?Umma na bedroom OK kira min ita, Sannan ya samu  guri ya zauna.

Umma washe da baki ta fito sun dade suna hira,Inda tasa talatu ta cika mai tray da kayan motsa baki ,suna cikin hira majid ya dawo suka dasa sabuwar hira.

Sosai suke jin dadi gadar inda yau sai da su fatuha suka taka, duk da ba wani abu suka iya ba..." Sosai sun burge mutane ita da fatsima saboda cikin tsari suke rawar su kamar manyan yan'mata.....

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Blood sister deeja*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

*👏🏼Godiya da jinjina👍🏼 gare ku masoya na ❤ Ina matuqar jin dadi yadda kuke bani

qwaringwiwa wajan suburbudu maku wannan novel din*💃💃

*This page is for u amal*   21_22

Basu suka dawo daga family house ba sai 9:00pm Anuty bilki ta wuce gidan ta

A gajiye likis ya dawo direct toilet ya shiga yayi wanka yana fitowa ya dau jidda ya mata wanka sai rigima take mai ....sai daya gama shirya ta tsaf ya samata night dress pink wando da riga ya raba mata gashin ta gida biyu sannan ya kwatar da ita... Oya yanzu ayi bacci.... Bana jin bacci daddy please ka bani story... Ok angel bari daddy ya shirya... Toh daddy am waiting... Sai daya shirya sannan ya qarewa dakin kallo ba laifi ta gyara dakin amma dai shi gyaran bai mai ba..... riqe da story book din jidda ya dawo saman bed lokacin har tayi bacci smile yayi tare da yi mata pack ya janyo laptop din shi ya cigaba da aiki bashi ya gama aikin ba sai 12:00 sannan ya kwata tare da janyo Jidda kamar za'a kwace mai ita

Sosai suke kallan gad'a washe da baki kasan cewar yau suka fara zuwa...tap Alqawalin Allah kallo na wuce mu... "Sosai ma inji fatsima...ke ni daga yau ban qara fashi wallahi kullun sai na zo...nima haka Qur'an haka suka sha kallan gada daga nan kuma suka fara  tsokana dan wannan ya zamar masu jiki sannan suka dawo gida

Tunda safe ya tashi kasan cewar yau Monday cikin shirin shi na uniform ya ke shiryawa ba qaramin kyau yayi ba gafen da Jidda ke kwance ya kalla da alama baccin ya Mata dadi so be so ya tashe ta shiyasa beyi Mata wanka ba briefcase nashi ya dauka tare da yi Mata pack ya fitu...a parlou shi ya ci Karo da rabi'a na shara.. kallan tsana ya bita da shi har yayi gaba ya dawo... Keeee!!!cikin tsoro ta dago qara murtike fuska yayi yace... Angel na bedroom tana bacci so kibi hankali karki tashe ta kuma in tatashi ki Mata wanka kina jina..Eh" ya watsa mata harara ya ce saura na dawo naga kin min sata ya ja tsoki ya fice...

A men parlou ya ga mom zaune tana karanta azkar.. Har qasa ya gaishe ta tare da yimata pack...baby" na'am ....Jidda fa ...mom Jidda na bacci.. Ok.. So nake ma na samama Jidda school da malamin islamiyya ya rinqa Mata a gida... Ai hakan na da kyau kamar kasan magana dana ke San yimaka kenan ka rigani..smile yayi tare da wucewa dining area a tsaitsaye yayi break din ya fita ...

Tana tashi tayi wanke wanke sannan ta share gidan su qwal ba laifi yanzu fatuha anfara yin aiki shima din sai tasa kanta inna ta fito washe da baki...Ah'ah fatuha an Fara zama yan'mata....rufe fuskarta tayi ala dole kunyar inna take ji .....ohni fatuha kunya na ake ji to madalla Allah ya

shirye ki.. Ameen inna tare suka shiga madafi yau dai ba laifi fatuha tayi aiki sosai dan yau ko damar zuwa gantali bata samu Ba

Baba jinmai ce cikin daki sai harhada kayan ta take cikin ganamasgo washe da baki...mom ce ta leko dakin..Ah baba sai sauri kike ki tafi.. Washe baki tayi tace.. wallahi na matsu na ganni a wudil dinan na dade banga dan uwana jauro ba..."gaskiya ko" Yauwa maganar samomin yar aiki fa dan Allah baba jinmai ki samomin natsatsa Wanda zata iya aikin nan kisan halin baby da shegiyar tsurfa... Insha Allah Zan duba maki.. Sannan mom ta ciro maqudan kudi tabawa baba jinmai tayi tsaraba tare da hadata da driver ya kaita tasha murna wajan baba jinmai ba'a magana

Ana kaita ko tasha ta samu motar zuwa wudil dama mutun daya ake jira tana shiga mota tatashi

Baffa ne tsaye bakin uwar daka..ladingo ni zan wuce yau da wuri Zan dawo karki aiko min da abinci...toh malam ..fatuha da ke zaune bisa tabarma tace...baffa zanbi ka....kinga zafi ake ga rana idan mu kaje tare wuya zaki sha fatuha.....baki ta turo gaba ta fara matsar kwalla...toh shikenan dako hijabin ki muje washe baki tayi tare da shigewa akurkin dakin ta ta dauko hijabinta suka fita

Misalin karfe 2:00pm motar su baba jinmai ta tsaya a tasha wani irin dadi ne ya lulube ta yau ta zo mahaifarta zata ga dan uwanta da iyalan shi mashin tatare kasan cewa mota bata shiga cikin garin sai dai mashin ko amalanke

Direct gidan baffa aka sauke ta tare da biyan maimashin sannan ta sauke yan kayan ta da tsaraba washe da baki ta shiga gidan tare da sallama inna dake qoqarin fitowa daga madafi chak ta tsaya...saboda tsabar murya ta rasa Ina zata tsoma kanta..Ah'ah mutan birni sannu da zuwa tare da shifida mata tabarma da debo Mata ruwa a kwano na randa mai sanyi.....ah ladingo sai hidama kike kya bari mu gaisako... Washe baki tayi ace mutun ya sha tafiya ruwan sha ya gagare" toh ya hanya.... Hanya lafiya lau" ina fatuha yan'mata nasan yanzu dai samari sun fara yi mata layi Masha Allah indai kyau ne fatuha akwai shi..."Hmm inna ce ta marairaice tace..sun fita da Malam zuwa gona maganar samari kuwa fatuha babu su" fatuhar da bata ganin kowa da gashi a kauyan nan wani uba ne zai yadda dan shi ya auri fatuha bayan ta masu rashin kunya

baffa ko koda nayi Mata magana zai fara sababi.....alalai jauro haka ya bar fatuha ta zama abinda ta zama ohni jinmai!!! bari shi jauran ya dawo ya same ni... Haka inna ta rinqa lalaba ta dan bata so tayi ma baffa magana saboda kan fatuha be jin kunyar maida magana haka baba

jinmai ta gama kunfan baki

Jidda koda tatashi bata ga daddy din ta ba..da kyar ta yadda rabi'a ta Mata wanka shima sai da mom tasa baki Ana gama Mata wanka ta sauko downstair wajan mom...grandma Ina baba jinmai yau bata min wanka ba ita da dad ta Ina zancan tana matsar kwalla...sorry angel tare da goge Mata kwalla sannan ta jata jikin ta..baba jinmai ta je kauye lokacin da zata tafi kina bacci shiyasa angel... Grandma shi kuma daddy fa ya tafi ya bar little princess din shi at home...sorry angel ai zai dawo kin ji....um grandma please call him... Ok angel amma sai kinyi breakfast sannan... ok " oya muje nayi feeding naki

Alhaji ne yayi gyaran murya ya ce..um kina shan fama babanta  ya maki rigima ita ma ta maki...murmushi tayi tare da shafa sumar Jidda Wanda tasha gyara.... a hanakali tayi feeding Jidda sai da suka gama tsaf sannan shima Alhaji ya wuce office

After sun gama cin abincin mom ta Kira sadiq...yana zaune saman kujerar shi ta  office idanun shi a lumshe kamar meyin bacci wayar shi ta fara ruri a hankali ya bude  sexy eye's ball din shi ya sauke su kan screem din wayar....sweet mom ne rubuce hannu ya Kai ya dauka ....

daga dayan bangaran ...hello baby ya kake ya aiki ...lafiya lau mom.... Dama wannan ja'ira ce ta matsamin ka tafi aiki baka tashe ta ba sai rigima take...murmushi yayi daga bangaran shi hakan sai ya qara fituwa da zala kyan shi numfasawa yayi yace mom bata wayar...ok ...Jidda dake zaune saman cinyar mom ta washe baki tare da amsar wayar...daddy.. yes angel bata fuska tayi kamar yana ganin ta"tace shine daddy ka tafi work baka tada little princess din kaba..."sorry angel lokacin kina bacci bana so na tada little princess na bacci that is why my angel ...ok daddy inka dawo zamuyi wasa ko...yes mana ...washe hakura tayi....sannan ta ce um daddy ta qara bata fuska daddy baba jinmai tatafi kauye ban dani bayan tamin promise tare zamu...sorry angel next time tare zamu kinji...."Yeeee love u dady..."Love  u more angel bye sannan ya katse wayar tare da binta da kallo.

Yanzu tunda kinyi wayar da daddy naki sai ki huce ko dariya tayi ta cigaba da zuba ma mom surutu

Aiki baffa yake sosai fatuha na gefe tana taya shi tare da bashi labari in ta fadin abin dariya ya dara haka har suka gama

Cikin sallama suka shigo inna na zaune saman kujerar tayani gulma tana dama hura saboda baba jinmai nasan hura musanman damun inna..washe da baki suka qaraso fatuha ko jikin baba jinmai ta fada tana Mata oyoyo..Ah'Ah wanake gani kamar mutanan birni sannu da zuwa sannan baffa ya samu guri ya zauna ...inna ce tace...ohni fatuha yaushe zaki girma kin fada mata jiki salan ki karya ta baki ta turo gaba Kai inna har wani nauyi ke gareni tare da matse yar kwalla ..baba jinmai ko dariya abin ya ba

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★ we are the best★

https://mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum,-RHFWF-173984973194167/?refid=52&ref=opera_speed_dial&_tn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook. com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.com

25_26

Basu suka dawo gida ba sai bayan isha lokacin har jidda tayi bacci, dauke yake da ita har suka qaraso parlour, lokacin rabi'a tana qoqari fitowa daga kitchen' wani irin kallo ya wurga mata Jiki

ba qwari ta gaishe shi har tayi gaba yace" Keeee!!" Tsayawa tayi cikin tsoro da fargaba , Harara ya qara wurga mata cikin ktsawa yace mata "Sai ki zo ki amshe ta ko?" Jiki a sabule ta amshi jidda ,Kiyi mata wanka sannan ki Samata night dress ki kawo min ita daki na dan ban yadda ta rinqa kwana da ke ba ki koya mata halin bera tsaki yaja Mtsss, sannan ya wuce part din Abba.

Abba ne zaune saman two star fuskar shi manne da glass, sanye yake da fara jalabiya blue remote ne a hannu yana kallan news, Mom na gefen sa tana yanka fruit.

Cikin sallama ya shigo tare da gaishe da abba, Cikin fara'a Abba ya amsa yace "Ah har kun dawo daga zuminci?" Eh abba, to masha Allah ina jidda ? jidda tayi bacci, OK" sun dade suna hira sama sama daga nan Sadiq ya wuce part nashi ,ko da ya shiga dakinshi ya iske ankwantar da jidda shima bathroom ya shiga ya watsa ruwa ya fito sai da ya gama shirin shi na bacci sannan ya hada coffee yana sha yana dana laptop din shi ,ya dade a haka sannan ya ture laptop din tare da janyo jidda jikin shi bacci ya dauke shi.

Bayan an gama gada kowace ta wuce gidan su, Cikin sallama fatuha ta shigo gida lokaci baffa ya dawo gida yana zaune bisa tabarma inna na kusa da shi baba jinmai na gefe su, gefan baba jinmai ta je ta dauna washe da baki itama baba jinmai murmusawa tayi sun danyi hira sama sama da fatuha daga nan bacci ya sureta.

Baba jinmai ce tayi gyaran murya tace "Dama jauro ina so muyi wata magana da kai."inna da ke kusa da baffa tayi qoqari tashi baba jinmai tace "Kema zauna"haka ko akayi inna ta samu guri ta zauna.

Dama so nake nama magana kan fatuha ina so in zan koma birni sai mu koma tare, Zaro ido baffa yayi waje yana kallan yar uwar tashi à zuciyarsa yace "Anya ko baba jinmai tasan me take fada kuwa?"qara murmusawa tayi ta ce jauro ina fatan ba za ka watsamin qasa ido ba a ganina fatuha nima diya tace jauro, Baffa tsale yayi ya dare ya ce be san zancan ba babu inda fatuha zata tanan kauyen nan tare da shi baze lamunci hakan ba, baba jinmai ce ta fara matsr kwalla tana cewa "Ba komai jauro dan ka ga Allah be bani haihuwa ba shine zaka wulaqanta ni kan diyar ka, jauro da Allah ya bani haihuwa da yau ba zanji zafin abinda kayi min ba, tana maganar tana ta kuka inna sai lalashin take, Ganin kukan da take yasa jikin baffa yayi sanyi dan shi a ganin babu abinda baba jinmai zata nema a rayuwar shi ya hana ta.

Bayan da ya iya haka ya hakura ya amince tatafi da fatuha, aiko washe da baki tamai godiya tare da yimai alqawarin zata riqe amanar fatuha sosai daga nan kowa ya wuce dakin shin.

Ko da ya tashi ya gama shirin shi ciki uniform masha Allah yayi kyau sosai,  Ze dau briefcase din shi shikenan jidda ta tashi washe da baki tace "Daddy morning" morning too angel , hum yau ma daddy guduwa zakayi ka bar little princess din ka a gida? langwabe kai yayi ya ce "Sorry angel daddy work ze je kinji kuma yara basa zuwa kema very soon zaki fara zuwa school ai kinaso ko angel" washe baki tayi tace "Yes daddy zan fara zuwa school kamar yadda su yaya hannan ke zuwa da Anuty basma ko?" Eh mana angel' tsale tayi ta kai mai hug thanks my daddy ,smile yayi tare da yimata pack please angel ki tsaya rabi'a ta maki wanka kin ji? naji grandma na cewa kullun se kin rigima, Bata fuska tayi tace
"Daddy..." shhhh tare da yi mata pack à kumatu ya fice.

A dining area ya hadu da abba shima yana breakfast, mom na gefen shi ahankali ya qarasa yayi masu pack sannan ya samu waje ya zauna ya fara breakfast lafiyayan chips ne da plantain and egg sai tea mai kauri Wanda ya sha ovaltine, cikin natsuwa suka gama break din su abba da Sadiq tare suka fito inda yaran Sadiq ke ta kwasar gaisuwa wajan abba   tare da qamema Sadiq din cikin natsuwa moto cinsu suka fita daga harabar gidan.

Ko da fatuha ta tashi wanke wanke tayi, sannan ta dau tulun ta gidan su fatsima ta biya tare suka fito suna tafe suna hirar su, kandala suka hango dauke da tray gyadar ta qarasowa su kayi wajan ta, Kallan su take jiki ba kwari  Harara suka wurga mata taré da cewa "Bamu gyada ta murtala jikinta baqwari ta fara zuba masu gyadar tasan ko zata mutu baza su bata kudin gyadar ba, kuma ta matsa masu  su tona mata asiri " sai da ta gama zuba masu sannan fatuha ta amsa tace  "Cikin Murtala da dan mai gari ya mana alqawari ne muka amshi gyadar, Sannan kice mai ko ya bamu murtalar mu ko kuma murtala ta rinqa haihuwa sannan suka wuce suka barta tsaye tana matsar kwalla.

Suna isa rafi suka aje tulu na su gefen rafi suka wuce gonar mai gari suka fara tsinkar mangwaro da gwaba sai da suka diba san ransu sannan suka zo zasu fita mai gadi ya kama su, kai kai uban wa ya baku ikwan shigowa gonar mai gari? har ku tsinke  mai mangwaro, Fatuha ce ta turo baki gaba tace bala ne ya bani izinin shigowa ,shegiya mai kama da mayu, shi bala din sa'an kine inama kika san bala din?harara fatsima ta wurga mai in baka yadda ba sai ka kai mu wajan shi ka ji da kunnan ka ta ida zancan tana gyara Daurin zaninta.

Aiko haka akayi mai gadi jan su fatuha yayi har gaban bala, sai yan' harare harare suke su daya ,kaisu yayi suma bala ba yani sai ya ce shi ya ce su dinba dan yasan in bai ce ba tuna mai asari zasuyi, sannan yasa mai gadi ya sake su wani irin dadi suka ji suna ta shewa suka isa rafi suka debo ruwa.

Bai zame ko ina ba sai *Yandutse college* dan samoma jidda admission be sha wani wahalla ba ya samama ta inda duk angama abinda za'ayi, ranar Monday sai ta fara zuwa school sannan ya wuce office, a cewar shi inya dawo gida da yama zai samamata malamin adini.

Kwanci tashi asarar mai rai yau sati baba jinmai daya a wudil inda take ta hada kayanta dana fatuha, Fatuha sai kuka take har da  majina dan ita a ganin baba jinmai bata mata adalci ba ita tace mata tana san birni da zata kwashe ta su tafi toh Wallahi sai nayi rashin mutunci idan munje   sunje  kenan, baba jinmai ce ta juyo haba fatuha sai ka ce za'a cinye ki sai kuka kike haba fatuha kinsan muna tare kuma zan kula da ke kamar yadda inna zata kula da ke, fatuha dan Allah kiyi shuru kinji, Inna da ke gefe duk da tana jin wani irin amma tasan baba jinmai ba zata tayi abinda zai cutar da fatuha ba amma ko yaya tana jin zafin rabuwa da fatuha saboda fatuha yarinya ce mai shiga rai, a hankali inna ke lalashi fatuha har tayi shuru haka shima baffa da ke gefe haka baba jinmai ta gama hada kayan fatuha cikin yar leda gari yayi zafi ta miqa mata ta rungume.

Baffa kuma yaje taro masu mashin,  Sallama fatsima tayi ta shigo falon kallo daya zaka mata kasan itama ta ci kuka har ta gaji, wani saban kuka suka dasa ita da fatsima da kyar aka lalashe su sannan baffa ya shigo ya sheda masu gamai mashi din.

Suna kallan su har suka bile baffa ya goge yar kwallar shi dan shi ka dai yasan yadda yake ji, suna isa tasha suka samu motar Kano basu wani dade ba motar ta tashi.

Idanuwan shi lumshe kamar wanda ke bacci,  zaune yake saman resting chair yayi crossing leg's nashi Taba shin da akayi ne ya sasa ware sexy eye's ball's din shi ba kowa bane sai majid murmushi yayi yace "Yaushe ka zo ban sani ba?" yanzu na shigo mom ta ce min kana nan sannan ya zauna daya daga cikin chairs din ,OK ya aiki?  Alhamdulliha soma nake na dawo nan da aiki, kai Allah ya taimake ka har yau basu ma transfer din ba? Aiko dai ai bana fatan hakan wallahi murmushi sukayi su duka suka cigaba da magana à matsayin su na abokai kuma yan'uwa.

*Tah ku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*

*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com
*Facebook*:www.Facebook. com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.com

https://mobile.facebook.com/Real-Hausa-Fulani-Writers-forum-RHFWF-173984973194167/?refid=52&ref=opera_speed_dial&__tn__=H-R
27_28

Misalin karfe 5:00pm motar su fatuha ta tsaya a tasha lokacin har bacci ya dauke ta tana kafadar baba jinmai rungume da jakarta gari yayi zafi.ahankali baba jinmai ta shiga tashin ta.. Aiko nan tatashi tanayin wani wiqi wiqi da ido da qarewa tashar kallo. mutanene birjik..haka suka zuro kafafun suka fito daga motar. Baba jinmai ce ta zaro wayar ta cikin zani. y'ar baby nokia ce. bugu daya biyu' mom ta dauka. washe da baki baba jinmai da cewa.. "hajiya gani na iso ina tasha...daga bangaran mom murmushi tayi ta ce.. "masha Allah yanzu zan aiko driver ya dauke ko'... "Toh hajiya. Sannan ta katse wayar tana Murmushi ta kalli fatuha.. Yanzu za'a zo daukar mu kin ji yan'nan. kada kai fatuha tayi dan ita a wannan lokacin haushin kowa take ji ...

Ba'a fi 30 minutes ba driver ya qaraso tare da kwashi kayan su ya zuba cikin mota inda yayi yayi da fatuha ta bashi Jakarta ta qi ba yanda ya iya haka ko suka tafi

Kai tsaye sultan road suka wuce nan fa fatuha ta fara zare ido tana qarewa unguwar kallo kamar wanda ta zo aljana haka take gani... Washe baki tayi ta juyo tace... "Baba jinmai dama ashe aljanna kike zuwa... Baba jinmai dariya tayi ita da driven tace.. "aa fatuha nan ba aljanna bane birni kenan... "kai amma kwarankwatsi kinyi da kika zo dani dafa tare da fatsima kikaso zuwa ko... "ke da kikaita kuka baki san zuwa' "Qur'an yanzu ina san birnin.. 😃 ta'ida zancan lokacin yayi dai dai da isowarsu katafarin gate din gidan Alhaji Ibrahim. Zanso kuga yanda fatuha ke zarar ido 😂

Dai dai parking space su kayi parking baba jinmai ta kwaso masu kayan su fatuha dai na maqale da ledar ta, ta gari yayi zafi

Katafaran parlourn gidan suka shiga. Qauyanci wajan fatuha ba'a magana dan ko zama taqiyi saboda tayals sai da baba jinmai tayi da gaske sannan ta zauna saman carpet tana ta zara ido

Mom ce ke saukowa daga upstairs cikin murmushi tace... "ah sannu da zuwa baba jinmai tare da qarasowa parlour da zama saman two star tana facing din su baba jinmai d'in, "ya hanya. Tace da ita tana murmushi.
Alhamdulillah, baba jimmai tace.. "oh tare da yarinyar kuka zo kenan gaskiya naji dadi.
"fatuha dake rabe jikin baba jinmai ta gaida mom cikin girmamawa " baba jinmai ce ta washe baki tace... "Ai diyar qanina ce jauro,
"a'a ki ce min yar tashi ta yi girman haka ' "aiko dai hajiya.. Sunyi hira sama sama inda fatuha ke rabe jikin baba jinmai tana qarewa gidan kallo tare da santinsa

Lafiyayan abinci mom ta basu shinkafa da miyar kaji wadda taji kosulo.. kauyanci ko wajan fatuha ba'a cewa komai saboda bata tab'a cin irin abinci ba dan haka ta saki tinbi ta ci har da side kwano da qari... Baba jinmai dadi taji dan taga fatuha ta saki jikinta

Bayan sun gama cin abinci mom ta kai fatuha dakin jidda ta gwada mata toilet da duk yadda zatayi anfani da komai na toilet din tare da Ciro mata uniform din yan'aiki farar Riga da skirt dai dai gwiwa
ba laifi fatuha duk abinda mom ta gwada mata haka tayi..
wanka sosai tayi da dirje jikinta tare da wanke kanta da shafo .masha Allah gashin fatuha har gadan baya sai dai rashin kulla da shine yasa duk ya cure gu daya amma hakan bazai hanaka ganin kyan gashin ba. daure da towel ta fito.. Mom na zaune saman sofa tana jiran fitowar ta. Koda ta d'ago kanta mom d'in. tayaba kyau irin na fatuha. Hakan yasata yin murmushi..
ita ko saitahau sunne kai.
"Ah har kin fito..
D'aga mata kai tayi alamar Eh , uniform din mom ta dauka ta bata' ga wannan kayan kullun su zaki rinqa sawa akwai su da yawa cikin wardrobe ranar Friday ne kadai zaki sa kayan gida suma akwai su cikin wardrobe. na ki kuma anfidda su waje sannan in kayan sunyi dati ki aje su akwai mai wanki zai wanke maki su ya goge.. Washe da baki fatuha ta ce, "toh

Mom har takai bakin kofa ta dawo tare da cewa, "gobe ki shirya za'a kaiki wankin kai.. "to tace tare da yima mata godiya.. mom na fita ta shafe jikin ta da mai tare janyo kayan da mom d'in ta aje mata a saman gado farar rigar ta fara janyowa ta saka amma sai da tasha wuya sannan ta iya balle mab'allin rigar.. Saidai dai dai gwiwa rigar ta tsaya mata. "Kwarankwatsi gidan ga gidan yan'iska ne yo jifa yadda rigar ta min, skirt din ta janyo ta sa tana sawa taga ya tsaya a gwiwa shima..kut amma Qur'an mutanan sun rainani yo in ban da iskanci haka zanbi gari qafafu bude tap bilahilazi ban fita haka guri ta samu tayi zamanta tana ta kunfar baki tare da jero Allah ya isa

Mom dake zaune parlour jin fatuha shuru bata fitu ba yasa ta leqo dakin zaune ta same ta har bacci ya fara neman dauketa saboda gajiyar tafiya. tab'ata tayi tare da cewa "Fatuha... Nanta ware manyan idanunta.. mom tasakar mata murmushi, "hala kin kasa sa kayan tashi kiga yadda ake sawa.. nan mom ta shiga gwada mata masha Allah kayan sun mata kyau duk da fatuha tsine wa kayan take a zuciyar tare da jin haushi kayan

Bayan mom ta gama gwada mata ta bata dankwali ta refe kanta ruf kamar wadda tayi acuci yadda kan ya gwada sannan ta taja ta suka je parlour suka zaune saboda Sadiq sun fita da jidda shan ice cream

Bayan sun gama shan ice cream suka biya shop rite ya siya wa jidda new Teddy's masu kyau da kayan wasa jidda ko sai murna take a gajiye suka dawo gida . Sadiq na dauke da jidda a hannu shi yana mata cakulkuli tana dariya *ola* na bayan su riqe da kaya cikin sallama suka shigo.. mom na zaune tana kallo fatuha na gefan ta a takure,a ahankali Sadiq ya qaraso jidda na maqale a jikin shi ya kai room pack, mom ce ta murmusa tace, "baby har kun dawo... "yes sweet voice din Sadiq ne ya doki dudan kunnan fatuha ta waigo baki bude tana qare mashi kallo shi da jidda sakin baki tayi a zuciyarta tace dama ashe ina da raban ganin yan'. makka kai baba jinmai kwarankwatsi kin dubamin , duk wannan zancan da take idanun ta na kan su jidda , dagowar da Sadiq zeyi su kayi 4 eye's harara ya wurga mata tare da kauda kanshi, "mom wannan wacece.. murmushi mom tayi tace "wadda zata rinqa kulla da jidda diyar qanin baba jinmai ce. kallan fatuhan yayi wadda ke kallan su bata dauke ido ba harara ya qara banka mata sannan fatuha ta Ankara ashe harara yake aika mata aiko itama ta fakaici idan mom ta banka mai harara har da murguda mai baki, nanko ya saki baki yana mamakin wannan wacce Mara kunyar mai aiki ce mom ta samu wadda bata da kunya a fusace ya tashi ya ce, "keeeee!! Ni sa'an kine.. mom da ke zaune ta ce "Sadiq lafiya yarinya na zaman zamanta ka fara yi mata bala'i ka bari mana ta kwana biyu sannan ka nuna mata bakin halin naka wai me yasa kake haka ne baby. mom fada ta mai sosai cikin zafi rai ya bar parlour sannan ta shiga ba fatuha hakuri fatuha washe da baki ta ce "ba komai, mom ta gwada mata jidda ba qaramin dadi fatuha taji ba zata kulla da balarabiya bayan mom ta gama yi mata bayani sannan taqara mata da batun zata riqa gyara part din baban jidda sosai.. fatuha taji dadin hakan.
a cikin zuciyar ta kuwa cewa ta ke Qur'an daba balarabiya ba ce da wallahi bani kula da Ita.. Shi kuma wancan balaraban ni zaiwa iskaci wai dan yana da kyau. Qur'an gyara mai zama zanyi bilahilazi duk wannan maganar tana yin tane a cikin zuciyar ta

*Tah ku har kullun Salma mas'ud nadabo*

*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

https//,mobile.facebook.
com/Real-Hausa-fulani-writers-forum,-RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&_yn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.com

29_30

Mom ce ta haura upstairs ta bar jidda da fatuha zaune a parlour ,a hankali fatuha ta matso kusa da jidda washe da baki tace "Ya sunnan ki?" smile jidda tayi tare da fada mata sunan ta, sun dade a parlour zaune sannan jidda ta ja fatuha suka koma bedroom din jidda, jidda ta fara kwaso wa fatuha kayan wasa, washe da baki fatuha ta amshi teddy, kai Al Qur'an birni dadi garai yanzu sabida Allah ji wanga halita duk wasa ake da ita kai jama'a, jidda ce ta katse mata zance da cewa" Anuty garin Ku ba wannan teddy ne? nima daddy ke siyo min" dariya fatuha ta fashe da ita ke kekika san wani Daddy mtsss, kuma me Anuty da tedil (teddy) , jidda dariya tayi tace Aunty  ba sunan shi tedil ba sunan shi teddy ,Anuty kuma in mutun ya girme kane sai ka rinqa ce mai Anuty, aiyo ai mu a kauyen mu yaya ake cewa ko gwago, Ah wanga suna Qur'an dadi garai haka birni ya ke, jidda dai washe baki take tayi ta samu yar'uwa kamar ta me shegen surutu.

Haka suka rinqa zuba hira tare da wasa ita dai fatuha, zuciyar ta fes dan a ganin ta ta samu gurin zama kiran sallah magrib ne yasa suka tashi fatuha tayi alwala tare da jidda sannan suka fito Dan gabatar da  sallah.

Bayan sun gama sallah suka dawo parlour, parlour ba kowa sai baba jinmai da ke ta jera abinci ita da rabi'a washe da baki fatuha ta gaida baba jinmai da rabi'a, baba jinmai ce tace, "Ah fatuha anware kenan?" dariya kawai tayi , um ga abinci nan in kuna jin yunwa Ku zo Ku ci ki tabatar kin ba jidda ta ci ta koshi inji baba jinmai, toh kawai fatuha ta ce mata sannan baba jinmai da rabi'a suka shiga kitchen.

Kamar jira take su shige tayi tsale ta haye kujera dining area da kyar ta iya bude kulolin farfesun yan'ciki ne sai dafaifan doya da miyar kifi, tunkan ta fara ci miyan tbakinta ya tsinke, zubawa ta fara yi sai da kwanan ya kai har baki sannan ta tsayar da zubawa, jidda ko sai zaro ido take tana mamaki irin ci na sabuwar Anty ta,
lol.

Washe baki tayi tace, "Yauwa jidda sauko muci dan Qur'an ban iya ci a saman wannan abin , haka ko akayi suka sauko qasa suka fara ci, fatuha na ci tana zaro ido saboda dadi kuma ba wai qaramar loma take ba haka zata dauko doya biyo ta turawa kanta ta kuma turawa jidda.

Zaune yake saman sofa da alama daga wanka ya fito, shafe jikin shi yayi da lotion mai kamshi, yana gamawa ya feshe jikin shi da turare mai sanyi dadi wardrobe ya bude ya ciru 3quarte black sai fara t-shirt hannu rigar dai dai tamatsa ba qaramin kyau yayi ba gashin nan nashi ya kwanta abin sha'awa, ahankali ya kama handle din kofar part nashi ya fito.

Cikin natsuwa yake sakowa daga upstairs, sanye yake da bakin Sweet yayi matsifar yi masa kyau, fatuha da jidda na zaune a kasa ga plate à gabansu sai loma fatuha ke tura wa jidda, dan ita har ta koshi kuma da hannu take bata abincin, a fusace sadiq ya qaraso tare da dakawa fatuha tsawa "Keeee! Are you mad, your very stupid" futaha ko ware ido tayi washe da baki ta kalle shi tace, "Tap kai ka san wannan gwalangwatsin Qur'an" sannan ta cigaba ta dirkawa jidda doya jidda ko sai amsa take hankali kwance, lumshe ido sadiq yayi ji yake kamar ya shaqe fatuha dan haushi daka mata wata tsawar yayi ya ce, "Dan ubanki baki jin nane? uban waye yace kiyi feeding din angel ba spoon eeeh?" Turo baki gaba fatuha tayi tace, yo ni ban san inda fida (feeding) take ba ashe ba'a yaye taba Qur'an ban sani ba, sannan fatuha tace da jidda shine kika saki tinbi ina ta dirka maki abinci ,to ta yaye kanta sai ka zubar da fida(feeding)lol.

Wani irin baqin cikine ya turniqe sadiq ya qara wurga mata harara , aiko itama ta rama, yo ankan me mutun tunda na zo gidan su sai aika min hararata yake, ba Dan nayima Hajiya Alkawari zan zamna da ita iya wuya ,da sai nace banyin aikin ko ana dole ne ,kama gode wa

Allah saboda Kuna kama da larabawane shiyasa na tsaya da bilahilazi da tuni nayi tafiya ta aha, tare da gyara tsayuwar ta, sadiq ko baki ya saki yana mamaki irin wannan iskancin ta, tsawa ya kuma daka ma fatuha wadda tasa yan'hancita katsawa dan ubanki ni sa'an kine eeeeeh ido fatuha ta qara zarowa, sannan ya nuna ta da yatsa ya ce "Wallahi duk sanda na qara magana wannan dan banzan bakin naki ya maida min sai na fasa shi, ya qara wurga mata harara sannan ya sa hannu ze dauki jidda, ihu fatuha ta saka hakan yasa sadiq  juyowa yana mata kallan  wulaqance, Qur'an ba inda zaka da balarabiyannan kwarankwatsi, ko na fada ma hajiya tunda ita ta bani ita, dariya abin ya kusa ba ma sadiq amma sai ya daure ya wurga mata harara.

Mom dake bedroom taji ihu fatuha hakan yasa ta fito da sauri, ganin sadiq dauke da jidda fatuna na gefe tana ihu yasa mom   qarasowa, harara ta aikawa  sadiq tare da cewa, "Lafiya fatuha? me kuma ya miki?" turo baki tayi ta ce, "Yanzu saboda Allah hajiya ba ke kika bani wannan balarabiyar ba, na kulla da ita , to shine wai daga yaga ina bata abinci ya hau zagina har da ce min wai feda take sha" hajiya ko dariya abin  ya bata saboda ta gano abinda fatuha take nufi, sannan fatuha tace, "To shine hajiya yasa hannu ze dauke min ita Qur'an ban yadda ya maido min abuta" hajiya ta washe  baki tace "Yi hakuri fatuha ai baban tane shiyasa" aiyo toh shine hajiya be iya fada min dan girman Allah, ki ce ya ban  yarinyar dan Qur'an Santa nake tare da matse kwalla, mom ko dariya abin ke bata sadiq ko mamaki abin ke ba shi yau shida diyar shi za'a mai qarfin hali.

Toh shikenan sadiq bani jidda in ta mata wanka sai ta kawo ma ita ai shikenan anraba rigama ko fatuha, sadiq bata fuska yayi ji yake kamar ya shaqe fatuha dan haushi.

Haka sadiq ya miqa wa mom jidda tare da haurawa sama, sannan ya dau alwashin sai ya gyarawa wannan yarinyar zama dan yaga alamar da rashin kunya tazo.

Fatuha ko washe da baki ta amshi jidda, jidda ko sai raba ido take gashi cikin ta ya cika dam kamar yayi magana.....

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*

*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

https//,mobile. Facebook. Com/Real-Hausa-fulani-writers-forum,-RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial&_yn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook. com/REAL HAUSAFULANIWRITRESFORUM.com

*rip rip this page is for you my lovely one so enjoy the page this na for u no be so*😉

31_32

Washe da baki fatuha ta amshi jidda ta wuce da ita bedroom ta cire mata kaya direct toilet ta shige da ita sai da ta wanke jidda tas sannan suka fito.

Ah bilahilazi birni tayi yanzu dubi sau biyu ina sab'e ki , jidda ce ta washe baki ta ce "Anuty daddy ban san dati shiyasa" always yake min wanka yayi ma kanshi um tabe baki tayi tace yo ke ki kasan wannan, washe baki jidda ta kuma yi tace baba na fa nake nufi Anuty aiyo wai wannan baban naki ai dole yake wanka daga ganin shi ya cika tsirfa daddy nawa, um ke ni wani mai ake shafa maki in anmaki wanka smile jidda tayi ta dauko mata lotion din ta mai kamshi fatuha ta amsa, ah'ah wanga farin mai haka fa yo ai wannan kamar turare ne jidda ce ta fashe da dariya tace Anuty ba turare bane maine ga turare na chan saman dirss mirror Wanda daddy ya siyo min a uk, tir qashi me kuma uk, washe da baki jidda tace wata qasa ce haka a'a shi baban naki har shawagi yake qasa qasa tap kinga matso na shafe ki da mannan kar yaji shiru ya zo ya min tijara dan na lura dan ta kife ne baban naki ,haka ko ta shafe jikin jidda da lotion tare da anyana man a ranta ita ma ta gama shafa basilin dan ita yanzu ta zama yar birni.

Sai da ta gama shafe jidda da mai tsaf sannan jidda ta gwada mata inda night dress din ta suke kar ku ga abu komai fatuha ta gani sai ta mai sharhi bayan ta gama shirya ta tsaf, sannan

ta dauke ta dan kai ta dakin baban nata Wanda tayi ma laqabi da sangami.

Direct part din Sadiq suka wuce a hankali ta murda handle din kofar ta shiga , jidda tana ta zuba mata surutu, tana shiga parlour ta saki baki da hanci bata san sanda ta dire jidda ba a qasa wani irin sanyi dadi ne da kamshi ya doki hanci ta kasan cewa sadiq mutun ne mai san sanyi da kamshi shiyasa part din shi yafi na kowa sanyi a gidan, washe baki tayi tana qarewa parlour kallo saboda iya kar haduwa parlour ya hadu.

Jidda ko bedroom ta shige da gudu lokaci sadiq ya fito daga wanka, sanye yake da bathrobe hannu shi riqe da towel yana goge gashin kan shi jidda ta ruga ta rungume shi daddy wani irin murmushi ya saki tare da shagwabe fuska, um ni fushi nake da angel tare da daukar ta ya zaunar da ita saman bed shine saboda kinyi new Anuty kika manta daddy ko angel, shagwabe fuska ita ma tayi tare da daura hannu ta saman cheek din sadiq sorry daddy ta marairai ce kamar za tayi kuka ,dariya yayi tare da fara yi mata cakulkuli, dariyar su jidda ta ankarar da fatuha washe da baki ta nufi kofar bedroom ta bude a hankali ta shige, zaro ido tayi waje tana kallan dakin baki bude kai Amma wanga gida ya hadu kwarankwatsi yanzu gobe ni zan gyara wanga gurin , baki ta qara washe wa duk wannan maganar tana yin tane cikin zuciyarta, sadiq dake ma jidda cakulkuli tana dariya jin kamar an bude daki an shigo yasasa da gowa a hankali , ya sauke sexy eye's ball's din shi kan fatuha wani irin kallo ya wurga mata ita dinma shi take kallo tana aiyana irin kyau na sadiq tap amma dai sangami ba qaramin kyakyawa bane Qur'an, washe baki ta kuma yi tace "Amma fa sai bakin rai kamar fir'auna tir da wannan hali wallahi ga kyau ga bakar zuciya, ko da yake na kusa maganin shi ai, daka mata tsawar da sadiq yayi ne yasa ta dawo daga dogon tunanin da take tayi wiqi wiqi da ido, ur are very stupid ina maki magana kin yi shiru ehhh ?are u deaf or what tsawar da sadiq ya daka wa fatuha har wani fitsari taji ya taho mata gadan gadan ganin yana nufo ta yasa ta bude kofar tafita dakin da gudu sai da taje dai dai kofar parlour ta bude baki yadda zai jita tace Allah ya isa mugu kawai sannan ta bude kofar ta ida fita a guje sadiq dake bakin kofar bedroom yana jin ta lumshe ido yayi yana jin wani irin tsanar fatuha na ratsashi da mamakin rashin kunyar ta ,a hankali ya ja jikinsa ya koma saman bed lokacin jidda har tayi bacci shima kwantawa yayi tare da kara masu gudun AC ya ja masu blanket.

Tana isa daki ta kulle da makuli gudun kar sangami ya shigo wato sadiq toilet ta shige da gudu tayi fitsarin data matseta saboda tsabar tsawar da sadiq ya daka mata shi ya haifar mata da fitsari dole, tsoki ta ja tare da cire kayan jikin ta tayi wanka sai da ta wanke jikin ta tas sannan ta dauki karami'n towel ta daure ta fito, rigar baccin da mom ta gwada mata ta Ciro ta sa duguwar riga ce pink mai manyan follows milk rigar ta wuce gwiwa ba qaramin kyau tayi ma fatuha ba, ita kanta sai da ta yaba kyan rigar sannan ta kwanta saman bed tare da janyo blanket ta lulube ko 2 minutes ba tayi ba bacci ya sureta.

Asuba ta gari, tsaye yake gaban dress mirror yana shiri cikin uniform nashi kasan cewa yau Monday ba qaramin kyau yayi ba kofar bedroom ya kalla tare da jan tsaki sannan ya kalli bed jidda na bacci.

Fatuha ko yau bacci har da munshari ba ita ta tashi ba sai 6:00am, cikin sauri ta tashi tayi alwala tayi sallah sannan tayi wanka ko mai bata tsaya shafawa ba tayi sauri ta zura uniform din ta kasan cewa mom ta fada mata jidda na zuwa school yasa take shirin cikin sauri cikin sauri ta nufi part din sadiq dai dai bakin kofa ta tsaye gaban ta na dukan uku uku saboda ta tuna artabun da suka sha da sangami jiya kawai shahada tayi tare da qundun bala ta bude kofar ta shiga taré da yin sallama, ba kowa parlour hakan yasa ta murda handle din kofar bedroom sadiq ta hangoshi tsaye gaban dress mirror a hankali ya dago sexy eye's ball's din shi wani irin kallo ya wurga mata tare da jan tsoki, cikin tsawa ya ce "Yanzu ne time din da ya kamata ki shigo eeh? baki san tana zuwa school bane, koko rashin sanin muhinmanci ilimi yasa kika zauna baki zo ba eeh? nuna ta yayi da yatsa yace as from to day karki qara kai wannan time din baki zo ba stupid girl kawai" duk da bata san Kalmar da ya fadi aqarshe ba amma jikin ta ya bata zagin ta yayi sai da ta fakaici idan shi sannan ta bala mai harara tare da daukar jidda daga saman bed zata fita da ita har ta kai bakin qofa, ya kara daka mata tsawa yace "Kin makarar da ita? yanzu Kuma ina zaki kaita? oya wuce ki mata wanka a bathroom dina, wiqi wiqi da ido fatuha tayi dan ita bata san me ye bathroom ba, wata uwar tsawa ya kuma daka mata oh waike wata irin yarin ya ce ehh ki kai ta ban daki na kiyi mata wankan yar qauye kawai mtss, saura kuma inkin je kinmin kauyan ci jiki ba kwari fatuha ta shiga toilet din ba laifi dan kauyanci da tayi kadan ne sannan tayi ma jidda wankan, tana mata tana zuba mata surutu dauke da ita ta fito sannan ta zauna da ita saman bed sadiq na zaune saman sofa yana kallansu shafe jikin jidda tayi da mai sannan ta dau uniform din jidda zata sa mata nan fa kar ku ga zare ido dan ta rasa ta inda zata samata rigar saboda gown ce irin mai kamar biri da wando dinan tayi tsuru tsuru, sadiq jan tsaki yayi tare da fisge rigar ya Shiga sama jidda fatuha duk tana kallan yadda ya ke samata sai da ya gama shirya jidda sannan ya mata pack, daddy good morning , morning too angel how was ur night, cool daddy. good, fatuha ko ta saki baki tana kallan su.

Sai da suka gama shiryawa tsaf sannan sadiq ya dau briefcase din shi ,fatuha kuma ta dauki jidda suka sauko downstairs mom da abba na zaune a dining area har sun fara breakfast cikin ladabi sadiq ya gaishe su haka ma fatuha da jidda mom ce ta kalli fatuha washe da baki ta ce "Ya kwanan baqunta?" murmushi fatuha tayi tare da jama jidda kujera ta zauna cikin natsuwa ta shiga saving din jidda abinci, da ta gama sai ta zauna shima cikin dari dari sannan ta sa hannu cikin plate din.. wata irin tsawa sadiq ya daka mata wadda tasa fatuha fara matsar kwalla, cikin kakausar murya yafara cewa "Wai bana ce maki ki daina feeding din angel da hannu ki bane eeh" Mom ce ta kalle shi tare da wurgamai harara , baby wai me yasa ka ke haka ne eeh fada ta mai sosai sannan shima Abba ya dara da ce mai "Kai haka ake a rayuwa? kai kullun cikin zafin rai sadiq wai me yasa baza gyara halin ka bane eh baby?", shiru sadiq yayi tare da aikawa fatuha harara ita ko tayi kamar bata gani ba sai ma gwalo da ta aika mai cikin na tsuwa suka gama breakfast.

Briefcase din shi sadiq ya dau ka fatuha na dauke da jidda suka fito harabar gidan, haka fatuha ta rinqa zare ido tana qarewa yaran sadiq kallo *ola* ne ya qaraso cikin sauri tare da amsar briefcase din sadiq ya kai mai mota fatuha na biye ta shi suna zuwa gaban mota fatuha ta aje jidda cikin mota ,zata juya sadiq ya fisgota ta fado jikinsa,da sauri ya ture ta tare da taka mata qafa da booth din kafar shi ya murzashi sosai, jin za tayi ihu yasa ya matse mata baki da hannun shi da karfi yana kallan ta ido cikin ido ,idanun fatuha sun cika da kwalla tap saboda ita ka dai tasan azabar da take ji ,ture ta yayi tare da nunata da yatsa ya shige motarsa har zai tada yajiyo muryarta tana magana da yake ahankali take magna shiyasa baiji abinda take fadi,kwafa yayi ya tada motar suka bar harabar gidan. fatuha ko Allah ya isa ta Shiga jeramai tare da shigewa gidan a guje.

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//,mobile. Facebook. Com/Real-Hausa-fulani-writers-forum-RHFWF-173973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_yn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook. com/REAL HAUSAFULANIWRITERSFORUM.com

*👏🏼Godiya ta musanman ga masoya na ❤ina jin dadi addu'ar ku ta fatan alheri😍 nima ina san ku ana mugun tare*🤝🏽

*Wannan safin nakune masoya na asha karatu lafiya*❤

33_34

Parlour ta qaraso tare da share yar qwallar da ya taru à idonta, Mom na zaune saman three star tana kallo juyowa tayi cikin murmushi tare da kallan fatuha, ita ma fatuha murmushi tayi tare da fara kwashe kayan abinci da ke dining area, ah fatuha da kin bari rabi'a ta zo ta kwashe, washe baki tayi tare da cewa barshi kawai hajiya, mom murmusawa tayi tare da cewa "Ni ko fatuha da kin daina ce min hajiya nan da yafi! Ki rinqa kira na da sunnan da sadiq ke kira na" murmushi fatuha tayi tare da cewa, toh, sannan ta kwashe kayan ta kai kitchen mom kuma ta cigaba da kallan ta tana ayana wasu abubuwa à ranta,tana fituwa direct part din sadiq ta wuce ta gyara part din sosai, tana gamawa ta shiga toilet shima toilet din sai daya sha wanki dan fatuha gyara tayi bana wasa ba, tana gamawa ta washe baki tare da zama saman sofa tana qarewa dakin kallo hotan sadiq ta hango manne jikin bango tangameme shi da kausar sunyi murmushi.

A hankali ta qaraso wajan hotan tare da washe baki tana kallan hotan, ohni ashe sangami na murmushi ah ji yadda ya washe hakura dan Allah ai da haka yake kullun daya fi kyan gani, murmushi tayi tare da daura hannu saman pic din ,um gaskaya kana da kyau Qur'an chan kuma sai ta bata fuska tare da cije lips dinta dariya tayi sannan tace, "Kwarankwatsi zaka zo ka same ni wallahi ba kasan *wacece fatuha ba yar gidan baffa jauro*" sannan ta bala wa pic din harara ta fita daga part din.

Tana sakowa downstairs ta shige bedroom dita wanka ta kumayi, tana fitowa ta shafe jikin ta da lotion tana shafa lotion din tana washe baki , Qur'an wanga mai sanyi garai ga kamshi tap wallahi birni tayi sai da ta gama shafe jikin da mai tas  sannan ta sa wasu uniform din.

Cikin school yayi parking tare da fituwa ya budewa jidda murfin mota smile ya mata me sanyi, sannan ya ciro mata lunch box  dita ya miqa mata, bata fuska jidda tayi tare da cewa "Daddy am going to miss u daddy" saman kanta ya  shafa  tare da cewa "Sorry angel soon za'a tashi aiko se  inna dawo gida sai muje shan ice cream ko my angel" washe baki tayi tare da yi mashi pack sannan ta shige class yana kallanta har ta shige sannan ya sauke ajiyar zuciya ya shige mota yatafi.

Bayan ta gama shirin ta tafito parlour ba kowa sai kamshi da ke tashi na girki, kitchen din ta nufa tare da sallama baba jinmai ke girki sai rabi'a na gyara salat murmushi tayi tare da gaishe

su washe da baki baba jinmai ta amsa taré da cewa "Yar albarka kin zo taya ni aiki ne?" daga kai tayi alamar  Eh, can kuma fatuha ta bata fuska tare da cewa baba wai ina kike kwana jiya kika barni ni ka dai, washe baki baba jinmai tayi tare da cewa, ah aini fatuha banan nake kwana ba a gida na nake kwana se da safe na zo ,turo baki fatuha tayi tace gaskiya baba yau binki zanyi,ah ba za'ayi haka ba ki zauna nan nima ai gidan bacci ke kai ni baba jinmai ta shiga lalaba fatuha.

Taya su aiki tashiga yi sosai can baba jinmai  ta miqawa fatuha kwano ta debo  man da za'a soya kaji a stor, wani irin murmushi tayi tare da Shiga stor din nan ta zuba a kwano tare da qule wani a leda tasa a aljihun skrit din ta tafitu sannan tayi ma baba jinmai sallama ta koma parlour ta cigaba da kallo tayi tana washe baki, mom ce  ke saukowa daga stairs sanye da mayafi da car key a hannu ta kallan gefan da fatuha take tayi tare da cewa "Oh na manta, nayi da ke jiya zan kai ki gyaran kai wallahi na manta gashi yanzu fita zanyi" murmushi fatuha tayi ta ce ba komai gobe maje , toh shikenan inna manta ki tuna min please toh ta ce mata tare da rakota har bakin kofa sannan ta koma parlour ta cigaba da kallo.

Tana kallo har bacci ya kwashe ta a parlour, cikin bacci taji ana sallama tashi tayi tare da ware idanuwan ta ta sauke su kan  Anuty bilki, ware ido ta kuma yi tana qarewa Anuty bilki kallo dan tabas tayi mata kama da sadiq sai dai sadiq ya fita kyau sosai qaqaro murmushi tayi bakin ta na rawa ta gaida Anuty bilki zama tayi tare da amsawa tayi ma fatuha murmushi, um hajiyar ba ta nan ta fita, murmushi Anuty bilki tayi tace ai na sani munyi waya yanzu zata dawo ba dadewa zatayi ba, fatuha kitchen ta shige ta fada ma baba jinmai anyi baquwa lemo ta zuba mata a tray da kyan motsa baki tare da ce mata gata nan zuwa taga baquwar , Anuty bilki ko kayan jikin ta ta rage tare da haurawa upstairs dan ta watsa ruwan , fatuha na zuwa parlour taga ba baquwa sai afra da ke bacci saman kujera baba jinmai ta qwalawa kira ta fitu a rude ita ma Anuty bilki da shigar ta bedroom kenan ta sauko  turus baba jinmai tayi a parlour lafiya fatuha me ya faru baba wallahi baquwar ce ban gani ba gashi ta bar yar ta a nan Anuty bilki ce ta qaraso, washe baki baba jinmai tayi tace, ah wai Bilkisu kike nufi ai yar gidan ce amma tayi aure ganin gida tazo yi murmushi fatuha tayi tace, "Aiyo aini ban sani ba shiyasa" itama Anuty bilki dariya tayi sannan ta haura sama tare da ba  fatuha afra ta kula da ita kafin ta fito.

Misalin karfe 12:00pm jidda ta dawo school ita da Jamal, kasan cewar school daya suke da yan'yan Anuty bilki cikin murna fatuha ta tare su , kasancewar fatuha me san yara ce shiyasa ta ja jidda da Jamal bathroom ta masu wanka suka fita tas sannan ta sa masu kaya ta zo da su dining area suka ci abinci sannan ta dawo parlour da su suna dan taba hira sama sama, can sai ga hannan ita ma ta dawo daga school washe da baki ta qaraso ta fada jikin Anuty bilki wash mom I am tied sorry sweet je kiyi wanka ki canza kaya fatuha ko washe baki tayi tana qarewa su hanan kallo, tsakanin hanan da fatuha kunsan sa'anin ne shiyasa tunda ta shigo fatuha ke kallan ta hakan sai yasa ta tuna da fatsima kwalla taji ta zo mata gaskiya ta San tayi kewar su inna da fatsima daki   ta shige tayi kwanciyar Hanan ce ta shigo ta shige toilet tayi wanka

sannan ta fito daure da towel suna hada ido da fatuha tayi murmushi.. sannu ki ,yauwa fatuha tace mata, nan hanan ta fara janta da hira sama sama, hanan dama kawa take  so  gashi ta samu aiko nan hira ta barke tsakanin su in fatuha ta fadi wani abu hanan tayi dariya sosai har cikin ta ya kule.

Sai yama likis su hanan suka tafi, har bakin mota fatuha ta rako su ita da jidda kamar kar su tafi saboda fatuha taji dadi hirarsu da hanan.

Bayan sun tafi suka koma bedroom din  jidda, taci gaba da zubama fatuha surutu can kamar kamar aj mintsi neta ta tashi ta koma parlour kadan kadan  ta leqa waje.

Motar sadiq ce ta kunno kai cikin gidan, wani irin murmushi fatuha tayi tare da yin Sauri da haura sawa, upstairs part din sadiq ta shige direct toilet din shi ta shiga ta fido da man da ta kule a leda ta juye shi qasan toilet din sannan ta fito tana dariya tana waigen part din ji tayi ta fada jikin mutun, idanunta ta zaro cikin tsoro da fargaba ,tayi  lamo tana jiran aradu, wata irin tsawa sadiq ya daka mata tare da ture ta ta tafi tagalgal zata fadi ya fisgota tare da qanqance idanu yana kallonta , fatuha kuwa har ta fara matsar kwalla, cikin kakausar murya yace "Ke wace irin mahaukaciya ce ? ya karasa zancan da murya mai sauti" Wanda yasa fatuha sakin kuka saboda a iya rayuwar ta ba Wanda ya taba mata irin wannan ihu, kuka take sosai tana girgiza mai kai janta ya cigaba dayi har sai da ya kai last stairs sannan ya ban kada ta ta fadi qasa tayi zaman yan bori nunata yayi da yatsa tare da cije lips din shi ya dau briefcase din shi ya shige part nashi fatuha ko kuka tayi san ranta da kyar ta tashi saboda qugun ta ya riqe bedroom ta Shiga  shiga à toilettes dan watsa ruwa, bata jima sosai ta fito daure da tawel yashirya cikin Riga da skt na yan kanti sosai tayu kyau masha Allah ta fito parlour can kuma sai tayi murmushi ta haura sama.

Sadiq na Shiga daki saman bed ya fada tare da lumshe ido, yana maida numfashi a hankali wata irin tsanar fatuha na ratsashi ware sexy eye's dinshi yayi tare da tashi tsaye, ya je gaban fridge ya bude ya curo fresh  milk ya sha sannan ya fara jin zuciyar shi ta daina kuna, ya tashi ya cire uniform dinshi yashiga toilettes .

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//,mobile. Facebook.
Com/Real-Hausa-fulani-writers-forum-RHFWF-173973194167/?refid=52&red
opare-speed_dial_yn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook. com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.com

*hehe qawalliya roman jaba wannan page naki ne amal*
35_36

A hankali ya murda handle din kofar toilet ya zura kafar shi ji kake suuuu gwajaf yayi faduwar yan bori, fatuha da ke maqale bakin kofa ta kasa kunne jin faduwar sadiq ya sata bushewa da dariya har da rawar tanbola dan shauqi bude kofar tayi ta shigo bedroom din tana shigowa ta qara fashewa da dariya, saboda zaman da sadiq yayi a qasan toilet qarasowa tayi bakin toilet din, a hankali sadiq ya dago sexy eye's ball's din shi ya sauke su kan fatuha wani irin kallo ya wurga mata dariya ta kumayi tare da bala mai harara, ah me kyau ansha qasa dariya ta kumayi tare da gyara tsayuwa toh me kyau bari na kirama hajiya ta kirama mai dauri saboda nasan ka goce koka kare ta qara bushewa da dariya ,sadiq ko cije lips yayi yana jin wani irin radadi da tsanar fatuha na ratsa shi kallan banza ya wurga mata yana qoqarin tashi amma ya kasa wani irin radadi qugunshi ke mai, cije lips yayi ya zauna dan baya iya tashi dariya fatuha tayi tace, "Kwarankwatsi baka iya tashi Qur'an ka bugu ba kadan ba qila ma ka kare ko ka goce", dariya ta kumayi ta nuna idanuwan ta da yatsu biyu sannan ta nuna idan sadiq Wanda ke binta da kallan tsana, daure fuska tayi tace ka tuna turani da kayi dazu a matatakala na fadi? toh Allah ya isa ba kasan wacece fatuha ba ko? kaje kauyan wudil ka tanbayi *wacece fatuha diyar baffa jauro qawar fatsima*, sannan ta qara fashewa da dariya ta ce "Kuma daga yau zan fara nuna ma irin kallan haukar fatuha ,kuma wallahi kasani fatuha ba'a mata abu ta hakura ko ta dangana, a lokaci ba hakuri nayi ba shi yasa na rama, ta bala mai harara tana qoqarin fita, sadiq ko wani miyan bakin ciki ya hadiye yana jin wani irin bakin ciki ,ji yake kamar ya tashi ya shaqe fatuha har sai numfashin ta ya kusa daukewa ya sake ta lumshe idanuwan shi yayi.

Washe da baki fatuha ta fito daga part din sadiq sai da ta dai daita kanta sannan ta fara matsar kwallar gulma, bedroom din mom ta nufa tana yarfe hannu a hankali ta bude kofar mom ta hango kwance saman bed tana karanta azkar, cikin na tsuwa ta shigo tana matser kwalla mom ce ta dago su kayi 4eye's da fatuha murmushi ta saki tana qoqarin tashi ta ce, fatuha qaraso mana jikin kofa ta qara maqalewa tana matsar kwallar gulma da kyar ta iya furta mom dama baban jidda ne ya ce na kawo mai ruwa ina shiga dakin na ganshi ya fadi a kewaye kuma ya kasa tashi tana ida zancan ta fashe da kukan munafurci mom tashi tsaye tayi cikin rudani muje bedroom din nashi naga ko lafiyar baby, mom na gaba fatuha na baya tana aika gwalo suka shige part din direct bedroom din sadiq ta shige yanan zaune inda fatuha ta barshi yayi yayi ya tashi amma ya kasa mom ce ta qaraso tare da kiran sunan shi cikin damuwa ya juyo yana kallan fatuha na bayan mom tana matsar kwalla da sun hada ido da sadiq ta aika mai gwallo shikuma ya aika mata harara, sannu baby kaji bari mu taimaka ma ka tashi, no mom ba ku iyawa a miqomin phone din tana saman stool na kira *ola* da *Sunday* cikin sauri mom ta miqa mai wayar fatuha na gefe rabe zuciyar ta fes.

Bugu daya biyu *ola* ya daga kiran sadiq, sadiq ya sheda mashi yana neman shi, shi da *Sunday* cikin Sauri suka qaraso bedroom din, ganin su mom tsaitsaye yasa jikin su *ola* yin sanyi hango sadiq su kayi zaune a toilet yayi zaman yan'bori a hankali *ola* ya qaraso tare da gaida mom cikin hausar su wadda bata fita amsa mai tayi sadiq a hankali ya ce *ola* taimaka min na tashi kai da *sunday* OK boss Sunday d ola suka taimaka ma sadiq ya miqe suka daurashi saman bed mom sai sannu take mai itama fatuha sannu tamai wani irin mugun kallo ya mata, ya kauda kai mom ce tace baka ji fatuha na ma sannu bane lumshe ido yayi tare da ware su yace ban ji ba ya qara maida idanuwan shi ya rufe, wayar shi mom ta Curo ta kira doctor yakub ba ayi minti 39ba sai ga doctor yakub riqe da briefcase din shi ya shigo, fatuha ta mai isowa har bedroom din sadiq gaida mom yayi sannan ya shiga duba sadiq tare da tataba inda ya bige sannan yayi yan rubuce rubuce, gyaran murya yayi ya ce Alhamdulillah buguwa ce amma be goce ba kuma be kare ba abin ya zo da sauki mom murmushi tayi tare da hamdala, sannan doctor ya bashi magani da ze shafa da kuma na ciwan jiki sannan yayi ma su mom sallama ya tafi, mom da fatuha kuma suka fita cikin cool voice nashi sadiq yace da ola ya taimaka ya kai shi bathroom ya watsa ruwa amma ya fara goge man da ke zube a toilet sai da ola ya wanke toilet din tas sannan ya taimakawa sadiq ya shiga toilet, ola na bakin kofa yana jiran sadiq yana gama wanka ya kira ola ya taimakamai ya fito ko da ya fito ola ya fito mai da jalabiya milk bayan ya gama shafe jikin shi da mai sannan ola ya taimakamai ya shafa mai magani sannan yasa jalabiya ya koma saman bed ya lumshe ido ,ola ne ya bare maganin da ruwa ya bashi ya sha yana gama sha ya lumshe ido bacci mai nauyi ya dauke shi, ola ya koma saman sofa ya zauna Sunday kuma ya kwashe kayan da suka baci da mai ya fita.

Wash Qur'an yau nayi aiki inama a ce fatsima na kusa ta qara bushewa da dariya, ta kalli bed jidda na kwance tana sharar bacci dariya tayi tace "Allah sarki angal wato(angel) yau na naqasa baban ki se hakuri angal na san in zafi yayi zafi har sunnan ki sai ya fada ta kara fashewa da dariya tare da rausayar da kai ,Amma fa gaskiya ban duba mai ba ta ida zancan tana cire kayanta ta shige toilet tayi wanka daure da towel ta fito lokacin jidda tatashi, murmushi tayi ma jidda tare da daukarta dan lokaci 4:00pm saura malamin jidda ya kusa zuwa wanka ta mata a tare suka fito suka shirya sallah su kayi saboda anata kiraye kirayan sallah bayan sun gama sallah fatuha ta rako jidda har waje lokaci har malam ya zo ji tayi itama tana sha'awar karatun, cikin gida ta juya tare da Shiga bedroom din mom, mom na zaune saman daduma karasowa tayi tare da murmushi ta tanbayi mom itama tana so ta fara zuwa malam na qara mata karatu mom ta ce babu komai washe da baki ta fita ,taje wajan malam itama ba laifi fatuha ta Dan san sururi da yawa sai karatun nata ba tajiweed shine ka dai ya dan bata karatun ba laifi sunyi karatu sosai inda fatuha ta natsu tana ta karatu, dan wannan malamin ba karamar malami bane.

Bayan sun gama karatu misalin karfe 6:00pm suka shigo gida cikin farinciki, mom na zaune saman three star tana kallo abba na gafenta gaishe su tayi cikin na tsuwa sannan ta shige daki jidda kuma ta fada jikin abba tana zuba mai surutu kiran sallar magrib ne ya sa abba tashi ya wuce masallaci ,jidda kuma ta shige bedroom lokacin fatuha ta fito daga toilet daure da tawel tayi arwalarta à toilettes din, murmushi fatuha tayi tace, "Jidda yi maza kiyi alwala kiyi sallah kiyi ma baban ki addu'a, be lafiya kinji" waro ido jidda tayi tace Anuty me ya samu daddy tareda ruga wajen kofa zata fita, janyo ta fatuha tayi tace, yi hakuri mu fara yin sallah sai na kai ki kinji jidda toh tace mata tana matsar kwalla fatuha kuma na lalashin ta.

Bayan sun gama sallah fatuha ta shirya jidda cikin night dress din ta blue n white wando da Riga ba qaramin kyau su kayi mata ba ,ta ja hannu ta suka wuce part din sadiq.

Suna Shiga suka samu ola zaune saman sofa, sadiq ma zaune saman bed ,yana shan coffee da gudu jidda ta fadi jikin shi tana kuka, daddy lalashin ta ya shigayi angel menene yake damun ki ,bata fuska tayi tace "Daddy ashe baka da lafiya shine baka fada min ba? ta ida zancan tana matsar kwalla" sorry angel lafiyar daddy qlau, waya fada maki daddy be lafiya? fatuha ta nuna da ke manne jiki kofa kamar ka ce tak ta arce wani irin kallan tsana ya gefa mata tare da qaqaro murmushi yayi wa jidda yana kallan fatuha , angel na rasa yadda akayi grandma ta samomaki new Anuty mahaukaciya ya ida zancan yana kallan fatuha ido cikin ido, kauda kai tayi tare da turo baki gaba, daddy new Anuty ba mahaukaciya bace ba injiwa ya ce maki ba mahaukaciya ba ce fatuha ko wani irin tsoki ta ja tare da jan kofar bedroom da karfi ta fita lumshe ido sadiq yayi yana tunanin irin hukuncin da zaiyi ma fatuha in ya tashi.

*Taku har kullun mai qaunar ku Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*

👮🏽

*writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//,mobile. Facebook. Com/Real-Hausa-fulani-writers-forum-RHFWF-173973194167refid-52&red opare-speed_dial_yn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail. com

*Facebook*:www.Facebook. com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.com

37_38

Fatuha bedroom ta shigo tare da yin sallah isha'i saboda tana da arwalata, bayan ta gama sallah ta rage kayan jikin ta yar rigar bacci tasa wadda yanzu ta zamar mata jiki, in batasa ba ko bacci bata iyawa kanta ta qarewa kallo ta cikin mirror ita kanta mamaki kanta take saboda ta wani qara haske da kyau sannan komai na jikin ta ya ciciko rufe idanuwan tayi tare da ware su, ta sauke su kan qirjinta Wanda yanzu ya fara cikowa sosai, murmushi tayi tare da jin kunya ta bar gaban dress mirror din ta fada gado tare da yin addu'a lumshe idanuwan tayi sadiq ne ya fadu mata a rai tayi sauri ware idanuwan ta tare da sakin dariya saboda duk lokaci da ta tuna da zaman yan borin da sadiq yayi sai ta dara a haka har bacci ya kwashe ta.

Duk juyi dayayi sai ya zabga tsaki saboda bacin rai ola ne ya juyo ya ce boss are u ok , lumshe ido yayi yace "Yess" ok good night, boss if u need something talk to me please,  ok  tare da juyawa ya gyara kwaciyar  shi a hankali ya shafa gashin jidda sannan ya lumshe ido, daya lumshe ido fatuha yake gani tana mai dariyar qeta wata irin iska ya furzar mai zafi daga bakin shi ba abinda zai hana shi yima fatuha horo mai tsanani Wanda ko wani aka ce tayima irin cin kasin da ta mai ba zatayi marmarin maimaitawa ba, tsaki ya kuma ja saboda takaici a haka har baccin barawo ya dauke shi.

*Asuba ta gari..*

Tunda asuba fatuha ta tashi saboda tasan in yau bata tashi da wuri ba Allah ka dai ya san jarabar da sadiq ze mata ,dan tsaki ta ja can kuma tayi murmushi tace, ko ba komai ina ganin mai kyau Qur'an naji dadi, sannan ta shige toilet tayi wanka tare da yin brush da dauro alwala tayi sallah sannan tasa uniform komawa tayi ta zauna saman bed tana kallan agogo karfe shida take so ta shiga part din sadiq.

Ba laifi daya tashi sallah asuba kafar ta saki tunda har ya taka bada taimakwan ola ba, toilet ya shiga yana shiga abinda ya faru jiya ya fara dawo mai kamar yanzu, murmushi yayi yace fatuha baki ji sannan ya qara jan tsoki ya dauro alwala tare da yin wanka ya fito ko da ya fito jalabiya white yasa ya tada sallah yana gamawa ya koma ya kwanta saboda har yanzu jikin nashi yana jin shi wani irin.

Bude handle din kofa tayi ta fito direct part din sadiq ta wuce kai tsaye, bedroom ta shige kallo daya tayi ma daki hango ola tayi kwance yana ta share bacci har da munshari saboda dadi, dariya ta so ta kubuce mata ta guntse dariyar kallan bed tayi sadiq kwace rungume da jidda murmushi tayi a hankali ta qarasa tare da leka fuskar sadiq ta ga dai bacci yake cikin dubara ta shiga janye jidda daga jikin shi, hannu ta ya kama a tunanin shi jidda ce zaro ido waje fatuha tayi tare da fara matsar kwalla a tunanin ta tashi yayi jin beyi magana bane ya sata lumshe ido a hankali ta zare hannu ta ta dau jidda suka fita, direct bathroom ta dire jidda ta fara yi mata wanka , washe da baki jidda tace Anuty good morning , tap ke kika san wannan dariya jidda tayi ta ce inakwana fa nake nufi Anuty aiyo aini ban sani ba, a ina ake koya maki wannan abun wai washe baki jidda tayi tace "A school "aiyo wai makarantar da zaki yanzu daga mata kai jidda tayi Alamar eh, murmushi fatuha tayi tare da daukar jidda suka fito bedroom ta dire ta saman bed tare da janyo lotion tana shafa mata, kai Amma gaskiya yarannan nada dadi jidda zaki rinqa koya min ko murmushi Jidda tayi tace Anuty kije daddy ya fara koya maki nima ai shi ya fara koya min ta ida zancan tana washe hakura, fatuha zaro ido tayi tace tap lalai yarin ya har yanzu baki san bakin halin ubaki ba Qur'an wannan zancan tana yin shine a zuciyar ta, washe baki fatuha tayi tace ah ni nafi san ki kowa yamin kinji kinga daddy aiki yake zuwa ko, daga kai jidda tayi tare da cewa toh Anuty zan koya maki murmushi fatuha tayi tare da zurawa jidda uniform suka fito dining area lokacin su baba jinmai sun gama jera komai bude kololin ta fara marfesun kaji ne da soyanyan chips da egg da tea, murmushi fatuha tayi dan tunda ta zo birni ba abinda keyi mata dadi kamar chips shiyasa duk sanda akayi sakin tunbi take taci sosai zuba ma jidda tayi a plate tare da jamata kujera ta zauna ,zata fara feeding nata kenan sai ga su mom sun iso , gaishe su tayi cikin ladabi suka amsa plate ta janyo ta fara saving nasu mom sai murmushi take ita dai fatuha ta mata ko Dan abin dariyar ta ta cikin saving nasu sai ga sadiq ya qaraso dining yana tafiya a hankali yana dingishi ,a hankali fatuha ta kalli qafar wata irin dariya ce ta zo mata saboda yadda yake harba kafar kamar tsangal gumtse dariyar tayi ta cigaba da abinda take shiko sai aika mata mugun kallo yake , cikin na tsuwa ya qaraso wajan

mom tare da yi mata pack a goshi ita da abba, abba murmushi yayi tare da shafa sumar shi, baby ya jiki shagwabe fuska yayi yace abba da sauki ,good amma dai gaskiya yau baza kaje aiki ba ko dan bata fuska yayi ya ce zani abba, gaskiya baby bazaka office yau ba ka bari zuwa gobe ka warware sosai, abba,shhh kawai ka hakura kaji ya ida zancan yana shafa gefan fuskar sadiq fatuha ko Sakin baki tayi da hanci, tace "Ohni sangami duk wani shaqiyanci ya iya, yo in banda iskanci qatoto da shi sai zuba shagwaba yake sai ka ce Jidda kai kwarankwatsi mai kyau dan bariki ne "duk wannan maganar tana yinta ne a zuciya kallan da sadiq ya wurga mata ne yasa ta dawo hankalin ta Jidda ya janyo jikin shi yau daddy ne zeyi feeding angel so bana buqatar ganin ki a nan tare da warce spoon din hannu fatuha, mom ce ta bala mai harara bata fuska yayi kamar qaramin yaro ya cigaba da feeding din jidda tana mai surutu, fatuha ko qoqari tashi tayi mom tace,"Ah fatuha aike sauki kika samu zauna ki ci abincin ki kan lokaci" murmushi tayi tare da kada kai ta zauna ta zuba dai dai cin ta tasa hannu ta fara cin hankalin ta kwance tana ci tana lumshe ido saboda tana san chips sadiq bala mata harara ya ke tayi wata loma da tayi sai da abin ya kusa bashi dariya da haushi duk suka hade mai ita ko ko a jikin ta su mom ma har karsu suke.

Bayan angama breakfast har bakin mota sadiq ya raka jidda, fatuha na riqe da lunch box din jidda sai da ta tafi sannan suka juyo zasu koma gida, da gudu fatuha ta wuce sadiq sai da taje bakin kofa sannan ta juyo ta mai gwalo tare da kwakwayar yadda yake tafiya ta fashe da dariya ta shige da gudu cije lips din shi yayi tare da tura hannu shi cikin sumar sa, oh Allah ka bani inkwan cima yarin yar nan sannan shima ya qarasa parlour ko da ya shigo ba kowa sai baba jinmai da ke kwashe kayan breakfast, gaishe ta yayi ta amsa washe da baki, part din shi ya wuce ya murda handle din kofar ya ji rufe mamaki ne ya rufe shi fatuha da ke jingine jikin kofar tace, me kyau kwarankwatsi ban budema kofar nan sai na gama aiki na Dan nasan halin ka kai mugune wallahi, ka na shigowa zaka bigeni sadiq da ke wajan kofa yayi sororo yana mamakin raini da fatuha ta mai cige lips yayi tare da barin gurin saboda ya san idan ya cigaba da tsayawa har kashe ta sai yayi dan bacin rai ,fatuha jin ya tafi yasa ta cigaba da aikin ta tanayi tana yan'wake wakyan ta har ta gama tuni daki yayi kyau sosai sannan tabi part din da turaran wuta tuni part din ya dau kamshi da kyau sannan ta qara gudun AC dakin ita kanta sai da taji kamar tayi bacci dan Kyan da part din ya mata.

A hankali taje bakin kofa ta murda handle ta leqa taga ba kowa, sannan ta fito da sauri ta wuce sadiq da ke kwance saman three star idanuwan shi lumshe kamar me bacci yana kallan fatuha ta ruga daki da gudu ta kule, tsoki ya ja tare da tashi duk kiyi ki gaba zan kamaki ne tare da wucewa part nashi dan bacci yake ji ko da ya shiga part din shi da kanshi sai da yayaba kyan da part din yayi, ga kamshi se tashi yake da sanyi irin yadda yake so lumshe ido yayi ya ja jiki ya hau bed ya kwanta.

Tana shiga bedroom kayan jikin ta ta rage ta shiga toilet, tayi wanka sosai dan yanzu ba qaramin jin dadi take ba in tana wanka amma da a kauye sai anyi da gaske ,yanzu ko fatuha ansan muhinmancin wanka, daure da towel ta fito ta goge jikin ta tare da shafe jikin da lotion mai kamshi da feshe jikin ta da turare yar huda da murza duk ba wata kwalliya tayi ba masha

Allah fatuha tayi kyau, uniform din ta ta zura sannan tataro gashin ta Wanda ya cure gudaya tana qoqari kamashi amma ta kasa saboda yawan shi da tsaho bata fuska tayi tace, "Allah sarki inna da kina kusa da kin gyara min magana da su kayi da mom ce ta fado mata daure kan tayi da sauri ta haura upstairs dakin mom ta shiga ba ta nan neman ta ta shiga yi, kitchen ta shiga tare da tanbayar su rabi'a ina mom, tace mata tana part din abba ,toh tace tare da komawa parlour ta samu wuri ta zauna tana kallan film din India tana washe hakur.

Mom ce zaune da abba a bedroom din shi tana zaune saman kujera a hankali ya qaraso ya rungume ta ta baya, murmushi tayi, madam kullun qara kyau kike baki tsufa gashi har da jikoki, dariya tayi tace "Ya za'ayi na tsufa bayan mijin kullun yaro yake komawa" hancinta ya ja cikin tsokana , um next week zan koma uk kan maganan gaskiya this time around ban tafiya ni ka dai, tare nake so mu tafi murmushi mom tayi tace "Kamar kasan abinda ke raina kenan smile yayi um kuma sai gashi na rigaki fada ba, ya ida zancan tare da yi mata kiss a kumatu, ni ko abban sadiq kunyi waya da jawad kuwa? dan murmusawa yayi yace "Eh jiya munyi waya ya ce min yanzu shukura tsohhon ciki gare ta, so yake in ta haihu sai su zo ganin gida murmushi mom tayi ,Allah ya sauke ta lafiya kamar kasan nayi missing nashi wallahi ya kamata jawad ya dawo Nigeria da aiki amma nasan ba lalai ne yazo ba saboda na lura yafi san London sosai , um ke dai ki ce danki kike san gani yauwa gobe ki shirya ina so muje wajan ammi muyi masu sallama kafun mu tafi ,to tace mai tare da tashi zata fita janyo ta yayi jikin shi please in kinje karfa ki dade ki bar tsohon mijin ki da jira kinji murmushi tayi tare da kashe mai ido.. lol ah tsofafi na konewa hehe.

( shawara ga mata please mata ya kamata musani tsufa baya hana soyayya karki ce dan kina da manyan ya'ya ki ce ke kin girma ita soyayya bata girma, kuma gyara da tatalin miji shi ke qara dankwan soyayya, so da yawa wasu matan suke jawa maza jansu bin mata saboda kina ganin kin girma komai sai ki daina ,in mijin ki mai so ne daga nan zai fara bin ya'ya cikin shi a waje suna mai yana jin dadi please mata mu kiyaye) .

Fatuha da ke zaune saman kujera tana kallo, mom ce ta sauko daga upstairs, cikin ladabi fatuha ta gaishe ta tare da tuna mata maganar gyaraan kai , toh shikenan je ki shirya mu tafi , mom bada wannan kayan zani ba eh kisa kayan gida toh tace mata ta shige bedroom , mom ko part din abba ta koma ta tanbaye shi zata fita ya bata izini, sannan ta dawo dakin ta ta shirya cikin atamfa black mai ratsin red n yellow bubuce mai kyau tuni mom ta fito sosai bedroom din fatuha ta wuce tsaye, ta same ta ta rasa kayan da zata sa washe da baki mom ta qaraso, fatuha har yanzu baki shirya ba shagwabe fuska tayi taca "Wallahi mom na rasa kayan da zansa ne, zabamin dan Allah "to tace mata wata hadadiyar gown mom ta janyo brown colour mai ratsin milk da Stone's a jikin rigar mai dogwan hannu ce sai veil milk , masha Allah fatuha ba qaramin kyau kayan suka mata ba cib suka mata qirjin ko kamar tasa bara saboda yadda kayan suka mata rolling veil din tayi da gashin ta data daure sai abin ya bada kala ta fito fes, takalmi tasa black mai kyau suka fito , direct parking space suka wuce mom ta jasu suka fita sai fatima salon da ke gandu.

Basu wani dade ba a Solon din ba sosai an gyara gashin fatuha Dan ko ba'a sa mai ba saboda laushishin gashin ta dan in aka sa mai, ze iya konewa gyara shi kawai akayi masha Allah ita kanta fatuha sai da ta tsorata da gashin ta saboda har qugunta ya kai, da yaji gyara amma sai ya rage yawa su Kansu yan wajan yaba gashin su kayi  ana gamawa suka dawo gida, a parking space mom tayi parking suka fito har zasu shiga gida sai ga driven jidda  ya kunno kai yayi parking da gudu jidda ta qaraso tare da rungume fatuha tace "Anuty kinyi kyau ,waya maki kawalliya?" dariya fatuha tayi dan ita ba Wanda ya mata kwalliya daukar jidda tayi suka qaraso parlour sadiq na zaune saman two star yana shan coffee gefensa kuma baba jinmai ce tana dan taba hira da shi da alama tafiya zatayi.

Cikin sallama suka qaraso, sadiq ya amsa sallamar, fatuha  ke dauke da jidda , jidda ta zame daga jikin ta ta Ruga wajan sadiq ta rungume shi wasa ya shiga yi mata tana dariya  qarasowa Mmy tayi ta zauna saman three star ta ce "Oya a wuce aje a cire uniform, kin bar Anuty na jiran ki " sadiq ne ya dago ya kalli fatuha ya wani tabe baki tare wurga mata harara ya miqa mata jidda, baba jinmai ko sai yaba kyan da fatuha tayi take tare da yima su mom sai da safe fatuha kuma ta ja jidda zuwa bedroom.

*Taku har kullun mai qaunar Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

*📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★
https://mobile.facebook.com/Real-Hausa-Fulani-Writers-forum-RHFWF-173984973194167/?refid=52&ref=opera_speed_dial&__tn__=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail. com

*fan's ana mugun tare dinnan sosai*🤝🏾

39_40

Bayan ta gama ma jidda wanka ta shafe ta da mai tare da saka mata kaya jeans n t-shirt tasa mata.. riga pink wando bleu sannan ta gyara mata gashin ta. Aiko tuni jidda tafito tayi kyau masha Allah. toilet ta koma ta dauro alwala kasan cewa 4:00pm tayi ita da jidda suka gabatar da sallah suna idarwa fatuha ta cire veil din kanta tana kallan gashin ta a mirror tana washe baki, jidda ce ta ce "Anuty gashin kine haka.. jiyowa fatuha tayi washe da baki tace "kema kin gani ko. Ai Allah daga yau na gama yawo da dankwalli wallahi wannan gashi kamar ba nawa ba. "gaskiya Anuty kina da gashi dama ki qaramin.. Jidda ta ida zancan tare da washe hakura.. Murmushi Faruwa tayi tare da maida dakwallin ta janyo hijabinta dana jidda suka  wuce wajan malam

Sosai suke karatun. Damma karutun ya zo ma fatuha da sauki dan duk wani qari da malam ya mata jiya ta juye mai shi.. Shikansa yana yabawa da qoqarinta..  qara musu yayi. Dan haka basu suka shiga gida ba sai 6:00pm

Sadiq dake tsaye gaban dress mirror yana gyara sumar shi a hankali ya ji anbude kofar dakinsa... Aiko cikin zafi rai ya juyo a tunanin fatuha ce ta zo mai da wani saban rai ni sai idanuwan shi ya gane mai majid...😀

bata fuska yayi tare da juya mai baya.. smile majid yayi ya qaraso with full confidence nashi , "big man fushi kake dani ko.

kauda kai sadiq yayi ya nufi wajan drowe yana ciro kayan shi.

murmushi majid yayi tare da zama saman sofa tsaf.

sadiq ya gama shiryawa fuskar shi daure ya dau phone inshi da ke bedside drowe. ze fita majid ya riqe mashi hannu tare da shagwabe fuska sorry bros, juyawa sadiq yayi ya wurga mai harara "leave me alone tare da fisge hannu shi ze murda handle kofar kenan majid yace, "haba  sadiq. am sorry nine fa majid. juyawa sadiq yayi ya kalle shi , ya qara bala mai harara "kasan da haka shine ka manta dani ko. "sorry kasan bana zama sosai shiyasa amma ai na kusa dawowa nan da aiki. Kaga dawo ka zauna muyi magana.

Jin hakan yasa sadeeq sakin handle din ya dawo ya zauna , "baby meya samu qafar ka naga kamar kana dingishi

jan tsaki sadiq yayi ya ce "tsautsayi ne kawai.. "eyya sorry , " Tashi muje parlour na gaji da zama a bedroom, "OK.. Majid yace

parlour suka koma suka dasa sabuwar hira basu suka daina hira ba sai magrib.. dauro alwala sukayi tare da wuce wa masallaci

"Anuty.

"na'am... "dan Allah ki koyamin qarin dazu ban iya ba sosai, "to shikenan nima zaki koya min na boko ko. "eh zan koya maki mana Anuty. "To bari mu fara yin sallah

Tashi sukayi tare da dauro alwala suka gabatar da sallah  bayan sun idar fatuha ta qara

biyawa jidda karatun sannan jidda ta fara koyawa fatuha ABCD karku so ku ga... kwamatsala da kyar da kyar ta dan iya shima ba sosai ba amma tasa ma ranta sai ta iya ko dan ta rinqa jin abinda sangami ke cewa wani locaki

Bayan sun dawo masallaci majid ya fada two star "wash am tied...
Guntun tsaki sadiq yace "kai dai Ka bani daga zuwa masallaci har ka gaji sai ka ce ba namiji ba mtss.. fruit ya curo a fridge ya fara ci majid ya zuro hannu suna ci suna hira, "ni fa kaga wallahi na gaji da wannan gwaranci aura zan zo nayi wallahi..
smile sadiq yayi ya ce "aiya kamata kam,

"aikaima ya kamata kayi wani auran sadiq.. Duba da yau kusan shekara kausar 5 da rasuwa. sadiq ya kamata kayi aure haka ko saboda angel.. bata fuska sadiq yayi yace, "majid bana tunanin zanyi wani abu wai shi aure yanxu. tunda na rasa kausar na rasa wani bari na rayuwata. majid kafin a samu mata kamar kausar sai antona.. kausar tatara komai dana ke so agun mace. bana tunanin akwai wata ya'mace da zata iya maida gurbinta... ya ida zancan hawaye masu zafi na zubomai,
kallan tausayi majid ya mai da cewa. "sorry baby. na famama inda kema ciwo ko. girgiza kai yayi tare da goge hawayan shi da bayan hannu yayi smile yace .. "majid baka famamin komai ba. indai tunanin kausar ne ba yau na fara ba. yau kusan 5 year da ita nake kwana da ita nake tashi majid , murmusawa majid yayi tare da qoqarin canza topic dan a duniya ba abinda ya tsana irin damuwar sadiq haka shima sadiq ba abinda ya tsana irin damuwar majid , kallan ball suka shiga yi tare da yin musu dama sun sama ba yau suka fara ba damma yanzu sun girma ne. dada ne har kuka sai Sadiq ya sa majid cikin nishadi suke kallo

"Kinga zo muje mu ci abinci muyi sallah na maki wanka kafin baban ki ya biyo mu. washe baki jidda tayi parlour suka koma dining area suka wuce fatuha ta fara saving nasu tuwo shinkafa ce miyar taushe taji Alayahu da kaji cikin nutsuwa suke ci a plate daya...

bayan sun kammala fatuha ta kwashe kwanikan ta kai kitchen jidda kuma ta haura upstairs dan tayi missing daddy tun da ta dawo daga school bata qara ganin shi ba. bata iya jira har sai an mata wani wanka. a hankali ta murda handle din kofar a zaune ta gansu a parlour rugawa tayi jikin majid tana cewa. " small daddy I miss u.. smile majid yayi. "miss u angel how are u, "fine uncle , sadiq ne ya murmusa yace "ni fa yanzu fushi nake da angel tunda tayi new Anuty take mantawa da daddy. bata fuska tayi kamar zatayi kuka "uncle bafa haka bane new Anuty na da kirki kuma tana min wasa kuma kasan wani abu daddy sai ta zamo daga jikin majid taje ga Sadeeq tahau yimai rad'a akunne. jin abinda take gayamai yasashi yin wani killing smile...
{Wanda koni Salma ban san me jidda take cemai ba,}
"Na zo maki da ice cream amman tunda dadynki kawai kika fadamawa bana baki ice cream din.
Jin abinda majid yace shiyasata tsalle tana kuka sai ya bata ganin da gaske kukan ta ke sanyi na gaske shiyasa shimata ta bari se ze tafi ya dauko mata.. washe hakori tayi tace "thank u small daddy tare da yimai pack tanamaici gaba da cewa.. Aunty bata San na guduba dan

wanka zata min fa😀.. murmushi majid yayi ya ce "to diyar Anuty kice ina gaida Anuty.
kallan shi sadiq yayi a zuciyar shi yace da kasan wacece fatuha da ko hanya daya baza ka so ta hada ku ba balle kuma wata gaisuwa tabe baki yayi tare da jan tsaki ciki ciki

Tana fitowa daga kitchen ta fara neman jidda ba ita ba alamar ta upstairs ta haura saboda tasan bata wuce part din sadiq tana last stairs kenan sai ga jidda ta fito daga part din washe da baki murmushi fatuha tayi tace.. "shine baki jira na maki wanka ba sokike daddy yamin fada ne... girgiza kai jidda tayi fatuha ta dauke ta direct bathroom ta dire ta ta fara yi mata wanka sai da ta wanke ta tas sannan suka fito ta aje ta saman bed ta janyo lotion da night dress din jidda sai da ta shafe ta dashi. sannan ta zura mata kaya

"Big man bari na zo na wuce dare nayi.
"tun yanzu dare be wani yi ba na dauka fa kwana ka zo min wallahi kaga mun dade bamu hadu ba. murmushi majid yayi.. yace "next time zankwana.. "To shikenan.
har bakin mota ya raka shi ya Ciro ice cream din jidda ya bashi "gashi aba angel nasan Anuty ta maqale ta shiyasa bata fito ba ka shafa min kanta , "ok ka gaishe min da Umma da ammi "to zasu ji Alhaji da baba fa me suka tsarema da baza ka ce a gaishe su ba... dariya sadiq yayi tare da kai mai duka "wallahi majid ka rainani tunda na ce a gaida mutan gida ai suma sun shiga, harara majid ya bala mai ba "waninan ammi da Umma kawai ka ce kuma da yaushe ma ka girmeni har kake fadi na raina ka , harara sadiq ya qara wurga mai aidai na baka 4 hours ko qarya nayi. Ya qarashe tare da hade ran wasa. dariya majid ya fashe da ita tare da ba mota wuta.
Sai da safe ace ma mom na zo tana part din abba. "Toh sadiq yace mai da daga mai hannu har sai da motar shi ta fita sannan sadiq ya koma cikin gidan ,

dauke da jidda fatuha ta fito. Aiko nan take sukaci karo da sadiq a parlour...
B'allama fatuha harara yayi da kauda kai...
Itako tayi kamar bata gani ba. yana gaba suna bayan shi jidda na zuba surutu suna shiga part din a parlour fatuha ta aje jidda tana qoqari fita
"keee.. Yace da Ita.
Nan taja birki ta tsaye zuciyar ta na duka uku uku dan bata manta rashin kunyar da ta mai ba da safe ,"ba dake nake magana. ya fadi cikin daka tsawa. juyowa tayi tana zare ido , "kije kitchen ki hada min coffee ki kawo min.. zaro ido fatuha tayi waje um kwarankwatsi ban san me hakan ba. tsoki yaja mtss "yar kauyan banza toh burni nake nufi tea mara madara zaki hadu ki kawo min karki sa sugar a ciki.. ya ida zancan tare da balla mata harara abin ma dariya ya so ya ba fatuha wani lokaci sadiq in yana harara kamar qaramin yaro a zuciyar ta tace bema san idan yana fada wani qara kyau yakeba
ta dan ja tsaki ta fita.. saida ta gama hada mai ta kai mai yana zaune parlour yadda ta barshi jidda na saman cinyar shi da alama bacci ya dauke ta hannu ya miqa ze amshi coffee tana bashi ya saki cup din ya fadi gaba daya ruwan tea din ya zube mata a kafa wani irin ihu fatuha ta bude baki zatayi janyo ta yayi tare da to she mata baki yana kallan ta ido cikin ido idanuwanan tana sun ciko da kwalla hawaye daya nabin daya..

murmushi yayi komin banza ya sata kuka gashi matsar da yayi ma bakin bana wasa bane dan bakin sai radadi yake mata sai da tayi kuka san raita sannan ya sake ta tare da hankada ta ta fadi kasa sannan ya tashi ya kashe kayan kallo ya matso gaf da ita har tana jin saukar numfashinshi yace cikin cool voice na shi "wannan ka dan na maki akwai saura nan tafe.. ya ja saki tare da daukar jidda sai da ya kai bakin kofar bedroom ya juyo tare da yin killing smile din shi yacigaba da cewa. "kuma ki tabata kin gyara gurin kafin ki bar wajen.. Yana fad'in hakan ya shige bedroom ya barta tana matsar kwalla tare da jera mai Allah ya isa, kuma indai gyara gurine wallahi banyi mugu kawai sannan taja kafar ta wadda ta kone wajan har yayi ja bakin tama haka saboda ya ji matsar manya

Direct bedroom dinta ta wuce tare da rage kayan jikinta
bathroom ta shige tayi wanka ta fito daure da towel tana shafa mai tana jera wda cigaba da jera mishi Allah ya isan
A haka har ta gama shirin tafada saman bed se bacci

*Fan's kuyi hakuri da wannan page din yau bana jinyin typing din saboda ina wani dan aiki*

*taku har kullun mai qaunar ku Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&_yn_=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSAFULANI WRITERSFORUM.com

41_42

Kiran sallah asuba ne ya tada fatuha, arwala ta dauro tare da yin wanka bayan ta idar da sallah ta shafe jikin ta da mai kamar kullun tare da fesa turare uniform ta zure sannan ta daure gashin kanta Wanda da kyar ta kama shi, ganin be kamuwa yasa ta sake shi haka kawai ta fita direct part din sadiq ta shiga tana karema parlour din kallo ,har yanzu glass din jiya nan zube a parlour baki ta tabe ta shige bedroom sadiq na kwance jidda na maqale a jkin shi da alama daga masallaci ya dawo bacci ya kwashe shi dan jalabiya ce a jikin shi ba night dress ba sajan nan nashi yayi lufluf kwance, qare mai kallo fatuha tayi sannan ta bala mai harara kamar idanuwan shi biyu a hankali ta sa hannu ta fara janye jidda daga jikin shi janyo jidda ya qara yi ya maqale ta, abin ma dariya ya ba fatuha qara jan jidda tayi shima ya qara jan jidda haka suka riqa ja inja qara leqa fuskar shi tayi taga dai bacci yake a hankali ta qara miqa hannu zata janye jidda cikin dubara ta janye jidda direct bathroom ta dire ta, kamar kullun ta shirya jidda murmushi tayi washe da baki tace Anuty I like u murmushi fatuha tayi tare da langwabe kai ta shafa kan jidda tare da cewa jidda kisan ban iya wannan yaran ba, murmushi jidda tayi ina nufi kina birge ni Anuty murmushi fatuha tayi wadda ya baya kyawawan hakuran ta tace nima haka Jidda pack jidda tayi mata itama fatuha pack tama jidda.

Janyo hannun jidda tayi cikin ni shadi suka qaraso dining area tea ta shiga hada ma jidda mai kauri, Wanda yaji ovaltine da madara tare bread n egg a hankali ta Shiga feeding din jidda tana amsa itama in taji dadi se ta gutsuro bread din taba fatuha, mom da abba ne suka qaraso cikin fara'a dining area cikin ladabi fatuha ta gaishe su ,cikin farinciki suka hada masu breakfast, washe da baki mom ta amsa jidda ce ta washe baki tare da cewa morning grandma n grandpa morning too angel suka amsa a tare bayan jidda ta gama hada masu ta aje masu cikin ni shadi suke breakfast.

Tsaye yake gaban dress mirror sanye da bathrobe hannu shi riqe da qaramin towel yana goge sumar kanshi da alama daga wanka ya fitu cikin tsuwa ya yake shirin lotion ya shafa tare da saka uniform din shi sannan ya feshe jikin da turaruka masu kamshi booth din shi ya curo ya saka black se sheqi yake tsaf ya fito sojan shi hula shi ya dauko ya sa sai agogwan shi silver na zurfa wani irin kyau yayi ba dan kadan ba sai dai fuskar nan daure briefcase din shi ya dauko tare da daukar wayar shi da ke bedside drowe a hankali ya bude kofar bedroom kallo daya yayi ma parlour tare da jan dogwan tsaki fatuha kin rainani wallahi sannan yasa qafa ya fitu daga part din a hankali yake saukowa daga upstairs tuni kamshi turaran shi ya mamaye parlour fatuha da ke feeding din jidda ta dago idanuwan tana qaremai kallo cikin isa ya qaraso wayar shi ya cure ya kara a kunne cikin natsuwa yake wayar , holle ole daga bangaran ola yace hello boss, ka zo ka amshi briefcase din , to ya ce mai tare da kashe wayar ya qaraso dinning area smile yayi tare da gaishe da su mom jidda washe da baki ta gaishe haka fatuha banza yayi da

ita kamar be ji tare da qare mata kallo yau kuma wani saban iskanci yima mutane yawo a gida ba dankwalli duk yana yin maganar a cikin zuciyar shi a hankali ta janyo cup da niyar hada mai breakfast hannu ta ya rike ya wurga mata wani irin kallo ya aje hannu tare janye cup din mom ce ta aika mai harara sai yayi kamar be gani ya cigaba da aikin da ya ke ole ne ya shigo cikin sallama suka amsa sannan ya amshe briefcase din sadiq ya fice da ita abba ne ya katse shurun da cewa, ah ka ce min qafa ta warke murmushi sadiq yayi tare da cewa eh abba toh masha Allah , abba ya maganar kwangilar kunko samu a'a munan dai muna fama amma insha Allah this time around zamu samu abinda muke so murmushi sadiq yayi tare da cewa Allah yasa mom ta amsa da ameen tashi yayi tsaye tare da cewa oya angel mu fati , ah baby karka ce min ruwa tea din har ya isheka ba bread ba komai eh mom na koshi toh shikenan, hannu jidda ya kama har sun kai baki ko abba yace yawa baby ina san fadama ranar Sunday tare da mom din ku zamu tafi uk , OK sadiq ya ce tare da sa kai ya fita fatuha na biye da su da lunch box din jidda har gaban mota sannan ta miqa wa jidda lunch box din tare yi mata pack sadiq kallan su yayi tare da tabe baki sannan ya shige mota.

A hankali ta juyo ta shige gida, kwashe kayan breakfast din tayi mom na zaune a parlour tana kallo fatuha ta zo ta wuce kitchen washe da baki ta gaida baba jinmai itama baba jinmai washe da baki ta amsa ,rabi'a na gefe tana gyara kayan miya tayata fatuha ta Shiga yi suka gyara tare sosai ta taya su baba jinmai aiki a kitchen saboda aiki na burge ta kusan tare da ita aka dafa lunch baba jinmai ko dadi take ji har qosawa take suje kauye jauro yaga yadda fatuha ta koma kamar balarabiya, bayan sun gama aikin fatuha ta wanke duk wani kwano da akayi anfani da shi rabi'a ko sai hanata take amma taqi bari sai da suka gama komai sannan fatuha ta dawo parlour, ko da ta dawo mom ta bar parlour bedroom ta shige tare da rage kayan jikin ta bathroom ta shige ta watsa ruwa daure da tawel tafito bayan ta gama komai sannan ta tuna ashe bata gyara part din sangamin ba, ko mai bata shafa ba ta zura kayan ta direct part din sadiq taje ta fara gyara sai da ta gyara shi tas sannan ta zauna a parlour saman three star tana maida numfashi lumshe idanunta tayi tare da ware su, fita tayi daga part din ta koma bedroom ta kuma watsa ruwa sannan ta shefe jikita da mai tare da fesa turare da maida uniform din ta.

Misalin karfe 2:00pm su jidda suka dawo ,kasan cewa yau sadiq be da wani aiki tare suka dawo part din shi ya nufa masha Allah gyaran part din ya mai yana jin dadi ganin part din shi a gyare, duk rashin jin fatuha tasan aikin ta shiyasa wata rana yake daga mata kafa bathroom ya shige ya watsa ruwa ya fito cikin wando da riga ya shirya, kayan sun mai kyau sosai. bangaran su fatuha kuwa jidda na dawowa yadda ta saba yi mata haka ta mata sannan tace taje parlour ko da ta fito parlour daddyn ta gani jikin shi ta fada tana zuba mai surutu shikuma yana saurareta yana jin dadi, mom da abba ne ke saukowa daga upstairs abba sanye da shada malinmalin brown mom na sanye da atanfa pink mai ratsin greed n bleu sanye da mayafinta ba qaramin kyau sukayi ba, parlour suka qaraso washe da baki jidda ta sauka daga jikin sadiq ta riqe hannun grandpa murmushi abba yayi yace "Sadiq yau da wuri ka d'awo daga wajen aiki kenan?" smile yayi tare da cewa eh to mu zamu wuce gidan ammi mu masu sallama to Allah ya

tsare ameen jidda ce tace grandpa zan biku toh shikenan yima fatuha magana inji mom sai muje tare ko, rugawa tayi bedroom fatuha kuwa tunda jidda ta fita wani irin bacci ne ya sure ta ko da jidda ta shigo taga fatuha na bacci veil din ta ta dauka tare da fita ,grandma Anuty bacci ta take toh shikenan tunda bacci take mu tafi kawai ta samu hutu ne washe da baki jidda ta bi su abba, sadiq ya rako su har parking space sannan ya koma gida ko da ya koma wani irin killing smile yayi upstairs ya haura sannan ya fito kitchen ya shiga ya dauko ruwa a fridge me sanyi Wanda har qanqara ya fara saboda tsabar sanyi a hankali ya murda handle din dakin fatuha ya shiga hangota yayi saman bed tana sharar bacci gashin ta ya baje saman gadon, cije lips yayi sannan ya qaraso sai da yazo dai dai face din ta ya bude murfin rubar ruwan ya juye mata shi, fatuha da ke bacci wani irin razana tayi ta tashi cikin gigice wa ta yunkura zata fita saboda tsoro, sadiq ya janyo gashin ta tare da dauke ta da lafiyeyan mari ,wani irin kuka fatuha ta saki tare da zama saman bed jajayan eye's din ta ta dago tana kalla sadiq wani irin murmushi yayi yace "Fatuha yau zan koya maki hankali, bani kika so ki nakasa ba ? toni yau kona maki gashi zanyi ya ida zancan tare ya matse mata fuskarta, idanuwan fatuha sunyi jawur sai kuka take tana bama sadiq hakuri ashana ya Ciro a aljihun shi ya kunna tare da fusgo gashin ta wani irin kuka fatuha tasa dan Allah me kyau kayi hakuri wallahi bazan sake ba ta ida zancan tana qara rushewa da saban kuka, shhhh yimin shiru fitsarariyar banza nufo gashin ta yayi da wutar take fatuha ta fashe da wani sabon kukan tare da tafiya luuuu ta sume, murmushi sadiq yayi ganin suma tayi marar kunyar qarya kitchen ya koma ya dauko wani saban ruwan sanyi ya dawo bedroom ya qara juye mata shi wata irin ajiyar zuciya ta saki tare da fashe wa da kuka tana bama sadiq hakuri, cije lips yayi na qare mata kallo yarin ya ce sosai amma sai rashin kunya duk à zuci yake wanga zancan , bindiga ya ciro ya daura mata akai tuni fatuha ta saki fitsari ta sauke numfashi agwagwame cikin sarkewar murya tace dan Allah me kyau kayi hakuri bazan sake ba, tsaki yaja tare da cewa fitsari ma kikayi ko? a'a wallahi ruwa ne haka wallahi, murmushi yayi dan yasan qarya take sannan yace daga yau se yau kika qara min rashin kunya sai na b'ula maki kai da wannan abar , girgiza kai tayi alamar baza ta sake ba, sannan ya hankada ta kanta ya bigi gado ta qara sakin wani saban kukan sannan sadiq ya sa kai ya fita.

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

★we are the best★

http//mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_dial_&_yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.com

43_45

Sai da fatuha ta ci kuka sosai tare da jerawa sadiq Allah ya isa, sannan ta tashi jiki ba qwari ta nade zanin bed din Allah ya taimake ta katifar akwai leda dan haka ruwan da fitsarin be shige cikin katifar ba iya karshi saman bedsheet tatare shi tayi ta aje ta shiga toilet ta watsa ruwa, tana gamawa ta fito ta dauki bedsheet din ta wanke shi tas sannan ta fito da bokitin ta aje agefe sai da ta shirya tsaf sannan ta dau bokitin ta fita ko da tafi dasu ola taci karo da Sunday yaran sadiq suna ta shawagi a tsakar farfajiyar gidan, kai tsaye wajan shanya ta nufa ta shayan bedsheet din sannan ta dawo ta zauna saman wata resting chair da ke a farfajiyar gidan lumshe ido tayi tana jin wani tsoro sadiq na ratsa ta, wasu hawaye masu zafi na zubo mata, dan yau ba qaramar wahala tasha a hannun shi ba take nan wani zazabi mai zafi ya lulube ta sakamakon ruwan sanyin da sadiq ya sheqa mata, ganin masasarar taci qarfin ta yasa ta ja jiki ta koma parlour saman three star ta zauna ta qudindine waje daya tana kyarma abin gwanin ban tausayi😰.

Bangaran sadiq ko zuciyar shi fes bathroom ma ya shige ya sheqa wanka bai jima sosai ya fito daure da tawel da Dan karami yana sane gashin kansa, gaban dress mirror ya tsaya yana gyara kanshi da ya tuno da yanda fatuha tayi se ya saki murmushi jin dadi bayan ya gama shiryawa cikin 3quarte da armless t-shirt din shi cikin shirin shi na zuwa gym , sannan ya feshe jikin da turare masu sanyi kamshi a hankali ya bude handle din kofar tare da barin part din cikin isa yake sakowa daga upstairs fatuha ya hango saman three star qudindine kauda kansa yayi yana qoqarin fita har yayi gaba sai kuma ya dawo saboda barin da yaga jikinta nayi yasa yaji tausayinta kadan azuciyarsa, a hankali ya qaraso gaban three star din ya leqa fuskar ta Wanda tayi jawur ga shatin hannu shi kwace a fuskar ta lumshe ido yayi tare da waresu a kanta a hankali ya kai hannu ya taba goshin ta ji yayi goshi zafi rau kamar wuta, a hankali fatuha ta ware idanuwan ta ta fara rera mai kuka a tunanin ta wani muguntar ya zo yi mata, daurewa yayi tare da cewa yima muta ne shuru kafi na kife ki da wani sabon Marin tsuru tsuru tayi tana kallan shi ga wani irin zazabi da take ji ,lumshe ido tayi ta juya mai baya wayar shi ya ciro dake

aljihunshi bugu daya biyu Dr yakub ya dauka sannan ya sheda mai yana buqatar ganin shi , OK ya ce mai tare qatse wayar sannan ya kalli inda fatuha take kwance hata gashin kanta jiqe yake a hankali ya kai hannu ya dauki fatuha ita ko sai matsar kwalla take tana bashi hakuri banza yayi da ita be dire ta ko ina sai bedroom din ta, saman bed ya direta sannan ya dau ko hand dryer daya ke anfani da ita ya busar mata da kan ta fatuha ko sai bin shi take da ido AC din ya rage ma gudu tare da rufe ta da blanket ya koma gefe ya zauna fatuha ko lumshe indo tayi kamar me bacci.

Ba'a fi 50 minutes ba sai ga Dr yakub sadiq ne ya mai iso har bedroom dinta, dudubata yayi sannan ya fito da alura da magunguna ya aje a gefe sai da ya gama zuko alura sannan yayi ma fatuha magana, hajiya ki juya zan maki alura ko dan fever ta sauka ,waro ido fatuha tayi ta fara kuka dan Allah kayi hakuri wallahi bana san alura kuka take sosai sadiq ta shiga ba hakuri, banza yayi da ita kamar bai jinta, ohni fatuha yau na shiga 3 ban taba tunanin muguntar me kyau ta kai haka ba duk wannan zancan tana yin shine a zuciyar ta ,Dr ne ya katse shurun da cewa please ki tsaya na maki alura kin ji ba zafi ba kuma ko dan ki samu sauki masasarar da kike yi kinji ,Dr ya ida zancan yana smile wallahi bana san alura dan Allah kayi hakuri ka kyale ni Dr yakub ne ya juyo ya kalli sadiq dake ta latsa wayar shi kamar ba mutun a wajan ka ji mara lafiyar ka bata san alura kuma irin wannan fever se da alura yake sauka ,dago sexy eye's ball's din shi yayi yana qarewa bed din kallo da fatuha take kwance saman bed din cikin isa ya qaraso yace fatuha shuri tayi kamar bata ji shi sarai yasan tana jinshi ,wani saban rainin ne haka ji yayi dama be kira Dr din ba ya barta ciwo ya kashe ta inya tashi daf da ita ya zo ya zauna tare janyo ta kuka tasa tana cewa ni ka kyale ni bana so banza yayi da ita ya riqe ta gam Dr ya zunkuda mata alura wani irin kuka ta saki tare da rungume sadiq gam tana kuka se da tayi kuka san ran ta sannan ta fara sauke a jiyar zuciya dan guntun tsaki sadiq ya ja tare da zame ta daga jikin shi fatuha ko yana zame ta ta koma ta kwanta saman bed tana sauke ajiyar zuciya, sannu Dr yakub ya mata sannan ya dau briefcase din shi tare da yima sadiq bayanin yadda zata sha maganin Godiya ya mashi sannan ya rako shi har bakin kofa yashiga motarsa ya tafi. shi kuma ya koma bedroom din fatuha ja mata blanket din yayi sannan ya fita ita kuma bacci ya sure ta.

Bangaran su mom ko sun isa family house lafiya,d irect part din ammi suka fara shiga cikin fara'a ta tarbe su da jin dadi asiya mai aiki ta kira ta kawo masu fura mai sanyi da kayan motsa baki, aiko sakin jiki sukayi suka sha dan ammi ba irin iyayan mijin nan ba ce me takurawa surukanta daukar su take kamar ya'ya ta Jidda ta janyo tana mata wasa ,yan'mata baba ina baban naki kwana biyu shuru murmushi jidda tayi tace "Daddy nanan lafiya lau "to madala kwana ki nake ji majid na cewa sadiq be ji dadi ba mom ce ta ce wallahi ko faduwa yayi a toilet Allah sarki ai abun ya zo da sauki, masha Allah ai yanzu ya warware sosai da tare zamu zo ma Eyya sun sha hira sosai da ammi daga nan suka wuce part din Umma lokaci baba be dade da dawowa daga kasuwa ba, baba jan abba yayi suka shige part nashi suka dasa sabuwar hira abin ka da yan'uwa haka Umma da mom suka bude saban shafi na hira basma ce ta fito sanye da gown ta zo har parlour ta gaida mom ,tare da kawo masu kayan motsa baki sannan ta ja jidda bedroom din tana mata wasa tare da tanbayar ina daddy washe da baki jidda tace yanan

lafiya lau ok good ,idan kun koma gida ki ce mai anuty basma na gaisheshi to jidda tace mata, chocolate ta dauko a bedside drowe taba jidda sannan ta cigaba da assignment din ta da datake yi sun dade sosai dan kusan a can su kayi dinner sai kusan 9:00pm sannan suka fito, se da abba ya qara leqawa part din ammi ya gaishe da alhaji sannan suka fito har bakin mota Umma da baba da basma suka rako su sannan suka juya cikin gida.

Fatuha kuwa sadiq na lulube ta bacci ya kwashe ta ,ba ita ta tashi ba sai da ake Kiran sallar isha'i ko da ta tashi zazabin ya sauka sai dai jikin ta ba qwari, a hankali ta yaye blanket din jikinta ta shige toilet arwala ta dauro bayan ta gabatar da sallah ta koma saman bed ta kwanta, sadiq bashi ya fito daga gym ba sai magrib wanka yayi ya tafi masallaci bashi ya dawo ba sai bayan sallah isha'i ko da ya shigo gida yaji ba motsin kowa hakan tabatar mai da su mom basu dawo ba, bedroom din fatuha ya leqa kwance ya hango ta jin shigowar shi yasa fatuha qara yin lamo haskyan dakin ya kunna tuni dakin ya gwaraye da haske ,a hankali ya qaraso ya leqa fuskar ta tare da cewa fatuha banza tayi kamar me bacci tsaki ya ja yace "Nasan kina jina ko? ki tashi ki sha magani kona qarasa ki da bindiga, tunda dai mutuwar kike so" tuni fatuha ta tashi zaune tana zarar ido maganin ya shiga bale mata ya bata sai da ta sha sannan ya miqa mata fresh milk tace ta koshi wani irin kallo ya wurga mata ba arziqi ta kafa kai ta sanye, sannan ya fita daga daki yana fita ta ce ah ashe su sangami ana da kirki har da hada ni da madara mai dadi sannan ta ja dan guntun tsaki ta koma ta kwanta.

Bayan ya fito daga dakin fatuha parlour ya dawo ya zauna tare da lumshe idanuwan shi kamar me bacci cikin sallama su mom suka shigo wani irin smile yayi tare da tashi zaune, ya qaraso wajan su jidda ce ta rungume shi tana cewa daddy I miss u miss u more angel kin tafi kin bar daddy shi ka dai a gida, turo baki tayi tace "Daddy Anuty nan bata taya Kuyi hira ko? ta ida zancan ta bata fuska" eyya angel Anuty ba lafiya fever take, mom da zaman ta kenan saman three star tace me ya sameta sadiq yace mom fever take dazu na ganta a parlour zaune tana rawar sanyi shine na kira mata Dr yakub ,good baby ka kyauta bari na dubata abba da ke haurawa upstairs ya ce kice ina mata sannu to mom ta ce tare da shiga ita da jidda, ko da suka shiga a lokacin fatuha tayi bacci cikin tausayawa Mmy take kallanta domin sakanita d Allah take son yarinyar d'aga karshe tayi mata Adu'a suka bar dakin.

yau ko sadiq shi da kanshi ya shirya jidda, sannan su kayi bacci jidda ko sai missing din Anuty fatuha take sadiq ko dadi ya ji komin banza ta saitu.

*taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&_yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REAlHAUSAFULANIWRITERSFORUM.com

45_46

*Yan uwa kuyi hakuri jiya nayi mstk maimakon nasa 43_44 sai nasa 43_45 ina fatan zaku min uzuri yauw zamu tashi d'aga 45_46 ina fatan kungane ni Salma ina Al'fahari d'aku Nagode sosai yanda k'uke son wanga littafin nawa Allah Ubangigi yabarmu taré Ameen....wanga pag din sadaukarwane gaduk mai bin labarin I love you ol my fan's😍😍🤸*

Misalin karfe 6:00am na safe fatuha ta tashi Alhamdulillah jikin nata da sauki, à hankali ta sauko d'aga gadon ta shiga toilettes wanka tayi tare da yin arwala ,tana fitowa tasa doguwar Riga ta shimfida daduma domin gabatar da sallah ,kasan cewar yau juma'a tana gamawa ta cire rigar ta saka wata Riga da wando mai mai ruwan zumuwa Rigar ya tsaya mata har gwuwa ba qaramin kyau kayan suka mata sai suka fido da ship din ta sosai veil din kayan ta dauko se yar hoda data Murza se lipstick ta sama lips din ta , tayi kyau masha Allah direct part din sadiq ta wuce a dai dai bakin kofar ta ci birki ta zaro idanuwan ta har ga Allah yanzu Sadiq ya fara bata tsoro daure, fuska tayi à hankali ta murda handle din kofar, parlour ba kowa sai sanyi AC da ke tashi da kamshi a hankali ta qarasa kofar bedroom ta murda a hankali sadiq ta hango gaban dress mirror, sanye da bathrobe yana goge gashin kan shi cikin sallama ta qaraso bedroom din ciki ciki ya amsa kamar me koyan magana jidda dake zaune saman bed itama sanye da bathrobe da alamar da ya gama gyara kanshi ze gyarata washe da baki jidda tace Anuty tare da rugawa a rungume ta bata fuska tayi tace "Anuty ashe baki lafiya shine baki fada min ba? ta

ida zancan tana bata fuska" murmushi fatuha tayi tace "Ai yanzu na warke sauki ranki Jidda ta" toh shikenan Anuty sadiq ko harkar gaban shi yake fatuha kuwa sai binshi take da ido a sace ohni mutun sai shegen kinibibi kamar mace dan gutun tsaki fatuha ta ja tare da daukar jidda suka fita.

Bedroom ta dire jidda ta shirya ta cikin uniform din ta, sannan ta raba mata gashin ta gida biyu taja hannun ta suka wuce dining area ,mom da abba na zaune a dining area cikin natsuwa ta qaraso ita da jidda ta gaishe su mom cikin ladabi a tare suka amsa tare da yimata ya jikin, washe da baki tace da sauki jidda ta jama kujera ta zauna sannan ta fara saving nata tana cikin saving nata sadiq ya qaraso dining area gaishe da su mom yayi tare da yi masu pack sannan ya samu kujera ya zauna masha Allah ya sha kyau har ya gaji, kallo daya fatuha ta masa ta kauda kai cikin tsanar sa Amma duk da haka sai da ta yaba kyau irin na sadiq har mamaki take anya akwai wanda ya fishi kyau kuwa musanman yau da yake sanye da manyan kaya, tunda ta zo gidan yau ce rana ta farko data fara ganin me kyau da manyan kaya shada ce sky blue yasa tasha dinki da dark blue zare anmai irin dinkinnan na sarauta se hula blue mai ratsin dark blue , hannu ya kai ya dau cup ya fara hada tea dan shi mutun ne ba mai san yawan cin abinci , bayan ya gama hada tea ya fara sha a hankali mom ce ta kalle shi tare da cewa baby karka ce min yau ma tea kadai zaka sha lagwabe kai yayi yace eh, haba baby wai me yasa baka san cin abinci ne eh abba da ke gefe yace "Sai kace ba soja ba sojoji da aka sani da cin abinci , shagwabe fuska yayi ya cigaba da shan tea din ganin mom nata magana yasa shi cin chips din kadan fatuha sai da tabatar jidda taci ta koshi sannan ta kyale ta bayan sun kamala cin abincin sadiq ya dau jidda fatuha na biye da su da lunch box har bakin mota , sannan jidda ta mata pack ta shige mota juyowa tayi ta shigo gida da abba ta ci karo mom ta rako shi riqe da briefcase din shi wuce su tayi ta koma dining area chips ta Zumaba da farfesun kifi bata wani ci da yawa ba saboda har yau bakin ta ba dadi bayan ta kamala ta fara kokarin kwashe kwanikan ,mom ce shigo washe da baki tace "Haba fatuha ke da baki da lafiya ina ke ina aiki ki ?zauna ki hutu" washe baki fatuha tayi tana qoqarin yin magana mom ta hanata kwalawa rabi'a kira tayi cikin ladabi rabi'a ta qaraso tayi ta d'urkusa har kasa ta gaishe da mom , yawa rabi'a kwanikanan zaki kwashe sannan yau ki je ki gyara part din sadiq saboda fatuha bata jin dadi har cikin zuciyar rabi'a bata so mom ta ce ta gyara part din sadiq ba saboda basa wani shan inuwa daya jiki ba qwari ta kwashe kayan dining area din fatuha kuwa daki ta koma tasha magani bata wani dadi ba bacci ya kwasheta.

A cikin school yayi parking din motar shi tare da zagayowa ya budewa jidda murfin mota ,ta fito lunch box din ya miqa mata tare da yi mata pack ,daddy am going to miss u , I now angel karki damu anjima in an tashi ni zanzo daukar ki kin ji angel murmushi tayi tare da yi mai pack ta shige class yana kallan ta har ta shige ,shi kuma ya wuce wajan aiki taré da kaunar diyar tashi.

Ba ita ta tashi daga bacci sai karfe 11:30pm ita kanta tayi mamaki baccin da tasha, toilet ta shiga tayi wanka ta fito tare da shafe jikin ta da lotion wardrobe ta bude ta ciro atamfa brown

me ratsin black n white atamfar  ta hadu riga da skirt dinkin  ya mata kyau qarewa kanta kallo tayi ta cikin dressing mirror  murmushi ta saki tare da cewa gaskiya birni tayi dubin yanda na koma kamar ba fatuha inna ba duk wannan zancan tana yinshi ne a zuciyarta, murmushi takara yi tana qoqarin kama gashin kanta bude kofar da akayi ne yasa ta saurin waigowa a tunanin ta Jidda ce sai taga hanan washe baki tayi tare da cewa "Hanan cikin fara'a" hanan ta qaraso dakin sanye take da lace sky green mai ratsin black se veil din ta white ba qaramin kyau tayi ba ta fito yan'matan sak, zama tayi saman bed tare da cire veil din wash na gaji wallahi dariya fatuha tayi wai kin gaji, aiki me kikayi da kika gaji? murmushi hanan tayi tare da cewa "Kai fatuha karki ce min wannan uban gashin naki ne?" fari da ido fatuha tayi tace na hanan ne bugu hanan ta kai mata cikin wasa kai Amma fa kin ji dadi murmushi fatuha tayi tace "Ina Jamal da afra?" suna parlour tare da grandma nima tanbayar ki nayi sai grandma ke ce min baki ji dadi ba shine fa na shigo na maki sannu toh ashe har kin warke kin fara make up ta ida zancan cikin tsokana, dariya fatuha tayi ta ce "Wallahi naji sauki danma mom bata barni nayi aiki ba"  ai ta kyauta wallahi amma yau baki je school ba eh exam muke na JSCE shiyasa ban je ba yau bani da paper Jamal kuma fever yake shiyasa, murmushi fatuha tayi ni wallahi ina san makarantar nan se ma na shirya jidda zata tafi sai naji kamar na bita, ai karutu akwai dadi akwai wahala kiyi ma mom magana mana smile fatuha tayi tare da cewa toh jidda ce ta shigo bedroom din ta fada jikin fatuha murmushi tayi tace "Yan makaranta har andawo kenan?" daga  mata kai jidda tayi ta eh Anuty kin ga daddy ya siyo min ice cream da zamu dawo har da chocolate da yawa  kuma fa naba daddy naki ya aje mana murmushi fatuha tayi ta ce toh ,a zuciyar ta kuwa cewa tayi tap wannan daddy naki ai sai ke hanan ce ta katse mata tunanin da cewa bari naje wajan uncle nima na amshi nawa tana fadin tana qoqarin daukar veil din ta zata fita , fatuha inkin gama shirya jidda ki same ni a parlour muyi lunch toh tace mata to bawai dan tasan me hanan ke nufi da kalmarta na qarshe ba daukar jidda tayi ta shige da ita bathroom ta wanke ta tas sannan suka fito ta shafeta da mai tare da Samata gwon pink me qaramin hannu se gashinta da ta gyara mata tayi kyau sosai masha Allah.

Direct parlour suka fito Anuty bilki na saman two star zaune, mom na  zaune saman three star suna kallo gaishe su tayi mom tayi mata ya jiki ita da Anuty bilki da gudu jidda ta koma wajan Jamal da ke zaune saman daya daga cikin kujerin dining area itama ta zauna cikin fara'a fatuha ta qaraso ta fara saving din su , hanan dake saukowa daga upstairs tana zunburo baki gaba cikin bacin rai ta qaraso dining area din fatuha  ta kalle ta tace, "Lafiya naga kamar an bata maki rai ?"dan guntun tsaki taja wallahi uncle ne ya bata min rai shi kullun cikin bakin rai maganar arziqi ba taba hada ku dashi, murmushi fatuha tayi tace "Yi hakuri kinji zauna mu ci abincin mu in mungama mu fita farfajiya shan iska" yawa tawa abinci suka  ci cikin nishadi bayan sun gama fatuha da hanan suka kwashe  kwanikan sunka kai kitchen sannan suka fita farfashi jiyar gidan domin shan iska.

Saman resting chair suka zauna ,suna dan taba hira fatuha ba qaramin jin dadi gurin take ba saboda har da yan shuke shuke lumshe ido tayi ta ware su, kai fatuha karki ce min wai bacci kike ji ah ba bacci nake jiba kawai wajan yamin ne ina san guri kamar haka, shiyasa sanda nake akauye kullun muna bakin rafi ni da fatsima murmushi hanan tayi sun dade sosai a filin

gida suna hira kiran sallah magrib ne ya tashe su a wajan suna tafe suna hira ,sadiq da ke qaqorin fitowa zai je masallaci sanye da jalabiya milk fatuha bata lura ba ta fada mai dan ita bata gani tana rike da hanan wata iri tsawa sadiq ya daka mata Wanda yasa yan hajin ta katsawa hanan ko take ta kama gefe jikin fatuha ta rabe, harara ya aika masu su duka stupid girl's kuna tafiya kuna kalle kalle baku kallan gaban ku mtss sannan ya sa kai ya fita. sauke ajiyar zuciya hanan tayi ta ce ba dai jaraba ba mtss sannu indai uncle ne haka yake kullun cikin bakin rai da hargowa, murmushi fatuha tayi tace ni zan fada maki haka sannan suka shige cikin gida.

*Fan's kuyi hakuri da wannan page din am to busy shiyasa nayi shi ba yawa*

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http//mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.comBayan su idar da sallah parlour suka dawo suna kallo , kitchen fatuha ta shiga anan ta iske baba jinmai tana farfesun yan'ciki gaishe ta tayi cikin sakin fuska ta amsa mata tare da yimata ya jiki ,da sauki ta bata amsa tana qoqarin bude fridge fruits ta debo ta zuba a ball na glass tare da wankewa sanna ta dauko wuka parlour ta koma hanan da ke zaune saman one star ta duro qasan carpet tare amshe wuqar,t ace "Bari ni na yanka fruit din? kinga ke bakida lafiya" harara fatuha ta aika mata waya ce maki bani lafiya? lafiya ta lau inda za'a auna mu qilama na fiki lafiya dariya hanan tayi ta ce "Wasa kenan" tare da cigaba da yanka fruit din sai da ta gama yanka fruits din sannan ta maida wuqar ta dawo parlour suka fara cikin fruit din cikin jin dadi suna kallo suna taba hira.

Anuty bilki ce zaune saman sofa mom na saman bed zaune, mom yanzu sai yaushe zaku dawo? wallahi ban sani ba amma nasan sai mun kai 2week tunda shi wancan zuwan da yayi se

da yayi kusan 3week, shagwabe fuska Anuty bilki tayi amma fa gaskiya mom zamuyi missing naki wallahi, murmushi mom tayi tare da cewa ah kanku bazan zauna ba naqi bin tsohon mijina ba akan Wanne dalili zan barshi kullun yana zuwa uk ni ina Nigeria ni mai ya'ya, ya'yan da suna gidan miji, dariya Anuty bilki tayi kai Mom harar ta wurga mata kinga in ta kuramin zakiya tashi ki ban gu kona samu na cigaba da hada shirgi na, ah Mom wato kaya zaki kwasa da yawa kenan? laaaa yau Allah ya kawo mu ya' na tirtse uwar ta Dan zatayi tafiya da uban ta , toh kaya zan diba da yawa kika bata min rai wallahi har wata sai muyi ta ida zancan tana bude bedside drowe baqar leda ta curo ,yauwa ga wannan tun wancan satin na so na aiko baby ya kawo maki, to ban samu dama ba washe baki Anuty bilki tayi kai Amma fa mom naji dadi Allah yasa wannan maganin irin wancan ne gaskiya wancan naji dadin shi murmushi Mom tayi tace "Ai ina tunanin wannan yafi wancan, dan wannan dan sudan ne" amma fa na gode Mom kamar kinsan gobe zai dawo toh ai shikenan daya garin da madara ake sha duk dare shi kuma dayan da zuma ga turaruka nan masu kamshi in kina anfani da su ko cup kika riqe sai yayi kamshi, washe baki Anuty bilki tayi mom thanks kamar kin san abban hanan nasan kamshi sosai wallahi , ah daughter waye baya san kamshi ?sai dai in Mutum bai samu ba kamshi na da muhinmanci sosai daughter ko kamshi kika riqe to wallahi kin riqe mijinki à wannunki, haka Anuty bilki ta riqa jerawa mom godiya agogo ta kalla kusan 8:30pm Mom bari muzo mu lalaba mu tafi gida dare ya fara yi, bada'n gobe abban hanan zai dawo ba da mun kwana wallahi, ai ko ba bazai d'awo gobe ba ban zan bari ki kwanar min gida ba, ke kullun kika zo yini sai ki bige da kwana ?ai hakuri ake a zauna har miji ya dawo ya same ka ba wai ka kwaso kafa kazo gida ba, mayafinta ta janyo da handbag dinta ta tura bakar ledar ciki fitowa sukayi daga bedroom din Anuty bilki na gaba mom na bayan ta suka sauko daga upstairs sai da ta iso parlour ta yafa mayafin ta ,su hanan da ke zaune parlour suna shan fruit Anuty bilki ta qaraso hanan ku tashi mu tafi dare nayi ,bata fuska hanan tayi tace "Momi na fa dauka sai 9:00pm zamu tafi "ai kin san bana san driven din dare ko ?kuma ba da driver nazo ba hanan bata so su tafi yanzu ba da ba exam suke ba da nan zata kwana fatuha ma haka bata ji dadi ba saboda in hanan ta zo tana dibe mata kewa Anuty bilki ce ta katse masu tunani da cewa "Hanan yima baba jinmai magana zamu tafi ta baki afra "bata ida rufe bakin ta ba sai ga baba jinmai riqe da hijabin ta a hannu afra na goye a bayan ta washe da baki tace ah kuma har kun fito yanzu na ke cewa bari na kawo maki Afra yau nama yi daran tafiya da yake na tsaya yima mai gida farfesu, mom ce ta ce ku dai baku ji baby ya sata farfesu ke kuma kin miqa mata diya tana ta fama ga afra da shegen kuka ,ba komai ai kuma ko kukan ba tayi ba Allah ya taimake ki shi kuma baby bayan yasan baki wuce magrib shine zai daura maki wahala, murmushi baba jinmai tayi tana qoqarin miqawa hanan afra ,dariya Anuty bilki tayi tace mom da kin bar shiga tsakanin baba jinmai da baby ko ka shiga kai zaka sha kunya murmushi mom tayi ,to ai sai mu wuce tare sai na sauke ki gida baba toh shikenan tare suka fito fatuha na kusa da hanan sunata zuba surutu jidda na riqe da hannu Jamal duk suka rako su filin gida , Anuty bilki na qoqarin bude murfin mota sadiq ya shigo tsayawa tayi tana sakin Murmushi qarasowa yayi yace "Sister har zaki tafi ?na dauka kwana zakiyi ai ya fadi cikin zolaya, harara ta maka mai baby ka rainani wallahi dariya yayi baba har dake zasu tafi da niyata na kai ki, ah ba komai Hanan dake kusa da fatuha sai turo baki take sadiq ne ya kalle ta tare da aika mata harara sister na kusa fara cima hanan naga kwanan wani rashin ji ke damun ta, ni ba ruwana wannan tsakanin ku ne, toh shikenan raurau da ido hanan tayi tare da cewa uncle sorry harara ya kuma aika mata ganin be da niyar hakura yasa ta tabe

baki ta shige mota tana yima fatuha bye bye su duka suka shige motar Anuty bilki tace "In anyi hutu this time around jidda a gida zatazo" toh ya ce mata ai sun kusa fara exam I think this Monday zasu fara eh Anuty bilki tace mai tare da ja su suka bar harabar gidan sannan su fatuha suka jiyo riqe take da hannu jidda.

Direct bedroom suka wuce sadiq kuma ya wuce dining area , ko da suka shiga bedroom fatuha ta dire jidda tayi mata wanka sannan itama tayi kusan tare suka shirya saboda itama yau ta gaji tasha surutu har da godema Allah, night dress suka sa sannan ta dau jidda tana mata surutu suna haurawa upstairs a hankali ta murda handle din kofar part din sadiq, a parlour suka iske shi zaune yana kallan news da gudu jidda ta fada jikin shi ,daddy yes angel ,um daddy ina ice cream din Anuty da chocolate din ta? laqace mata hanci yayi yace "Yana bedroom da gudu jidda ta shige bedroom fatuha kuma na qoqarin fita har ta bude kofar, jidda ta qaraso riqe da ledar shopping Anuty ga naki , angel har dani a tsarabar washe baki jidda tayi ta ce eh toh na gode ta amsa ta fita.

Direct bedroom din ta ta shige tare da kunna haske, saman bed ta zauna tare da bude ledar shopping din tun kan ta fara shan ice cream din miyan ta ya tsinke ,tana sha tana kada kai Amma fa wannan abu akwai dadi sosai gaskiya me kyau yasan kan kwadai, sai da ta cika cikin ta da ice cream sannan ta kwanta bacci yayi awan gaba da ita.

Akwana a tashi ba wuya wajan Allah sadiq ne janye da trolley din mom dana abba sai da ya zo bakin kofa ya ba ola da Sunday yayi musu umarnin da su sa kayan bayan boot, ok boss fatuha ko na parlour zaune sai tsoro take yanzu idan su mom suka tafi Allah ka dai yasan muguntar da sadiq zai mata ranan unguwa ka dai suka je amma sai da ta dandana kudar ta, bale kuma kwanaki duka wannan zancan a zuci take tare da kukan zuci dan tasan watan cin uban tane ya tsaya, su mom ne suka qaraso parlour tana riqe da hannu jidda sai lisafa mata tsaraba da zata mata take washe da baki fatuha ta tashi tana yi masu Allah ya kiyaye hanya , mom har ta kai bakin kofa ta juyo da kalli sadiq tace toh ga amanar fatuha sauran kuma inna dawo naji ka mata wani abu dan nasan halin, bata fuska yayi kamar qaramin yaro yana bin fatuha da harara tuni yan hanjin ta suka fara kadawa dan tasan kashin ta ya bushe daurewa kawai take amma ji take kamar ta daura hannu aka ta sa ihu gashi baba jinmai taje biki kauye daga ita sai rabi'a kuma rabi'a data gama aikin ta take tafiya ,jidda ce ta katse mata tunanin datake taré da janta tm har suka qarasa farfajiyar gidan, sadiq ne ya shiga wajan zaman driver da alama shi zai kaisu airport tuni jidda itama ta shige motar mom ce ta juyo tace fatuha duk abinda kike buqata kiyiwa baby magana kinji toh tace mata tana raraba ido tana daga masu hannu har motar su ta fita daga harabar gidan.

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.com

49_50

Su sadiq na fita harabar gidan, fatuha ta juyo gida cike da tsoro raurau tayi da ido kamar tayi kuka saboda tuntuni rabi'a ta tafi sai ita kadan kwal a gidan sai su ola, parlour ta zauna tayi tagumi kamar munafuka tana ta raraba ido kamar wadda tayima sarki qarya, ganin tsoran ba zai fishe ta da komai ba yasa ta kuna kallo washe da baki ta dau remote control tana canza tashoshi Bollywood ta kai tayi shiru tana kallan film gaba ki daya imanin ta naga TV jin cikin ta ya fara kukan yunwa yasa ta tashi dining area taje ta zubo macaroni da miya yaji kifi sosai kasan cewa fatuha ba mai san macaroni ba ce yasa ta zuba kadan, ta dawo parlour saman three star ta zauna ta Fara ci bayan ta kamala ta kai plate din kitchen tare da wanke wa bedroom ta koma tare da rage kayan jikin ta ta shiga wanka bata wani dade ba ta fito ko da ta fito lotion ta shafa tare da feshe jikin ta da turare white t-shirt din ta na aiki tasa kasan cewa rigar ta kawo mata gwiwa sai taji bata sha'awar sa skirt din gashin ta ta baza ta sharce masha Allah fatuha ba qaramin kyau tayi ba ,qarewa kanta kallo tayi a dressing mirror dariya tayi tace "Kai dan Allah dubi yadda nayi kamar ta cikin film din dana gama kalla hhhh lol" ta kumayin dariya tana godéma Allah da yawadata ta da gashi à haka tasa kafa tafita daga bedroom din.

Bangaran su sadiq har yana kai su mom airport , ya wuce da jidda family house dan shi yama manta da wata fatuha part din ammi ya shiga riqe da hannu jidda , a'a wana ke gani , murmushi

sadiq yayi tare da zama saman kujera yana gaisheta sannan yace, "Matar yanaga kin qara kyau?" washe baki ammi tayi tana gyara daurin dankwalin ta tare da amsa mai ta  qaraso parlour itama ta zauna, ohni mai gida ace min jiki yayi sauki da  har na fara dakan gunba ance min kana can rai hannu Allah ka zama dan gurgu ta ida zancan tana dariya ,turo baki sadiq yayi yace "Haba ammi har so kike na bingire kenan ?dariya ammi tayi tare da janyo jidda jikin ta yar nema yau ba'a amin gwalangwatsin ba smile jidda tayi kawai tare da cewa "Ammi ina gorubar da kika ce zaki siyo min ni da jamal? yar nema ashe baki manta ba ai tuntuni na siya tana daki na cikin  drowe, da gudu jidda ta shige dakin ammi ta dan juyo  tana facing din sadiq gyara murya ammi tayi tace "Ni ko Sadiq ya kamata kayi aure? Yanzu fisabilillahi dubi yadda jidda tayi wayau sosai yarinya na shirin zaman yan'mata, amma kai baka ko maganar aure bale nuna sha'awar ka ko dai baka lafiya ne Abubakar sadiq?" sadiq dake zaune saman three star ya hada gira sama data qasa kamar be taba dariya ba, kai kullun baka so a fada ma gaskiya sai ka hau gunguni shi kuma Ibrahim ya zuba ma ido ko maganar aure bai ma, sadiq ko  tunda ammi ta fara magana ya kai wuya dan shi be da tsarin yin wani aure yanzu, Alhaji ne ya qaraso parlour da alama yanzu ya dawo daga kasuwa ganin ammi nata fada yasa Alhaji qaraso dan yaji ba'a sin zancan, ganin sadiq  tatasa gaba ya san maganar gizo bata wuce qoqi, haba ladingo ya za ai ki tasa yaro gaba kina mai maganar aure? eh koma me ake samu a auran nan ai ya taba yi inya gaji da zama haka ai dole yayi aure tunda shi ba qarfe bane, ammi tabe baki tayi tace "Malam kenan da yaranan na da wannan tunanin ta tuni yayi amma kwata kwata banga alamar yin hakan ba , koma  dai meye ba kyau sasji gaba ba kina mai fada, ba ko abin motsa baki amma sai fada kike mai, shiko sadiq dadine ya mamaye mai zuciya sai  murmushi yake, ammi tayi yake tace "Wallahi malam abin ya tsayamin araine?" Alhaji zama yayi kusa da sadiq tare da shafa gashin shi yi hakuri kaji Abubakar sadiq, qaqaro murmushi sadiq yayi Wanda iya qarshi lips din shi yauwa ko kai fa, ammi kuma asiya ta kwalawa kira ta kawowa Alhaji abinci da sadiq, sadiq sai fama daurewa ammi yake bayan asiya ta kawo komai ammi tace ya sauko ya ci, na koshi ya fadi a taqaice, bude baki ammi tayi ta fara fada yanzu ni sadiq ban isa nama magana ba ko na baka shawara sai ka nunamin ban isa ba ko Ibrahim ai bai isa  yamin haka ba matsar kwalla ta fara Alhaji da ke gefe ta kaici ma ya hana shi magana sadiq ganin abun ammi da gaske ne ya sashi cin abincin tare da sakin rai sannan ammi ta ji dadi ba laifi ya dan saki jiki amma sai wani bangare na zuciyar shi ya ke ji kamar ta famamai inda ke mai qaiqayi tabas yasan yayi rashin kausar har abada bazai kuma samun wada zata maye gurbinta ba, amma wani bari na zuciyar shi yaqi yadda ya cusa san wata diya mace har ta samu gurbi a zuciyar shi numfashi ya sauke tare da miqewa tsaye yana kiran angel, mai gida kardai ka ce min tafiya za kayi ?ko har yanzu baka huce ba? murmushi sadiq yayi haba matar ni na isa nayi fushi dake nayi fushi dake gobe ina zan fake washe baki ammi tayi tace yauwa dan albarka , Allah yasa ma Albarka ameen ammi , bari na kirama yar neman nasan yanzu haka ta wargaza min daki dariya Alhaji yayi ya ce aiko data kyauta, malam har da kai masu biye ma ifiritan nan ko da yanzu Jamal zai zo su hade biyar baka siyan part din nan dariya Alhaji yayi tare da shigewa bedroom din shi, ammi kuma ta shige nata tana kwalawa jidda kira aiko tana isa dakin taci karo da abin goriba duk jidda ta watsar a tsakar dakin ohni ladingo ai dama na fadi nasan za'a rina tunda najiki shuru washe baki jidda tayi tace ammi, sadiq dake parlour ya qaraso yana dariya laa angel waya ce kiyi ma ammi baena turo baki tayi tace "Daddy ba bana nake ba" ammi tace gidan ku kikayi ko? dariya jidda tayi ta boye bayan baban ta , ammi bari mu qarasa part din

Umma toh shikenan saura canma ki mata barnar haqora jidda ta washe sannan sadiq yayi ma ammi sallama suka wuce part din Umma.

Parlour ta kuma dawowa tare da kallan agogo ganin karfe 3:00pm yasa fatuha rau rau da ido, tasan za'a rina tunda aka bar amanar ta a hannu sangami a iya tunanin ta ko wanne gari suka kai su mom ya ci ace sun dawo gida, zama tayi saman one star can kuma sai ta tashi upstairs ta haura sama direct part din sadiq ta shige a hankali ta murda handle din cikin sa'a kofar ta bude saboda a tunanin ta ya kulle part din, tana shiga sanyi da kamshi suka mamaye mata hanci lumshe ido tayi tare da mai da kofar parlour ta rufe bedroom dinshi ta shige tana ta kalle kalle wani album ta hango ya leqo ta qarqashin gado duqawa tayi tajanyo shi da hannun ta washe da baki ta bude album din pics din sadiq ta fara cikin karo da shi ya saki murmushi a pic din gashi yasha kyau har ya gaji ,cigaba tayi da ganin pics din album din wani guri ta Ganshi da kausar wani gurin shi daya ganin yadda suke pics din yasa fatuha ta dade tana kallan pics din ko ba'a fada mata ba tasan maman jidda ce saboda suna kama da jidda ji tayi gaba ki daya sun birge ta haka ta lalace tana kallan albums din kiran sallah la'asar ne ya sata qoqarin mai da album din har ta turashi qarqashin gado sai ta ji wani album din janyo shi tayi tare da yin smile, bari na tafi da wannan inna idar da sallah ya debe min kewa, tunda ni ka dai suka bari wato sun barni a gida duk abinda zai cinye ni ya cinye ni downstairs ta dawo ta aje album din a parlour ita kuma ta koma bedroom din ta dauro alwala.

Cikin sallama su ka shiga part din umma, Umma na zaune tana kallo tana shan fruit a hankali da alama zaman ya mata dadi ,cikin fara'a ta amsa sallamar su sadiq zaunawa yayi tare da gaishe ta ta amsa jidda ko saman ciyar Umma tayi masauki, yan'mata baba fari da ido jidda tayi tace "Na'am grandma" a'a waya koya maki fari da ido haka? dariya tayi tace "Anuty mana" wace Anutyn? Ta bata Amsa da cewa "Anuty fatuha mana" ah ni ban santa ba kam aiko Anuty fatuha na da kirki sosai yanzu haka tana gida murmushi Umma tayi tare da yi masu tayi fruits qasa sadiq ya sauko ya sha fruits din shi ya qoshi sannan ya haura upstairs cikin natsuwa ya murda handle din kofar daki kwance ya hango majid yana ta sharar bacci dan gutun tsaki ya ja tare da shiga daki fridge ya bude ya dau ruwa mai dan sanyi sanyi sai da yazo saitin face din majid ya zuba a hannun sa ya shiga yayafa mai, firgigit majid ya miqe yana qoqarin tashi ganin sadiq yasashi komawa ya zauna tare da zabga tsaki , kai dai wallahi mugune ,in banda mugunta ina bacci zaka sheqa min ruwa? harara sadiq ya aika mai yanzu lokacin bacci ne kana ganin la'asar ta wuce, mtss toh ina ruwan ka? da ruwa na sannan ya zauna saman sofa, wallahi big man baka kyauta min ba wallahi mafarkin wata hot baby nake kawai ka zo ka katse wa mutane jin dadi mtss tashi ka ban guri Dan iska kawai, dariya sadiq ya fashe da ita sakin baki majid yayi yana mai kallan rainin wayau me haka wai , kaga kyale ni je kayi wanka first munyi magana, ya ida zancan cikin dariyar shaqiyanci tsaki majid ya kuma ja sannan ya yaye blanket din jikin shi ya wuce bathroom ko 50 minutes beyi ba ya fito sanye da bathrobe dressing mirror ya nufa ya shafe jikin shi da mai da sunyi 4 eye's da sadiq sai ya aika mai harara shiko sadiq fuska yayi tare da janyo newspaper yana qarantawa sai da ya gama shirin shi tsaf sannan shima ya zauna saman sofa tare da qanqace ido yana kallan sadiq kamar zai mai masifa, dariya sadiq yayi tare

da kuma daurewa duka majid ya shiga kai mai dan iskan banza sai wani kallo kake kana dariya munafuki Allah kadai kasani, mafarkin uwar me kake to? Maji da yace "Dadin abun ba kai na farau ba, ya ida zancan yana harara sadiq" smile sadiq yayi yace nina ce ma wani abun ne? wanka fa kawai na ce kayi? ko nace wani abu ya ida zancan yana kare fuskar shi da newspaper yana dariya, sun dade sosai a family house ba su suka fara tunanin dawowa gida ba sai kusan 9:00pm lokacin jidda ma tayi bacci har farfajiyar gida suka rako su sannan sadiq ya ja mota suka bar gidan.

fatuha ko tana idar da sallah parlour ta dawo, ta cigaba ta kallan album tun bata jin tsoro har ta fara ji saboda duhu ya kunnu kai kuka ta ci ta gaji tare da rakubewa jikin kojera rungume da album har bacci wahala ya kwashe ta, a dai dai parking space yayi parking dauke da jidda ya fito tare da yima motar key a hankali ya bude kofar parlour, ya qarewa parlour kallo tare da kunna haske parlour ya gwaraye ko ina cikin natsuwa ya qaraso kallo daya yayi ma kujera da fatuha take kwance sannan ya wuce upstairs bedroom ya shin fide jidda sannan ya shiga bathroom ya watsa ruwa yana fitowa jalabiya white yasa ya fita daga part din, saboda yana son shan coffee ya dawo downstairs inda ya bar fatuha nan take kwance ware mata kallo ya shiga yi duka gashin kanta ya baje akan kujera , cinyarta bude yake kasan cewar qaramar riga ce a jikin ta fuskar ta Sadiq ya qarewa kallo masha Allah yauce rana ta farko da ya fara kallan fuskar fatuha da kyau eyes lash din ta sunyi gadar gadar kamar ansa mascara, tabe baki yayi yana qoqari shiga kitchen har ya kai bakin kofa ya dawo saboda album din da ya ganta rungume dashi cikin zafi rai ya juyo yace fatuha cikin daka tsawa cikin razana ta tashi tsaye tare da sakin album din qasa, dab da ita sadiq ya qaraso cikin zafin rai yace "Uban me kike min da album? Dan iskanci shine kika sakeshi kasa ko ? a tsawace yayi maganar" kuka fatuha ta saki saboda gabaki daya ya ruda ta mari ya wanke ta da shi lafiyayan open your month and talk to me , kuka fatuha ta saki mai tsuma zuciya tare da yin magana cikin shashakar muryar tace "Dan girman Allah kayi hakuri me nayi maka ne mai kyau? koko amanar da mom ta baka tun yau zaka fara cinta ta ida zancan tare da fashewa da kuka, bayan horan da kamin na barina a cikin makekyan gidanan be ishe ka ba shine Dan karfin hali harda mari na😭 kuka ta kuma saki tare rugawa da gudu bedroom.

Sadiq ko amanar mom da yaji fatuha tace ne yasa jikin shi yin sanyi tare da daukar album din jiki ba qwari ya haura upstairs.

*taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http//mobile.Facebook.com./Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.com
51_52

Fatuha na shiga bedroom saman bed ta fada tare da sakin saban kuka tana cigaba da jerawa sadiq Allah ya isa da ace Allah ya isan na fitowa a jiki to da daran yau ba abinda zai hana shi fitowa ajikin sadiq, kuka ta ke mai tsuma zuciya har da shesheqa tana a jiyar zuciya ita babban abinda ke damun ta koda ta zo mai muguntar sai ta kasa kuma ko tayi mai ramawa ya ke, lumshe idanuwanta tayi tare da sauke numfashi a hankali ta cigaba da jerawa sadiq alkaba'i haka har bacci barawo ya sace ta.

Bangaran sadiq ko saman sofa ya zauna tare da ganin be kyauta ma fatuha ba, lumshe ido yayi tare da ware su koma mai yayi mata ita ke san shiga gonar shi shiyasa shi kuma baya saurara mata da tasan yadda yake ji in yaga albums dinan da ko fada mata akayi ta dauko su inda ya aje ba zatayi ba, iska ya busar mai zafi daga bakin shi bayan ammi ta gama hada mai zafi ita kuma ta da gulamai lusafi album din ya bude a hankali kamar mejin tsoran wani abu ya shiga kallan pics din ya dade yana kallo inda yake ganin mutuwar kausar ta dawo mai sabuwa har hawaye sai da ya zubar kamar ba soja ba, anan saman sofa bacci ya kwasheshi.

*Asuba ta gari*

Ko da ya tashi da asuba wanka ya sheqa sannan yasa jalabiya ya wuce masallaci ,yana dawowa ya samu bacci mai cike da natsuwa amma duk da haka qirjin shi namai zafi saboda tsabar damuwa lumshe ido yayi tare da jan jidda jikin shi bacci ya kwashesu.

Fatuha ko da kuka ta tashi fuskar ta har tsami ta mata, saboda ba qaramin mari tasha hannun sadiq fuskar nan ta kunbura tayi sumtum kallan mirror tayi tare da fashewa da kuka

fuskar tayi jawur har idanta sai da ya qara girma saboda tsabar kuka ,toilet ta shiga tayi wanka tare da dauro arwala tana fitowa after dress tasa black tare da gabatar da sallah ko da ta idar da sallah kuka ta cigaba da rerawa sannan ta tashi jiki ba qwari ta murda handle din kofar tare da ficewa daga bedroom din direct part din sadiq ta shiga, duk da tana jin tsoro haka ta lalaba ta murda handle din kofar bedroom zaune ta hango sadiq saman sofa yana danna laptop yana shan coffee cikin dari dari ta qarasa shiguwa tare da yin sallama, dago kai sadiq yayi ya qare mata kallo shi kan shi yasan be kyauta ma fatuha ba ya bata mata baby face din ta, rabewa ta shiga yi dan tak take jira ta arce  sunan ta ya kira cikin cool voice din shi gaban ta ne ya yanke ya fadi duk da yauce rana ta farko da me kyau ya fara kiran sunan ta, sai  taji duk duniya ba wanda ya iya fadi fatuha qara kiran suna ta yayi hakan yasa ta fara matsar kwalla tana yarfe hannu  ta qarasa kusa da shi tare da tsugunnawa tana wasa da yantsun hannu ta idanuwanta taf da kwalla hannu yasa ya dago da habar ta lumshi ido yayi tare da waresu gaskiya be kyauta ma fatuha ba ji yadda ya mai da fuskarta, tausayi ta bashi sosai kuka ta shiga reramai a tunanin ta wani mari zai qara zabga mata shhhh ya ce mata cikin cool voice nashi shiru tayi tana matsar kwalla bedside drowe ya bude ya ciro magani a dan top sannan ya dawo sofe ya zauna tare da talabo mata fuskar matsar maganin yayi a hannu ya shiga shafa mata a face din ta kuka fatuha ta saka sai kace ya watsa mata ruwan zafi iskar bakin shi ya shiga hura mata mai sanyi nan fatuha ta lumshe idanuwan ta wani irin dadi taji dan tunda ta tashi da safe fuskar ke mata radadi sai yanzu da taji dama dama, ware eye's ball din ta tayi kan sadiq, sadiq da ke qoqari dagowa goshin su ya hade ushhh , shagwabe fuska fatuha tayi tare da fara kuka sorry yace mata sannan ya sa hannu ya murza mata wajan dan karya kunbura sannan ya kyaleta tare da yi mata lalausan smile  tashi tayi tana qoqarin daukar jidda su fita, fatuha yace juyowa tayi tana kallan shi, shiga da ita toilet dina ki mata wankan to ta ce mai sannan ta shige da jidda bathroom bin ta yayi da kallo tare da daukar newspaper.

Bayan ta wanke jidda tas suka fito washe da baki jidda ta gaisheshi, amsa mata yayi tare da yi mata pack, Anuty me ya sami fuskar ki jidda ta fada a tsora ce kallan sadiq fatuha tayi shima ita yake kallo sannan ya kauda  kai murmushi fatuha ta qaqaro tace "Bigewa fa nayi jiya, aini fushi nake dake Jidda kika tafi kika barni ni ka dai a gida to shine fa na bige gashi ba kyanan" raurau jidda tayi da ido tace "Sorry Anuty ba laifina bane laifin daddy ne ta ida zancan tana nuna daddy da hannu" daddy tace cikin shagwaba yes yace a  taqaice yana kallan newspaper, daddy please kar a qara barin Anuty a gida ita kadai daddy kalli face din Anuty fa?" tana fadi tana ware ido  juyowa sadiq yayi ya kalli jidda tare da lumshe ido angel kin fiye surutu please ki tsaya Anuty ta shirya ki kinga mun kusa maqara ,sai da fatuha ta gama shafe jidda da mai sannan suka fita kai tsaye bedroom din ta ta dire jidda ta shirya ta cikin uniform din ta sannan ta ruqo hannu ta suka fito parlour dînner area suka zauna ta shiga bama   jidda  abinci tana feeding din ta sadiq ya qaraso dining area riqe da briefcase din  shi kujera ya ja ya zauna ,plate fatuha ta janyo ta fara saving din sadiq yau anci sa'a be hana ta ba sai da ta gama zuba mai ta tura mai gaba sannan ta hada mai tea a cup ya amsa ya fara sha zai kai chips din baki ya kalli fatuha da ke feeding din jidda, yace
"Ke Baazakiyi break din ba?" kallan shi fatuha tayi ta hadiye wani yawo dan bata san me yake nufi da hakan ba murmushi sadiq yayi ya ce yar kauye kawai kalaci nake nufi washe baki fatuha

tayi tace "Aiyo zanci to" fara cin yanzu murmushi tayi tana ci tana feeding din jidda a zuciyar ta ko mamakin canji sadiq take, shiko sadiq amanar mom yake riqewa ba wai wani abun ba.

Bayan sun gama break har filin gida fatuha ta rako su da lunch box din jidda pack jidda ta mata tare da yi mata bye bye, fatuha na tsaye har suka fita daga harabar gida ta juyo ta dawo cikin gida kayan breakfast ta kwashe ta kai kitchen, a kitchen taga rabi'a na girki murmushi tayi tare da gaisheta amsa mata tayi cikin fara'a sannan ta aje kwanikan cikin zing ta wanke su tas rabi'a sai hannata take amma taki kusan tare sukayi komai na kitchen din sannan suka jera a dining area ,washe baki rabi'a tayi tace kai amma fa fatuha na gode dan ba dan ke ba da yanzu ina ta aiki wallahi murmushi fatuha tayi tare da cewa ba komai wallahi, bari na zo na lalaba na wuce gida ,kallan tausayi fatuha tayi tace "Wai har zaki tafi ne?" eh wallahi ,yanzu ni ka dai za'a bari a gida nan kamar maya ta ida zancan tana matsar kwalla, yi hakuri kin ji fatuha  akwai inda zani da ba inda zani  dana taya ki hira amma akwai inda zani, murmushi fatuha tayi tace "Ba komai bakin kofa ta raqo ta sannan ta koma parlour ta zauna tare da kunna kallo kitchen ta shiga ta gyara fruit sannan ta dawo parlour tana ci tana kallo har bacci ya kwashe ta.

Bangaran sadiq yana sauke jidda ya wuce office, ko da ya je office yayi aiki sosai karfe 2:00pm nayi ya fito yaje school din su Jidda ya dauko ta suka dawo office tare sai zuba mai surutu take kowa na office din ji yake da jidda daka ganta hannun wannan sai ka ganta hannun wancan sai la'asar sadiq ya amshe ta  suka wuce gida.

Fatuha ko kiran sallar la'asar ne ya tashe ta, wanka tayi tare da dauro arwala  tana gama sallah parlour ta dawo tana lunch cuscus ne da miyar kwai take ci tana jin dadin abincin har wani lumshe ido take, sallamar su sadiq ce ta qatse mata cin abinci washe da baki ta kalli jidda rugowa jidda tayi ta fada jikin fatuha tana dariya itama fatuha dariya tayi tare da gaishe da sadiq ciki ciki ya amsa kamar me koyan magana sannan ya haura upstairs ,fatuha ko saida ta cikawa jidda cikin ta da abinci sannan ta kai ta bedroom ta rage mata kaya sannan ta kaita toilette ta mata wanka sai da ta wanke ta tas sannan suka fito suna daririku lotion ta shafa mata sannan ta sa mata gwon brown mai kyau tare da jan hannun ta suka dawo parlour ,Hango sadiq sukayi yana zaune a dining area yana lunch guri fatuha ta samu ta zauna jidda ko wajan daddy ta nufa tare da haye mai cinya tana mai surutu, daddy yes angel ,daddy please muje shan ice cream please ta fadi tana lagwabe kai ja mata hanci sadiq yayi ya ce "Wannan bakin naki kullun san zaqi yake" dariya tayi mai nuni tana cikin farinciki,    ture plate din gaban shi yayi tare da aje jidda qasa qafa ta shiga bubuga mai ita aladule sai sun je shan ice cream yau ,  yace mata "Ok Angel is ok daina kukan kije Aunty ta Tashirya ki ko"   sannan ya haura sama yana last stairs jidda tace amma har da Anuty zamu tafi dan kar dodo ya ji mata ciwo toh, yace tare da bude kofar part din shi.

Shirya jidda tayi tsaf amma ita ta rasa kayan da zatasa, duk gwon din data janyo sai ta maida jidda rugawa ta yi parlour zaune ta sami sadiq cikin shirin shi na qananan kaya yasa red riga

mai ratsin black mai dogwon hannu sai wando black da takalmi yasha kyau har ya gaji sajan shi ya kwanta luf sai sumar kan shi da tasha gyara, daddy jidda tace ,a dan shagwabe sadiq ya juyo alamar gajiya menene angel lagwabe kai tayi tace daddy zo ka zaba ma Anuty dress ta rasa Wanda zatasa ,dan guntun tsaki sadiq ya ja yace "Angel me yasa kika fiye rigima?" um bata fuska tayi tana shirin yin kuka hakan yasa sadiq tashi ba dan ya so ba bedroom din fatuha ya shiga tsaye ya ganta gaban drower ta riqe qugu ga kaya baje a saman bed bakin kofa ya tsaya yana qarewa bayan ta kallo juyowa fatuha ta yi su kayi 4 eye's kauda kai tayi ta cigaba da abinda take a hankali ya qaraso wata gwon ya gani kawai ya janyo ba wai da ya lura da ita ba miqa mata yayi , kisa wannan mu tafi  sannan yasa kai ya fice cikin 5 minute  fatuha ta shirya cikin red gwon me Stone's sai black veil tasa tare da murza hoda ta shafa lipstick wani irin kyau fatuha tayi komai na ship din ta ya bayana duk da ba wasu shekaru gare ta ba kallo daya zaka mata Kasan ta hadu takalmi tasa tare da feshe jikin  ta da turare masu kamshi sanna ta yafa veil din ta a hankali ta bude handle din kofar bedroom din  parlour ta fito sadiq dake zaune saman two star ya lumshe ido, jidda na zaune gefe shi kamshin turaren fatuha ne yasa ta ware sexy eye's ball din shi ya sauke su kanta wani irin kyau ta mai tabe baki yayi yace ashe wannan yarin yar nada kyau duk yana wannan zancan ne a zuci miqewa yayi tare da daukar car key suka fita,  gaba jidda ta shiga fatuha na baya jidda sai zuba mata surutu take.

Sun sha yawo  kamar me ice cream ko har sai da suka ture, fatuha ko baki har kunne dan dadi duk inda suka wuce sai an kalle su saboda sun sha kyau sun gaji munjibir park sadiq ya kai su zama yayi a resting chair yana kallan su fatuha wasa ko ba wanda basuyi ba , basu suka bar munjibir park sai yamma likis a gajiye suka dawo gida, fatuha ko dadi fal a zuciyar ta jidda ko saboda tsabar gajiya tayi bacci cikin mota , sadiq ysa   hancin motar shi cikin gida parking space yayi parking bala mai gadi sai washe mai hakura yake daga mai hannu sadiq yayi tare da dai daita parking din motar sannan ya kashe motar fatuha kamar jira take ta fito murfin motar gaba ta bude tana qoqarin daukar jidda shima sadiq ya turo kai da hannu yana qoqarin daukar jidda ji kake gwab sun qume kai wash sadiq yace fatuha ma haka yadda sadiq yayi da fuska shi yaba fatuha dariya sai kace baby ,dariya ta rinqayi har ana ganin fararan haqoran ta  dariya da fatuha take sai ta qara mata  kyau hakan yasa sadiq  kallan ta kallan  da yake mata ne yasa ta tsagaita dariyar tare da daga mai gira harara ya aika mata ,in kin gama dariyar ki dauko ta mu shiga gida dariyar da yake shirin zo mata ta guntse tare da daukar jidda.

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Salma mas'ud nadabo*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=,52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSFULANIWRITERSFORUM.com

53_54

*Ina farin cikin tayamu marnar zagayowar wata mai Albarka,wata mai falala,wata mai dubin nasarori da ni'imomi , yan uwa Dan Àllah kada mubari wanga babbar garabasar ta wuce bamu samu nasarori da yake ciki,mudinga istigfari da hailala neman gafara à wajen Allah,mu yawaita Adu'a da karatun Alkur'ani mai girma, mu dinga nafiloli da rokon Allah ya biya mana bukatun mu na Alheri,Allah Ubangigi ya bamu ikwan yin ibada a cikin wanga watan mai Albarka watan Ramadan Allah yasa muna da raban ganinshi Ameen Dan Alfarman anabinmu Muhammad Sallah'llahu allaihi wa'sallam*

Sadiq na gaba tana biye dashi à baya, bakin bedroom din ta taci birki tana qoqarin bude kofar sadiq ya juyo fuskarsa ba yabo ba falasa yace"Iina kuma zaki da ita bayan tayi bacci? um dama wanka zan mata shafa sumar jidda yayi tare da cewa "Ki samata night dress kawai saboda tayi nisan bacci" Allah ya taimake ta jidda ta taba fadin Kalmar shiyasa ta gane mai yake nufi,haurawa sama yayi ita kuma ta shige daki tare da kunna haskyan dakin shin fide jidda tayi sannan ta soma rage kaya jikinta ,sai da ta shiga toilet tayi wanka sannan ta fito daure da qaramin towel cikin natsuwa ta shafe jikin ta da mai tare da zura night dress din ta riga ce pink mai zanan cartons jikin rigar, rigar dai dai gwiwa ta tsaya sai dan siririn hannun kamar na vest gashin ta ta sharce ya baje a gadan bayan ta bayan ta gama shirya kanta ta shirya jidda cikin kayan bacci, sanna ta dauke ta a hankali take taka upstairs din saboda yau jidda ta qara nauyi cikin natsuwa ta murda handle din kofar part din sadiq parlour ba kowa sai sanyi AC dake tashi da kamshi direct kofar bedroom ta bude tsaye ta hango sadiq gaban dressing mirror yana goge sumar shi da qaramin towel sanye yake da bathrobe white hakan yasa ana ganin lalausan gashinshi na qafa kauda kai fatuha tayi, tare da yin sallama juyowa yayi ya qare mata kallo , mamaki gashin fatuha ke ba shi gashin har yaso ya mata yauwa juyowa yayi ya cigaba da abin

da yake shin fide jidda tayi tana qoqarin fita,lumshe ido sadiq yayi tare da ware su yace "Fatuha" juyowa tayi tana kallan shi can sai tayi qasa da eye's ball's din ta, ki hada min coffee toh tace tare da fita downstairs ta dawo tare da shiga kitchen ta hada mai coffee ta dawo, ko da ta dawo yana zaune a parlour yana kallan news aje mai tayi saman stool tare da ficewa cikin natsuwa ya shiga shan coffee yana kallan news amma sai dai ku san kallan news din kawai yake ba wai dan yana fahimta ba kashe kayan kallan yayi ya koma bedroom saman bed ya kwanta tare da janyo jidda jikin shi lumshe ido yayi ba wai dan yana jin baccin ba ,saboda gaba ki daya kwanakin nan da tunanin kausar yake kwana.

Tana shiga bedroom ta fada saman bed tare da yin addu'a bacci ko minut 10 ba tayi ba bacci ya kwashe ta.

Kiran sallah asuba ne ya tashe ta wanka tayi tare da dauro arwala tana fitowa uniform tasa tare da gabatar da sallah, sannan ta shafa mai da fesa turare parlour ta fito ko ina share kwal hakan ya tabatar mata da rabi'a ta zo kitchen ta shiga washe da baki ta gaishe ta cikin fara'a ta amsa kasan cewar yau Saturday shiyasa fatuha bata je part din sadiq da wuri ba , rabi'a ta shiga tayawa aiki doya suka fere suka dafa sannan suka yanka fatuha ta gyara albasa rabi'a ta fasa kwai ta kade tare dasa albasa da percil da tonka santé da tafarnuwa da sauransu.. fatuha na kallo soya doyar da take , rabi'a da taga fatuha ta iya suyar sai ta sakar mata ta shiga gyara fruit saboda za'ayi ma sadiq juices da su bayan ta gyara ta markada ta juyo a jug ta saka qanqara ta kai dining area kafin ta dawo fatuha ta kamala soya doyar ta juye a kula rabi'a shigowa tayi da murmushi tace ,"Ah sannu da qoqari" murmushi fatuha tayi ki kai kula dining ni bara na soya kwai to fatuha tace tare da wanke hannu ta a zing ta dau kula ta wuce dining area, bayan ta aje kulla ta dawo parlour ta kunna kallo arewa24 tana kallan gari ya waye washe da baki take kallan dan tana jin dadin shirin ganin goma ta gota yasa ta haura upstairs tana bude parlour zaune taga sadiq saman three star, idanuwan shi lumshe abin ya so ya dan bata mamaki saboda be saba bacci a parlour ba sallama tayi sadiq da ke jingine kamar me bacci ya ware sexy eye's ball's din shi kan fatuha tare da amsawa kalla shi tayi ta tabe baki tare da gaishe shi amsawa yayi kamar be san magana fatuha ko shiga daki tayi amma sai dai yau tana ganin suku suku da sadiq yayi, yayi yawa sai taga yayi kamar wadda be samu bacci ba tabe baki ta yi tace ke "Fatuha ina ruwan ki?" duk wannan zancan a zuci takeyin shi tada jidda tayi washe da baki jidda ta tashe tana cewa,Anuty good morning? murmushi fatuha tayi tare da daukar ta ta kaita toilet ta mata kwanka suka fito suna dariya tsane mata jiki tayi sannan ta shafa mata lotion kasan Cewar akwai wasu kayan ta a dakin shiyasa anan fatuha ta shirya ta, jeans n t-shirt tasa mata rigar white sai jeans blue masha Allah tayi kyau sosai fita tayi daga dakin tabar fatuha na gyara daki.

Washe da baki ta fada jikin sadiq daddy morning, morning too angel, how was ur night angel, cool daddy n Ur's daddy same ya ida zancan yana mata pack, daddy yes sweet, um me ya sami

eye's din ka sunyi ja, lumshe ido yayi yace angel daddy ciwo ido yake, sorry daddy ,a kira uncle yakub ya duba ka please daddy, na warke ai har ma nasa magani ,sure daddy? yes angle pack ta mai tare da cewa daddy am Hungary, ok ina Anuty ? Anuty na busy now, OK muje nayi feeding naki ko sweet, OK daddy daukar jidda yayi yana mata wasa tana dariya sai da suka qaraso dining area ya ja kujera ya zauna sannan ya d'aura jidda saman cinyar shi  ya shiga saving din su sai da ya kamala ya fara feeding din jidda yana bata tana bashi cikin jin dadi.

Bayan ta gama share bedroom din tas ta dawo parlour ta kwalwale shi tas, ta kunna Burne  a socket tare dasa turaran wuta tuni part din ya dau kamshi mai sanyi gudun AC ta qara lumshe ido tayi tare da zama saman three star tana qarema dakin kallo, ita kanta part din ya mata kyau yadda ta gyara shi ji tayi kamar tayi bacci tashi tayi ta fita daga part din.

A hankali take sakowa daga upstairs jidda dake saman cinyar daddy ta kwalawa fatuha kira, cikin jin dadi Anuty juyowa fatuha tayi har sai da gashin ta iska ta kada shi fari tayi da ido tace "À" dariya jidda tayi tace "Daddy ka ga yadda gashin Anuty yayi lumshe ido yayi ya ware su kan fatuha yana qare mata kallo gani yake kamar idannuwan shi ke mai gizo kwanan kullun qara canza mai take kawar da zancan yayi ya cigaba da abinda yake,  saukowa jidda   tayi daga cinyar shi riqe da doya a hannun ta fada jikin fatuha Anuty na'am bude bakin ki na baki yam toh fatuha tace tare da bude dan qaramin bakinta ji tayi jidda ta bata ragowar doyar hannunta sadiq da ke zaune saman kujera dining yana kallan su ta qasan ido har mamakin yadda jidda ta saba da fatuha haka yake, tabe baki yayi ya shanye ragowar tea din da yake sha ya miqe  ya wuce su ya haura upstairs fatuha ko dining tazo ta cika tunbin ta sannan taja jidda suka koma parlour suna cikin kallo rabi'a ta fito tare da yi masu sallama, har bakin gate suka rakata bala mai gadi sai tsiya yake ma jidda ita kuma sai turo baki take fatuha ko dariya abin ya bata janyo jidda tayi suka dawo cikin gida suka cigaba da kallo.

Wani irin sanyi da kamshi ya doki hancin shi part din kwal kamar ba'a kwana ciki wani irin sanyayan ajiyar zuciya ya saki tare da sakin handle din kofar, bedroom ya shiga nan ma wani irin lalausan smile ya saki komai ya mai yadda yake so take ya ji wani irin bacci na fizgarsa saman bed ya fada tare da sauke ajiyar zuciya bacci da baiyi jiya ba shi ya kwasheshi.

Sun sha kallo har sun gaji  ba su suka bar parlour ba sai 1:30pm shima kiran sallah ne ya tashe su, arwala suka dauro sannan suka gabatar da sallah suna idarwa suka dawo parlour, ola ne yayi knocking din kofa fatuha ta tashi ta bude mai washe da baki ya kalle ta, cikin hausarsa mara fita yace madam sannu ,yawa fatuha tace , dama wannan malam min ne da ke koya maku karatu ne ya zo yanzu, murmushi fatuha tayi ta ce malam ai ba da rana yake zuwa ba ta fadi tana leqa waje bari ina zuwa daki ta shiga ta janyo  hijabin ta tare da daura zani saboda mini skrt ne jikin ta  sannan ta fito lokacin har ola ya koma bakin aikin shi malam na zaune saman tabirin mai gadi suna dan taba hira cikin natsuwa fatuha ta qaraso tare da gaishe shi, murmushi

yayi ya amsa, ah malama fatuha murmushi kawai tayi kinga yau na zo tun 2:00pm wallahi ina da wata safga anjima shine nace da naki zuwa qara na zo yanzu tunda kwana biyo ba muyi karatun ba murmushi fatuha ta yi ta ce aiko dai malam mun gode bari na kira jidda toh yace mata tare da tashi daga tebirin bala mai gadi ya koma inda suke gabatar da darasin, fatuha na shiga gida tasa mata hijabin ta suka fita.

Cikin jin dadi suka gabarta da darasin su inda malam yayi masu qari tare da yi masu yan tanbayoyi suka bashi amsa sai da ya tabatar sun gane misalin karfe hudu ya sallame su, ya wuce akan cewa gobe karfe hudu zai zo insha Allah littafan su suka kwashe suka shiga gida dama daure da arwala fatuha take sallah ta gabatar sannan ta cire zanin ta shiga wanka tana fitowa daure da towel ta tsane jikin ta tare da shafa jikin ta da lotion har ta dauko uniform din ta zata maida ta tabe baki, tunda na gama aiki ai sai na sa na gida dan ni na fara gajiya da su ta fadi tana turo baki wardrobe ta bude ta curo wata pink gwon mai dogwan hannu rigar simple ce mai kyau tayi shap sosai tayi mata kyau rigar ita kanta sai da ta yaba rigar parlour ta dawo ta zauna, jidda na zaune tana kallan carton itama ta zauna tana kallon.

Ring din wayar shi dake bedside drowe ne ya tasheshi dan guntun tsaki yaja tare da kai hannu ya dau wayar ,ba tare da ya duba suna ba,hello yace cikin alamar gajia ta daya bangaran a kayi dariya , sadiq tashi yayi zaune tare da saki guntun murmushi, wallahi sadiq baka da kirki Allah yasa ma ka gane mai magana yar dariya yayi tare da shafa sanjan shi ba Khaleed bane dariya Khaleed yayi yace ashe dai kana gane mutane dan guntun tsaki sadiq ya ja ya za'ai na kasa gane muryar childhood friend dina, ah ka kyauta ina majid ai ya fika zuminci, haka dai kace toh yau na leko Kano insha Allah zan shigo toh shikenan sai ka zo indan ka zo ka kira ni toh yace tare da yanke wayar agogwan dake manne a bangwan daki ya kalla ware sexy eye's ball's din shi yayi ohno na kwanta ina ta bacci har 4 ya gota tashi yayi tare da yaye blanket din jikin shi toilettes ya shige ya sheqa wanka yafito daure da karami'n tawel à kugunsa, sanye hannun shi riqe da qaramin towel yana tsane sumar kan shi yana cikin shafa lotion wayar shi ta fara ruri hannu ya sa ya dauka tare da karawa a kunne, hello big man ganin a filin gidan ku, smile sadiq yayi yace are u serious, yea angayama kowa irin kane Mara zuminci dariya sadiq yayi kai friend nine fa koma yane , toh shikenan ganin zuwa katse wayar yayi tare da zura jalabiya white ya fito daga part din shi ya wuce su fatuha a parlour suna ta karatun dan fatuha ta dake sai jidda ta koya mata karatun boko yanzu haka har ta iya ABCD.

Yana fita farfajiyar gida ya hango Khaleed jingine jikin motar shi mai tsada kallo daya zaka mai kasan shima dan hutu ne, kuma gaye ne sanye yake da shada tasha diki mai kyau Khaleed chocolate colour ne yana da saje da yakara bayanar da kyawunsa, yana da manyan ido murmushi ya saki ganin sadiq ya qara so fararan haqoran shi suka bayana cikin jin dadi sadiq ya qaraso tare da miqa mai hannu suka gaisa, Ashe dama zan kara ganinka a duniyar nan? murmushi Sadiq yayi bagashi ba ai kai ma baka zama shiyasa haka kuma dan last week ma na dawo daga London har muka hade da yaya jawad wajan shopping shi da matar shi har ya ke ce min sun kusa zuwa gida jira kawai yake Anuty shukara da haihu su zo, murmushi Sadiq yayi

ya ce haka ya fada min  suna tattaunawa har suka qaraso kofar parlour cikin parlour suka shigo har yanzu su fatuha na nan inda ya bar su ,Sadiq yace  "Fatuha"  dagowa tayi ita da jidda tare da gaishe da Khaleed murmushi Khaleed yayi tare da amsawa yana bin fatuha da kallo Sadiq ya katse mai tunanin da cewa "Fatuha ki kawo mana glass cup?" tace mai toh tare da shigewa kitchen ,jidda ga uncle Khaleed smile jidda tayi Khaleed murmushi yayi ya ce karka ce min angel ce ta girma haka ,ita ce mana zaro ido waje Khaleed yayi yace kai amma gaskiya mun yadda zuminci, come here angel kusa da shi jidda ta matso kallan ta yayi tare da daukar ta suka haura upstairs sai tanbayar ta ya ke tana zuba mai surutu suna shi ga part din Sadiq saman two star Khaleed ya zauna tare da daura jidda a cinyar shi ,sadiq fridge din bedroom ya bude ya curo lemu ka masu sanyi ya kawo ma Khaleed lokacin yayi dai dai da shigowar fatuha dauke da tray da cup's amsa tray din Sadiq yayi tare da yi mata nuni da ta dau jidda, Khaleed sai bin fatuha da kallo ya ke kiran jidda tayi suka fita a tare tana fita Khaleed ya sauke ajiyar zuciya, yana kallan  Sadiq, Sadiq din ma kallan shi yake ,big man ina kuka samo beautifully girl, wake nan ya fadi a taqaice wadda ta dau angel yanzu  murmushi Sadiq yayi yace "Fatuha she is my sister baka ga muna kama ba ya fadi zancan yana cigaba da zuba ma Khaleed juice" amma ai nasan kai ne dan auta baka da wata sister bashi glass cup yayi na lemo yana qara saki wani murmushin Wanda iya karshi lips din shi, she is my consin sister yanzu ka gane ko murmushi Khaleed yayi yace amma fa tana da kyau karka ce min basma ce ta zama mai kyau haka tanbayar Khaleed ta kusa fara kai Sadiq wuya amma sai ya maze yace ba ita ba ce wannan diyar sister mom ce eyya shi kan  Sadiq yana mamaki karyar da ya zauna yana shunfuda ma Khaleed toh me inya ce me aiki ce dan guntun saki ya ja a zuciyar shi ,Sadiq mom fa , mom ba ta nan sun tafi uk da abba OK hira suke sha sosai suna kallo.

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★we are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email*:realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook*:www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.com

57_58

*Godiya ta musanman gare ku mosayan ❤ wannan novel ina jin dadi 💃yadda kuke comments🤓 a kan wannan littafi hakan ya nuna min ana mugun tare 🤝 wannan shafin naku ne ,Dan Allah duk wadda nayima laifi ta yafe mini  ni nafe ma kowa Alfarman wanga wata mai Albarka mai falak mai dumbin nasrori watan Ramdan ,yan Dan Allah mu yawaita Adu'a da neman tafiyar Allah mudinga tashi cikin dare domin yawaita nafiloli da neman bukatunmu na Alheri à wajen Allah Allah yakaimu Farawar azumi lafiya Ameen Dan Alfarman anabinmu Muhammad Sallah'llahu allaihi wa'sallam Allah yasa muyi idaunmu cikin kociyar hankali da farinciki idan bamu ganshi ba Allah yayi mana rahma Ameen ni salma mas'ud nasani nake ma duk wani masoyina  happy Ramadan Kareem*_

*S* ai da fatuha taci kuka ta gaji sannan ta tashi ta shige kitchen, ta bude fridge ta ciro fruit  ta wanke ta dawo parlour tana ci tana kallo har bacci barawo ya kwashe ta.

A dai-dai bakin gate ya tsaya tare da yin horn shitu mai gadi ya taso ya bude mai gate, washe da baki yashiga gaisheda sadi , sannan sadiq ya sako hancin motar shi cikin gida Jamal dake filin gida yana ball ya saki murmushi ya biyo motar yana murna dai dai ta parking din motar yayi a parking space tare da bude murfin motar tunkan ya budewa jidda motar, tayi sauri fitowa ta washe ma Jamal baki small dad Jamal yace tare da fadawa jikin sadiq murmushi Sadiq yayi tare da d'aga shi sama yana mashi wasa dauke da shi ya shigo parlour tare da yin sallama Anuty bilki na saman three star zaune Hanan na saman one star cikin sallama sadiq yayi washe da baki Anuty bilki ta amsa tare wurga mai harara, sosa keya yayi tare da zama hanan da ke ,zaune a kujera ta gaisheshi a taqaice ya amsa mata tare da k'allan Anuty bilki cikin wasa tace dashi bl"Bari kallona!, ta fadi tana qara aika mai harara "dariya yayi yace "Kai sister tunda na kawo ta ai sai ki huce ban hucewa abinda sai da na rinqa binka sannan ka kawo ta, to ayi min hakuri plsss, toh tace tana kwallawa baba larai kira ta kawowa sadiq kayan motsa baki dauke da tray ta fito cike da kayan motsa baki ta aje mai a gaba tare da mai sannu da zuwa sannan ta juya ta koma bakin aikin ta, hira suka rinqa zubawa shida  yar uwar shi suna cikin yin hirar Aliyu min jin Anuty bilki ya dawo shima zama yayi aka dasa sabuwar hira da shi, basu suka tashi ba saida suka fara jin kiran sallah magrib, alwala suka dauro sadiq da Aliyu  suka wuce masallaci Kasan cewa Anuty bilki hutu take shiyasa ta cigaba da kallan ta.

Sai da aka gabatar da sallah sannan suka d'awo gida lokacin Anuty bilki ta shirya masu abinci a dining area ,aiko direct can suka  wuce dining area Anuty bilki ta shiga saving nasu lafiyayan jallof  taji naman rago da kosulo cikin jin dadi suka cin abinci tare da taba hira bayan sun

kamala cin abinci suka dawo parlour suna hira suna kallan news sai wajan karfe 10:00pm sadiq ya baro gidan Anuty bilki.

Kiran sallah magrib ne ya tashe ta d'aga barcci bedroom ta shiga tare da shigewa toilet ta d'auro alwala ta gabatar da sallah bayan ta idar tayi zaune saman daduma tayi tsuru tsuru wani irin tsoran gida take ji da wani fargaba, duk ji take gidan ya isheta tunanin rayuwar ta a kauye ita da fatsima ta shiga yi har da yan hawayan ta ji take k'amar ta rufe idanuwan ta ta ganta a kauyan wudil gaba ki d'aya kewar su inna ta dame ta, jan jiki tayi ta hau saman bed bawai dan tana jin bacci ba blanket taja tayi lamo tana matsar kwalla.

Bala mai gadi dake gyangyandi qara horn yasasa tashi firgigit wangale gate din yayi, yana washe baki qaraso da motar shi yayi dai dai saitin bala mai gadi tare da zuge glass din mota , murmushi yayi yace malm bala hala har ka fara bacci murmushi bala mai gadi yayi yace "Wallahi ko shi ke san dauke ni? saboda yar isakar da ake tana kadawa mai dadi sai kaji bacci na fizgar ka" murmushi Sadiq yayi tare da da ciro inda yake ajewa acikin motar yan' dubu dubu ko irgawa beyi ba ya damkawa bala mai gadi tare jan motar, bala mai gadi jerawa sadiq Albarka ya shiga yi da fatan alheri sannan ya soke kudin shi aljihu yana yin parking ya kashe motar tare da jingi da kujerar motar ya lumshe idanuwan shi tare da ware su murfin motar ya bude tare da samata ki yana shigowa parlour haske ya kunna ya gwaraye parlour k'allan parlour yayi ba kowa, t kashe haskan yayi a hankali ya qarasa bakin kofar dakin fatuha har zai murda handle din kofar sai ya fasa tare da ja baya ya wuce part din shi, fatuha ko duk wani motsi da sadiq yake a kunnanta take jin shin lamo tayi kamar me bacci haka ta rinqa zare ido har barcci ya kwashe ta.

Yana shiga bedroom toilet ya shige ya sheqa wanka ya fito, tsane jikin shi kawai yayi tare da zura k'ayan bacci yabi lafiyar bed ya kwanta.

Kiran sallah ne ya tashi fatuha toilet ta shiga tare da yin wanka tare da dauro alwala daure da tawel tafito Dan karamin towel na hannunta tana tsane jikin ta dashi, shafe jikin tayi da lotion tana gamawa tabude wardrobe ta ta janyo wasu Riga da sket tasha stone's a jiki ta mai kyau tana gama sasu ta dauko aftadress ta aza bisa domin gabatar da sallah tana idawa ta k'oma saman bed ta ta kwanta bacci ya qara kwasheta ba ita ta tashi ba sai karfe bakwai kallan agogwan dake manne jikin daki tayi tare da yin miqa toilet ta shiga tayi brush ta fito tare da sharce sumarta ta kwanta a gadan bayan ta a hankali ta bude kofar daki ta zuro kai ta laleqa taga ba kowa fitowa tayi ta nufi dining area tana qaraso wa taga sadiq zaune cikin shirin shi na unform yasha kyau har ya gaji dago eye's ball's din yayi su kayi ido hudu kauda kai yayi ya cigaba da breakfast gaisheshi tayi ya amsa a taqaice qoqarin barin gun take har ta juya yace "Fatuha" waigowa tayi hakan yasa iska ta hura gashin kan ta har ya shifi fuskar sadiq lumshe ido yayi tare da ware su a kanta itama din shi take kallo kauda kai yayi yace "Ki dawo kici abincin ki" washe baki tayi tare da jan kujera ta zauna saving din kanta tayi tare da janyo plate din gaban ta Sadiq kallan ta yake ta qasan ido hannun hagunta tasa ta gyara gashinta da iska

ke yawo da shi ta zura hannun ta, cikin plat ta fara cin abincin, chips ne da farfesun kifi wani irin dadi ya mata sai k'ada kai take tana ci sadiq mamaki qazantar fatuha yake, cin abinci da hannu ?ko wankesu batayi ba? kallan ta yake da gowar da zatayi ta kai wata lomar sukayi 4 eye's murmushin karfin hali ta mai tana qoqarin boye hannu ta dan kwata kwata ta manta yana wajan kauda kai yayi tare da daukar briefcase din shi kallan shi fatuha take tayi rau rau da ido ko kallan ta beyi ba yasa kai ya fice ture plate din tayi take nan taji abincin ya gundire ta, kwashe kwanikan tayi ta kai kitchen a nan ta ci karo da rabi'a na aiki gaisheta tayi ta amsa cikin fara'a taya ta aiki fatuha ta shiga yi tun tana hana ta har ta kyale ta, kusan tare sukayi komai na launch sannan suka jera a dining area bayan sun kamala fatuha ta shiga rokar rabi'a kar tatafi ta barta ita ka dai aiko taci sa'a rabi'a ta tsaya taji dadin hakan sosai, Dan haka ta wuce part din sadiq ta gyara shi tas ta dawo parlour suka cigaba da hira da rabi'a ko da aka kira sallah azahar tare sukayi sannan su kaci abinci sai kusan qafe hudu rabi'a tayima fatuha sallama fatuha bata ji dadi ba amma hakanan ta hakura ta zauna kiran sallah la'asar ne ya sata shiga bedroom ta shiga toilet tayi wanka tare da alwala saboda yau tasha aiki ba laifi wata hadadiyar Riga da isket ta kuma sawa hijabinta ta zura tayi sallah bayan ta gabatar da sallah ta cire hijabin ta dawo parlour, jin zaman parlour ya isheta ta yasa ta fita farfajiyar gida su ola da Sunday ne da sauran yaran sadiq suketa shawagi a gidan resting chair ta samu ta zauna tare da jin gina da kanta ta lumshe ido wani iska ke kadawa mai dadi da sanyi , Sunday ne ya zuguro imeka dake ta kallan fatuha har yana lashe baki hey imeka stop looking at her mind ur business this girl pass ur level na Oga consin sister be that I don't now fa amma this girl na beautiful ho u no go stop looking at her I will tell Oga sorry Sunday haba kar muyi haka da kai imeka ya fadi cikin hausar sa Mara dadi leave me alone Sunday ya fada , sorry lemme leave the place ma imeka tabirim bala mai gadi ya koma duk abun nan da sukeyi fatuha bata Sani ba.

Yau yasha aiki sosai wajan à office sai kusan yama likis sadiq ya nufo gida ,yana zuwa b'akin gate horn yayi bala mai gadi ya wangale mai gate ya kunno hanci motar shi hango fatuha yayi harabar gidan saman resting chair gashin ta ya bage kusan rabin qirjin ta duk waje suke domin Riga da isket ne ajinta Sun matse ta sosai d'omin da kyar take numshi, imeka da ke gefan bala mai gadi sai kallan ta yake ,lumshe ido sadiq yayi tare da ware su yaja motar da karfi dai dai parking space yayi parking ko dai daita parking din beyi ba ya fito cikin zafin rai fatuha dake kishingide ya nufa cikin zafi rai ya daka mata tsawa tare fisgota ta fada bisa fafadar kirjinsa ware ido tayi tare da saka mai kuka Janta yashiga ya cigaba da yi sai da ya zo parlour ya turata saman kujera har sai da kanta ya bigi kujera kuka ta qara saki tana kallan sadiq dan bata san laifin data mai ba, kallan ta yake ido cikin ido matsowa yayi daf da ita har tana jin saukar numfashishi matse mata fuska yayi cikin daka tsawa yace "Uban waye yace ki fita waje haka? ya fadi a tsawa ce" har cikin kanta sai da taji tsawar da sadiq ya mata runtse ido tayi tana girgiza kai tana kuka sakin fuskar yayi ya ja gashin kanta har saida ta saki qara tare da rushewa da wani saban kuka idan na qara ganin kin fita ba farfajiyar gidan nan baki sa hijabi ba sai na kona gashinan ya ida zancan taré da matse mata fuska da karfi kuka ta kuma saki tana kallan sadiq wani irin tsanar shi na fizgar ta, lumshe ido tayi tana jin zafi da radadin , wani wawan tsaki sadiq ya ja tare da tura ta ta bigi da kujera sannan ya dau briefcase din shi ya h'aura sama, kuka ta saki mai ban tausayi.

Yana shiga parlour shi ya wurgar da briefcase din shi ya zauna bisa kujera taré da lumshe ido, wata zuciyar ta ce mai "Kai sadiq ina ruwan ka da harkata? inma tsirara zata dinga yawo me ruwan ka ? runtse ido ya kuma yi" wata zuciyar tace masa "Ko Dan saboda tarbiyar diyar ka ka taka mata birki? saboda duk abinda tayi shi jidda zata kwaikwaya?" duk wannan zancan a zuci yake kiran sallah magrib ne ya tasheshi bedroom ya shige ya rage k'ayan jikin shi agurguje yayi wanka yana fitowa ko mai be shafa ba ya zura jalabiya a hankali yake sauko wa d'aga upstairs, inda ya bar fatuha har yanzu nan take kuka jin alamar tafiya ya sata dago jajayan idanuwanta ta kalli sadiq, sadiq ma k'allan ta yayi tare da aika mata harara mtss ya fice, kuka ta kuma saki sannan ta ja jiki ta shige daki tana alwala tana kuka har ta gama haka tafito ta zura abaya tana idar da sallah ta cigaba da lazumi har sai da aka kira isha'i ta tashi tayi sannan ta ja jiki ta k'oma bed ta cigaba da raira kukanta kanta har ciwo yake mata amma Dan jaraba takasa d'aina kukan.

bashi ya d'awo gida ba sai bayan sallah isha'i, yana shigowa parlour dining area ya wuce yana b'ude kulolin yaga alamar fatuha bata ci abinci ba d'ogwan tsaki yaja tare da rufe kulolin. K'wala mata k'ira yashiga yi shiru ba'a Amsa ba dan haka cikin natsuwa ya nufi dakin fatuha ya murda handle din kofar can saman g'ado ya hango fatuha cikin cool voice din shi yace mata " Yanzu Dan iskanci
kina jina kikayi banza dani?" Tayi shiru bata tanka masa ba, rashin yayi mugun bacci Dan haka ya daka mata wani uban tsawa w'adda ta sata zabura ta sauko d'aga bed tare da fashewa da wani sabon kuka😭, harara ya aika mata ya mata nuni d ta biyoshi, bin shi take har tana sarke kafa dining area ya isa itama taja ta tsaya oya wuce kici abinci ,à takaice tace masa ta koshi , wata tsawa ya kuma daka mata jiki na bari tana kuka ta fara zuba abincin dan kadan ta zuba wani irin kallo sadiq ya wurga mata tare da yin magana cikin daure fuska "Haka kike zuba abinci eeeh?" kuka tasa tare da cigaba da zuba abincin har ya kai bakin plate din tana qoqarin qara zuba wani sadiq ya matse hannunta da karfi har sai da ta saki qara, saboda ya lura bata da niyar daina zuba abincin juya abincin ta Shigayi ta qasa ci sai kuka , cikin murya mai sauti sadiq yace "Ko kiyi ma matune shuru! ko nasa alburushi na bula maki kai kowama ya huta, kuma abincin karki ci ki bari na tashi tsaye Allah danne ki zanyi na dura maki har da plate din" cikin hawaye fatuha tashiga dura abinci har tana jin kamar zatayi amai amma sai da ta cinye shi tana gama ci tayi qoqari tashi cikin sauri sadiq dake saman kujera dining area ya lumshe ido k'amar me jin barcci, har tayi nisa yace "Fatuha" juyowa tayi tana kallan shi hawaya da ke maqale a idanuwan ta suka gangaro bisa kumatunta, wani irin yerr sadiq yaji ajikinsa kallan ta yashiga yi kamar yauw yafara ganinta yakara Kiran ta akaro nabiyu "Fatuha!!!" gaban tane ya yanke ya fadi kuka ta kuma saki tare da dawowa ta durqusa g'aban shi tana rera wani saban kukan, a hankali sadiq ya kai lalausan hannun shi ya cigaba da gogema fatuha hawayan ta, lumshe ido tayi tare da ware su kan sadiq .yana gama goge mata hawayan ya mata alama ta tafi har tayi gaba ya ruqo hannun ta juyo da sauri domin ita yanzu yafara bata tsoro , Kangabar da kai yayi yace "Fatuha please kukan ya isa haka?" kallan shi take shima din haka, wasu Sabin hawayan ne suka qara zubowa wani irin kallo sadiq ke bin ta dashi ya koma abin tausayi kamar bashi ba hakan yasa fatuha hadiye wasu hawayen ,smile yayi tare da sakin ta cikin sauri ta shige daki tare da fada wa saman bed ,

shima sadiq upstairs ya haura cikin da farinciki dashi kansa mamakin haka yake..... Hmmm Kayi bayani Sadiq😘.

_*insha Allah bazan sake typing ba har sai bayan sallah wannan page din naku ne masoyan wannan littafin ga*_

_*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*_
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*_Writing by_*
*_salma mas'ud nadabo_*

*_Edit by_*
*_Raheenat_*

📘 *_REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM_*🐄
★we are the beat★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*_Email_* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*_Facebook_* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

_59_60_

*_Assalamu alaikum dibin masoya wannnan littafi ina mai yi maku B'arka da sallah kuma ina fatan kunyi sallah lafiyar Allah ya qarbi ibadun mu a yau ne zan cika alqawari nayi typing sai bayan azumin ga shi yau har Allah ya k'awo mu tabas duniya tana gudu Allah y'asa mu cika da imani_*

Tun ranar da fatuha tasha maqara ta shiga wasan boya da sadiq, kwata kwata b'ata bari su had'u dan ta lura aljanu ne gare shi, lol, ko gyaran part nashi za tayi sai ta b'ari ya tafi office haka shima bangaran sadiq bai wani damu da rashin ganin na ta ba, saboda yasan lafiyar ta lau of cos yana ganin part nashi fes .

Fatuha da rabi'a sun wani qara shaquwa musanman yanzu rabi'a bata tafiya gida sai 4, shiyasa fatuha ke dan jin d'adi gidan ita dai burin ta bai wuce ace su mom sun d'awo ba ko Jidda d'an ta gaji da zaman ka dai ci ku san tare suke aikin ma yanzu dan fatuha yanzu ta fara gogewa da girke girke dan yanzu kusan abinci gidan ita ke yin shi duk da rabi'a na h'ana ta.

Misalin karfe goma na d'are ya shigo gidan tsit ba motsin k'owa, inda sabo ya saba d'ama shi mutun ne ba mai san hayani ya b'ane part nashi ya wuce  tare da shigewa bathroom ya sheqa wanka,y ana  fitowa ko mai bai shafa ba ya zura jalabiya white ba qaramin kyau ta mai ba , fitowa yayi d'aga part din na shi ya wuce men parlour direct dinning area ya wuce abinci ya zuba dan ka dan shinkafa da miya ce tasha k'ayan had'i loma biyu zuwa uku yayi ya ture plate din dan kwata kwata b'aya jin d'adin jikin shi gaba ki daya ,yayi missing din jidda b'ama ya ganewa yayi missing nata sai ya je bacci  zai ji bed din wayam sai dai yayata juyi har ya samu bacci ya dauke shi, gashi b'aya so ya je gidan Anuty bilki yasan yana zuwa zata ce Jidda ta kawo shi shiyasa yake h'akura bangaran su mom ko duk san da ya tanbayi ranar dawowar su sai mom ta ce sai sun gama abinda suke.

Jiki ba kwari ya k'oma part din shi,  wata irin fever yake ji sama sama ga qirjin shi na mai zafi, magani ya cura d'aga bedside drowe  ya sha sannnan kwata ta tare da rufe jikin shi da blanket.

Asuba ta gari fatuha na tashi ta tsala wanka tare da gabatar da sallah, Sannan ta koma bacci cike da kewar su inna dan g'abaki d'aya yanzu kauye take so ta koma, zama gidan yanzu ya fara hawar mata kai abu d'aya ke mata dadi yanzu shine in malam ya zo k'oya mata karatu shima da sun g'ama ya tafi zata shigo gida kamar maya gaskiya ta gaji da irin wannan rayuwar gashi kwanan  ta lura mai kyau ko abinci baya ci, anya yana gidan ma kuwa ba ita ka dai suka bari ba Sannan ta ja dan guntun tsaki tare da gyara kwaciyar ta.

Ba ita ta tashi ba sai kusan karfe 10:30 brush kawai tayi tare da gyara gashin kanta ya kwanta har gadan baya, Sannan ta fito parlour sanye da gwon black mai kyau masha Allah fatuha tayi kyau ga wani haske da ta qara, gashi kullun yan matan ci bayana yake a jikin ta. Jin bata ji kamshi bane yasa gaban ta ya fadi leqawa kitchen tayi taga wayam ba rabi'a ba alama d'an bata rai tayi ta d'awo parlour tare da wucewa dining area bule kulolin jiya ta fara yi

jiya ma k'usan ita ka dai ta ci abincin dan guntun tsaki ta kuma ja tare da kwashe kayan ta wuce kitchen, gyara kitchen d'in ta shiga yi sai da kitchen din ya fita tas Sannan ta d'aura ruwan zafi k'an wuta ta fita sai da ta gama gyara k'o ina Sannan ta dawo kitchen ,ta juye ruwan zafin cikin Plack's sannan ta soya kwai ta juye a plate ta rufe yan ciki ta fido a fridge suma ta wanke ta gyara ta d'aura a tukunya t'are da gyara k'ayan miya ta zuba da k'ayan kamshi tuni kitchen din ya gwaraye da k'amshi d'adi, parlour ta fito tare da haurawa up stair's a hankali ta murda handle din kofar part din sadiq wani irin sanyi da kamshi dadi suka doki hanci ta, lumshe id'o tayi tare da ware su tare da qarewa parlour k,allo tsit parlour ba k'owa, h'akan ya tabatar mata da mai kyau ya tafi wajan aiki kofar bedroom ta nufa tare da bude ta a hankali ta shiga d'akin k'amar yand'a ta saba, sanyi AC ne kawai ke tashi sai kamshi k'ayan d'akin ta fara tatarewa duk da d'akin ba wani dati yayi ba blanket ta janyo zata linke sai taji anja, ware ido tayi waje tare da fara jin tsoro ko lafiya qara jan blanket din tayi taji anja dawowa tayi gaban bed din tayi ta tsaya a hankali ta kai hannu duk da zuciyar na dukan uku uku saboda tasan yau Tuesday sadiq na zuwa office kuma b'aya kai wannan lokacin bai fita ba, a h'ankali ta sa hannu ta fara yaye blanket din dai dai fuskar sadiq taja ta tsaya Chak, saboda ba abinda sadiq yake sai rawar dari .cikin rudewa fatuha ta ce "Mai kyau me ya same ka?" ta fadi bakin ta na rawa inbada rawar dari ba abinda ya ke sai hawayan fever d'ake bimai fuska dan ko magana be iyawa sai ma rintsa ido da yayi yana qoqari janyo blanket ya rufe jikin shi, riqe blanket din fatuha tayi har da yar kwalata mai kyau dan Allah me ke damu ka hannu ta kai ta taba goshin shin wani irin zafi taji rau take nan ta hau reramai kuka duk fever da ke jikin sadiq sai da fatuha ta dan bashi dariya, saboda yadda ta rude sai ka ce yau ta fara ganin ana fever amma sai ya guntse dariyar tare da qara lumshe ido dan bai San ganin wannan kukan ko mutuwa yayi ai sai h'aka fita tayi d'aga d'aki ganin zaman be fishe ta, tana zuwa bakin k'ofar fita suka ci qaro da ola shima zai shigo ya ji ko lafiya Oga bai fito ba ganin fatuha na kuka yasa shi tsayawa tanbayar ta lafiya kora mai bayani kawai tayi sannan. Shima ya haura sama part din sadiq wayar shi dake aljihu ya Ciro ya kira doctor yakub Sannan ya zauna saman sofa fatuha kuma na zaune kusa da sadiq tasa ruwan a ruba da towel tana dadana mai akai saboda jikin nashi ba qaramin zafi yayi ba cikin 15 minutes doctor ya qaraso gaishe shi fatuha tayi tare da matsa mai ya zauna, shi kuma ola ya fice , duba sadiq ya Shiga yi yan rubuce rubuce yayi tare da gwada BF din shi ya hau sosai kallan sa doctor yakub yayi tare da gwada kai ya curo allura ya mai fatuha dake gefe sai ka ce ance ita za ayima wa hada su rutse ido dan ba abinda ta tsana k'amar allura, bayan ya kamala duk abinda yake Dr yakub ya juyo cikin fara'a yace insha Allah anjima zai tashi kuma insha Allah fever zata sauka k'arki d'amu anjima zanzo, mai da magunguna dan Allah inya tashi ya samu yaci abinci dan babu alamar ya ci abinci idan zan d'awo zan dawo da ledar ruwa to fatuha ta ce mai tare da mai Godiya ta rakoshi har b'akin kofa ta koma ciki. Ko da ta koma ciki ,kitchen ta shige ta qarawa farfe Sun da take ruwa Sannan ta koma part din Sadiq leqa fuskar shi tayi ganin yana bacci yasata sakin ajiyar azuciya tare da taba goshin shi Alhamdulillah zazzabin ya sauka Sannan ta rage gudun AC d'aki ta fara gyara part din.

*_kuyi h'akuri da wannan page din nayi typing na shi sabod'a masoya masu san ji d'aga gare ni insha Allah gobe zan maku sweetest page_*

*_taku har kullun salma mas'ud nadabo_*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏽‍♂️

*_Writing by_*
*_salma mas'ud nadabo_*

*_Edit by_*
*_Raheenat_*

📘 *_REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM_*
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com-Real-Hausa-fulani-writers-forumRHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*_Email_*
realhausafulaniwritersforum@gmail. com

*_Facebook_* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

61_62

Sai da ta g'ama gyara part din tsaf sannan ta koma kitchen, lokacin har farfesun yayi ta juye a kula tare da plate ta zuba a tray tare da bread a hankali take taka upstairs saboda ta cika tray din da kayan abinci, baki kofa ta aje tray din Sannan ta bude k'ofar ta shi har cikin bedroom ta aje a stool qar'a leka fuskar sadiq tayi a qaro na biyu murmushi ta saki tare da zama gefan shi tana kallan yadda sajan shi ya kwanta luf har mamakin kyau irin na sadiq take ,sai dai yayi yar rama sannna fuskar tayi fayau dariya tayi tace "Ohni sangami ciwo yayi k'amu k'ayi bulun buqwi tunda likita ya tsulama allura kaji zafi sai bacci k'ake qila ma suma kayi saboda zafi, yadda kayi bacci kamar ba masifafe ba amma da ka warke zaka fara cika mana gida da tsuwa na huta da masifar ka ko ta kwana biyu ce wallahi um bari na lalaba naje nayi wanka a toilet din ka tunda

kai ka zama gawar shanu dan tashin ka ba yanzu.

Tashi fatuha tayi ta bude wardrobe ta Ciro qaramin towel ta tare da rage k'ayan cikin tasa towel, duk wannan abinda fatuha keyi duk a kunnan sadiq dan ya d'ade da tashi kawai dai yayi lamo ne toilet din ta shige ta sheqa wanka ta fito ko da fito cikin sanda take tafiyar har ta qaraso gefe bed leqa fuskar sadiq tayi tana riqe da qaramin towel tana goge gashin kanta, Allah sarki ba wan Allah sai bacci kake b'aka san wainar d'ana ke toyawa ba wai da zaka tashi d'ana sha masifa, yarfe gashin k'anta tayi wanda hakan yasa ruwan gashin ya watso ma sadiq a fuska dan motsa ido yayi hakan yasa fatuha zaro ido tare da yin lamo tana zare ido tana yar fe hannu ganin ya juya ya gyara kwaciyar shi ya sata sakin a jiyar zuciya baki dressing mirror din shi ta tsaya tana k'allan mayu kan d'ake baje akan dressing mirror tsuru tsuru tayi tana tunanin man da zata shafa can ta kai hannu kan wani mai na gashi k'asan cewa fatuha ba boko yasa ta d'auka ta fara shafawa sadiq dake k'allan ta ta qasan ido sai dariya yake guntsewa in taqaice maku duk wani mai d'ake saman dressing mirror sai da ta shafa dan taji ya mai kyau ya ke ji Sannan ta fita d'aga d'akin, tana zuwa bedroom din kaya tasa sadiq d'ake d'akin d'ariya yayi sosai har da riqe ciki dan guntun saki ya ja tare da cewa "Yar kauye kawai Sannan ya tashi a hankali duk da har yanzu b'aya jin karfin jikin shi" waka yayi Sannan ya fito yasa jalabiya ash mai kyau Sannan ya gabatar da sallolin shi, yana idawa ya qara koma wa ya kwanta dan karfin hali kawai yake.

Sket da riga tasa na atamfa mai ratsin dark green da coffee sai gyara gashin kanta da tayi tare da yin ture ka ga tsiya, Sannan ta qara fesa turare rufe bedroom din tayi ta fito Sannan ta haura upstairs direct bedroom din sadiq ta shige kwance ta gan shi amma sai dai wannan lokacin idanuwan shi biyu murmushi ta saki tare da qaraso wajan shi cikin sanyin murya tace "Mai kyau ya jiki?" lumshe ido yayi tare da ware su kan fatuha jim yayi yana qare mata kallo ba qaramin kyau tamai ba musanman dan qaramin lips din ta pick kauda kai yayi tare da cewa da sauki ya lumshe ido smile ta kuma yi tare da janyo tray dake saman stool ta cigaba da saving nashi cikin natsuwa kasan cewa tasan be cin abinci , shiyasa ta zuba mai farfesun yan cikin k'adan ciki dan ball,

Cikin sanyi murya ta kuma cewa "Mai kyau" ware sexy eye's ball's din yayi ya qara sauke su kan lips din ta cikin shagwaba da sanyi murya tace "Mai kyau dan Allah ka ci farfesun nan ka ga likita yace ka ci abinci" hade rai sadiq yayi tare da lumshe ido tare da yin magana cikin cool voice nashi yace "Bana jin yunwa fatuha" dan bata rai tayi tare da rausaya kai tace "Dan Allah k'aga ko akauye inna in bani lafiya in banci abinci ba har dure take min dan na samu lafiya ka ga yanzu mom bata nan bale ama dure dan Allah ka ci ta ida zancan tana rausaya kai tana k'allan sadiq dake kallan ta kamar qaramin yaro" qara hade rai yayi yace "b'afa naci leave me alone pls" zaro ido fatuha tayi tace "Kai kasan wannan" murmushi yayi wadda be yi niya ba yace "Fatuha wai yaushe zaki waye?" dariya tayi tace "Sai ranar d'ana fara zuwa boko ka ga da jidda nan ita ke koyamin yanzu kuma tana gidan Anuty bilki ta ida zancan tare da yin raurau da ido" ai ta kusa dawowa kin ji um to kina san karantun ne, bai ida rufe bakin shi ba Dr yakub ya

shigo, cikin salama tare wurgawa sadiq harara d'ake kwance gaisheshi fatuha tayi har qasa sannan ta dau ball din farfesun ta aje a tray tana qoqarin fita, ah wai fita zakiyi da kin tsaya ai murmushi fatuha tayi tace "Ina da abinyi ne a kitchen shiyasa ok wannan abincin fa nawaye kallan sadiq tayi dake ta faman aika mata harara tayi tsaye tare da sada kanta qasa ,juyowar Dr yakub yayi su kayi ido hudu da sadiq mtww h'aba captain me yasa kake haka ne please wai bana sha fada ma ba ka rage damuwa um saboda tsabar damuwa  ka daurawa k'anka hawan jini, me yasa kake abune kamar Mara tawakali ai kowa ya Sani duk me rai mamaci ne tunda kausar ta bar duniya ka daina walwala ka maida zuwa asibiti kamar zuwa kasuwa haba captain ko Dan lafiyar ka da matsayin ka ka hakura da wannan tunanin please, lumshe ido sadiq yayi k'amar yakub na magana da dutse tsaki Dr yakub yaja yace "To wannan abincin da k'aqi ci  me hakan ke nufi?" ware ido yayi yana aika ma fatuha da harara dan shi kwata kwata be buqatar wani abinci a cikin shi amma saboda tsabar naci irin na fatuha yanzu ta sasa ya ci abinci dan guntun tsaki yaja yana kalla yakub dake ta masifa yanzu  ka daure ka ci abinci ko nama alura ai dai ba saina fadama ila da alura kema mutun ba inbai ci abinci ba, duk yadda ya so ya kwace ma qincin abinci sai da yakub ya takura mai ya sha farfesun k'adan  ba tare da bread ba ba laifi farfesun ya mai dadi duk da b'akin shi ba test  aje ball din yayi fatuha ta dau tray din ta fita alura Dr yakub ya mai tare da daura mai ledar ruwa saboda ya lura sadiq be san cin abinci yana lafiyar ma yaci kadan bale yanzu.

Dawowar fatuha ce tasa Dr miqewa yace "To ni zan wuce dan Allah ki kulla da cin abincin shi inbai ci ba ki kira Anuty bilki ki fada mata ai yasan halin ta"  d'aga kai fatuha tayi sannan ta taimakamai da daukar mai briefcase din har sai da suka zo b'akin kofa ta mai sallah ta rufe gidan bedroom din sadiq ta kuma dawowa harara ya bita da shi sannan ya ja saki murguda mai baki itama tayi tare da zama saman sofa, keee wakike murgudawa baki rau rau da ido fatuha tayi tace "Bada kai nake ba" D'awa kike to? ya fada cikin sigar masifa um ba da kai nake ba wallahi mtww wallahi karki bari na tashi dan na tashi saina karkaryaki, bama na hana ki yawo ba hijabi ba eh amma ai a waje ka ce ba'a gida ba,yaja tsaki mtww  sannan ya juya ya lumshe ido.

*_Taku har kullun salma mas'ud nadabo_*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*_Writing by_*
*_salma mas'ud nadabo_*

*_Edit by_*

*_Raheenat_*

📘 *_REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM_*🐄
★We are the best★

http/Mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=,H-R

*_Email_* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*_Facebook_*www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

63_64

Juya b'ayan da sadiq yayi yasa fatuha jan dan guntun tsaki tare da kallan agogan dake maqale a bango kusan karfe 8:30 na dare, tashi tayi ta bar part din ta koma part din su tana shiga bedroom din ta rage kayan jiki ta tare da shiga toilet ta sheqa waka ta fito daure da towel ko shafa mai ba tayi ba ta bude wardrobe ta Ciro kayan baccin ta riga da wando pink masu Mayan flowers da zanan ya'yan cartoon d'aure gashi k'anta tayi da wata yar kibiya ta d'aure kai sannan ta fesa turara har zata kwanta sadiq ya fado mata a rai ta barshi a d'aki shi ka dai ,gashi baya da lafiya tashi tayi zubur zata fita sai Kuma taci birki tace "Ko naje tijara zai mun dan ba mutunci gare shi ba" karma ya tsinka ni wata zuciyar tace haba fatuha duk rashin mutuncin mutu be lafiya ai dole ya shafa wa mutane lafiya riqe handle din kofar tayi kamar me na zari can kuma ta bude ta wuce part din sadiq  ta shiga dakin har yanzu bacci yake parlour ta d'awo ta kuna kallo dan ba wani bacci take ji ba  cikin jin dadi take kallan arewa24 suna shirin tarkwan kauna  gaba ki d'aya film din ya mata d'adi sosai sai da aka kamala film din misalin karfe 10:00 na dare sannan ta leqa dakin sadiq b'akin bed din ta tsaya tana qaremai kallo a hankali ta kai hannu zata taba goshin shi amma ta k'asa sai dunqwule hannu tayi tana nazarin jikin naji ganin ya motsa ya sata gyara tsayuwa tana kallan yana yin shi lumshe ido tayi a hankali ta kai hannu ta goshin sadiq ji tayi zafi rau kamar garwashi mamaki ne ya kamata da tsoro cikin rawar murya tace "Mai kyau?" shuru sadiq yayi saboda shi ka dai yasan yadda yake jin fever na damu shi kneel down fatuha tayi gaba gadan ta qara cewa mai kyau a qaro na biyu, bude sexy eye's ball's din yayi a hankali yana kallan fatuha data fara matsar kwalla smile yayi yace cikin cool voice nashi "Menene fatuha? kin kasa bacci ne?" girgiza kai tayi alamar a'a to menene kallan shi fatuha ta kumayi tace 'Masasarannan ta matsama baka ji jikin ka da zafi ba da a kauye ne da inna ta dafa ma magunguna kuma da kasha zaka warke amma nan likita sai duba ka yake

amma ka qi warkewa mai kyau dan Allah ka daina tunani kaji shiyasa kaqi warkewa ta fadi zancan tana matsar kwalla" kallan ta sadiq kawai yake yana mamaki irin tausayi na fatuha gabaki d'aya tabi ta rude tunda t'aga be lafiya lumshe ido yayi tare da warewa ya sauke so a kanta insha Allah fatuha zan daina kinji murmushi ta saki mai hade da kuka kuka ta tashi ta shiga toilet din sadiq shi kuma ya bita da kallo ruwa ta debo a babba ball ta tasa towel a ciki ta dawo d'aki har yanzu idanuwan sadiq na kan fatuha ko qif tawa bayayi, sai da ta qaraso gaban shi ya lumshe ido aje ball din tayi a gefen bedside drowe cikin na tsuwa ta shiga matse towel din a hankali ta nufo towel din da goshin sadiq ta fara dadan namai kamar yadda inna ke mata in tana masasara ko ina na jikin shi ta bi inda ke bude tana danna mai towel din a hankali fever ta fara sauka shi kanshi Sadiq yaji dadin jikin shi sai dai dan dumin da jikin yayi bacci ne ya fara fisgar shi kafin ka ce mi bacci ya kwashe shi, sai fatuha d'ake ta faman dannamai towel.

A hankali ta fara gyan gyadi dan ta fara jin bacci ,sai bacci ya fisgeta sai firgigit ta tashi ta cigaba sai da bacci yaci karfin ta ta fada fadadan qirjin sadiq bacci ya kwashe ta.

Kiran sallah asuba ne ya tashi sadiq a hankali yake bude sexy eye's ball's din shi ya sauke su kan fatuha da ke bacci malemale a qirjin shi ga gashin ta ya baje saman qirjin shi matsar da gashin yayi yana qarema fuskar ta kallo ,har mamaki wayau irin na fatuha yake gata qarama amma sai dai tana da halin manya yunqurin tashi yayi yaji ta motsa komawa yayi, lumshe ido yayi lamo kamar me bacci. tashi fatuha tayi tare da ware ido tace "Nashiga uku yaushe bacci ya kwashe ni? wayo Allah na da mai kyau ya tashi ya ganni dana bani" hannu ta kai goshin sadiq jin ba zafi yasata sakin ajiyar zuciya Alhamdulillah jikin yayi sauki bari nayi sauri na d'auro alwala part din ta bari ta wuce nasu.

Alwala k'awai ta dauro ta gabatar da sallah, bayan ta idar ta tsaya lazimi da bita qaratun ta saboda anjima da rana malam zai amsa .

Fatuha na fita sadiq ya ware idanuwan shi tare da tabe b'aki yunqurin tashi yayi yaji hannu shi yayi zafi, sai a lokacin ya tuna da ledar ruwan da aka qaramai har ruwan ya qare ga hannu ya kunbura ya manta shaf be cire ba yaye blanket din jikin shi yayi ya shiga bathroom sai da yayi wanka ya fito sanye da bathrobe da qaramin towel a hannu shi yana goge sumar shi da hannu daya saboda d'aya hannu namai
zafi sosai.

Lokacin yayi dai dai da turowar kofar waigowa yayi yana kallan kofar, fatuha d'ake b'akin kofa itama shi take k'allo kauda kai tayi tare da cewa inakwana amsa mata yayi babu yabo babu falasa qoqarin fita take yace "Fatuha." juyowata tayi ta na kallan sadiq Wanda shi ma ita yake kalla yace "thanks for the caring" murmushi fatuha ta saki duk da bata ji abinda yace karshe ba

ta gane mai yake nufi da Kalmar farko   qarasa fita tayi shi kuma ya cigaba da aikin  gaban shi.

Yau ma k'amar jiya h'ar yanzu rabi'a b'ata zoba har hankalin fatuha ya fara tashi da rashin zuwan nata, shara tayi da wanke wanke sannan ta fera dankali ta soya ta juye a kuloli tare da kwai sannan ta daura ruwan zafi ya tafasa ta juye kamar yadda rabi'a keyi haka tayi har su ola sai da ta basu nasu amma har yanzu lamarin rabi'a na bata mamaki zuba k'ayan abincin sadiq tayi a tray ta aje a dining area sannan ta shige bedroom ta cire k'ayan baccin ta shige bathroom tayi wanka tana fitowa mai ta shafa tasa material  red mai ratsin golding a jiki masha Allah fatuha ba qaramin kyau tayi ba daure gashin ta tayi da yar kibiyar soke g'ashi sannan ta fesa turare  mai kamshi sannan ta fito d'aga bedroom,

Direct dining area ta wuce ta  dau tray din  kayan abinci San an ta wuce part din SadiQ , a hankali ta tura kofar bedroom din kishingide ta ganshi saman bed yana sanye da riga da wando riga mai dowan hannu red mai ratsin black sai jeans blue ba qaramin kyau yayi ba fuskar nan tashi tayi fayau cikin sallama fatuha ta shigo, amsa mata yayi a ta qaice aje tray din tayi a stool,

Sannan tace, "Mai kyau ya jiki ?" amsawa yayi cikin cool voice din shi, jiki da sauki fatuha to Allah ya qaro sauki sannan ta zauna saman sofa tana facing din sadiq wayar shi ce d'ake saman bedside drowe ta fara ruri hannu ya kai ya dauka sunan da ya gani jikin screen din wayar ya sasa smile,

D'aga d'ayan bangaran Anuty bilki tace "Hello baby , ya kake ?" lafiya lau  Maman hanan ya naji voice naka wani iri , yanzu na ta shi d'aga bacci ya fada a taqaice , murmushi tayi d'aga d'ayan bangaran, bari na baka jidda tun jiya  take matsamin tayi missing naka kai da fatuha smile sadiq yayi Wanda ya bayana fararan hakuran shi miqawa angel wayar Anuty bilki tayi, daddy? yes my princesses, dadd I miss u miss u more angel daddy yaushe zaka zo d'auka na? sai end of this week angel yeee daddy  love u dadd ina Anuty fatuha gatanan kusa dani pls dadd ka bata muyi magana I miss her ok Angel lemme give her.

Fatuha dake zaune saman sofa sai smile take saboda ta gane da jidda sadiq yake waya, saboda da ita ka dai yake waya yana smile ko mom miqa mata wayar yayi ta kara a kunne cike da jin dadi tace Jidda na'am Anuty dan bata fuska fatuha tayi hakan ya  fito mata da sak yarintar ta , jidda haka ake ki tafi ki barni ni ka dai a gida dan Allah ki dawo kin ji, laaa Anuty baga dadd ba ya tayaki wasa ai daddy ya iya wasa dago ido tayi ta kalli sadiq da shima din ita yake kallo ta hadi wani yawu tace cikin zuciyar ta gaskiya jidda ba hankali ina ni ina wasa da sangami mtww Anuty da jidda ta ce ne ya maido da fatuha daga dugwan tunanin da ta tafi sun dade sosai suna waya da jidda har mamaki fatuha take yadda suka dade kamar ba kudi ake dibaba.

Miqawa sadiq wayar tayi tare da qoqarin bude kulolin abincin dake saman stool, saving nashi ta shiga yi chips n egg sai farfesun yan ciki dake ta zuba kamshi ni kaina ganin qoqarin fatuha nake dan yanzu baza ta wuce 14 years ba, bayan ta kamala saving din nashi ta miqamai plate din hade da fork amsa yayi yana qoqarin daukar fork din da hannu amma ya qasa saboda hannu yayi tsamin daurewa yayi zaiyi ta maza ya ci da hannu kan dole amma ya kasa fatuha na

lura da yadda yake matsawa kan shi taimakamai tayi ta amshi plate din sadiq ya bita da kallo debo chips din tayi ta kai mai baki duk da tana gudun tsinki na sadiq aiko taci za'a ba musu ya amsa haka ta cigaba da feeding din shi yana amsa har sai da chips din ya qare sannan fatuha ta saurara mai, tana qoqarin qaromai wani zaro ido sadiq yayi waje yace fatuha wazai ci wannan? kai mana lalai to wannan din da kyar na dura shima anfada maki kowa irin kine acici harara fatuha ta aika mai ta na qoqarin tashi riqe hannu ta yayi yace sorry murmushi ta saki sannan ta dau plate din chips din tana ci.

Rayuwa na tafiya komai na gudu kwanakin da sadiq ya dauka yana rashin lafiya duk wata dawainiyar shi fatuha ce take bashi kullawa, hakan yasa wata irin shaquwa ta shiga tsakanin su da sadiq a yanzu jin fatuha yake kamar qanwar shi hakama itama fatuha kusan yanzu kullun suna tare sai dai inya tafi aiki ko masallaci yanzu sosai fatuha ke jin dadin gidan haka shima sadiq duk wani tunani da damuwa ya ragu ba kamar da ba, har wata yar qiba yayi saboda fatuha bata barin shi da yunwa dan yanzu kusan ita ke feeding din shi duk wani abinci tana bashi tana mai hira har ya cinye be Sani ba kullun fatuha sai tasasa dariya da labaran ta haka rabi'a ma ta dawo ta amshi aikin ta ashe itama fever tayi.

D'ariri kun d'ake tashi a dakin sadiq ,ya Sani tura kofar kar ayi ban dani fatuha ce sanye da rigar sadiq ta uniform na wajan aiki ala dole sadiq take kwaikwaya dariya Sadiq ya saki tare da matsowa kusa da ita ja mata hancin yayi tare da cewa "Fatuha baki ji ko?" dariya ta saki tace "Mai kyau ai haka kake yi inkasa uniform ta ida zancan tana qoqarin fita daga bedroom din "riqe hannu ta yayi ya ce " Anjima ki shirya zamu je dauko angel tsale tayi tare da rungume sadiq tana d'ariya shima din rungume ta yayi yana smile dan sakin sadiq tayi tace "Wallahi da jidda b'ata nan gidan ba dadi "ko eh mana ok oya kije ki shirya ki cire min kaya bata fuska sadiq yayi yace 2days dinnan kin fara rai nani Allah, turo b'aki gab'a fatuha tayi tace " Yi hakuri smile Sadiq yayi yace wannan b'akin naki ya iya b'ada hakuri kuma ya iya rashin jin" zame wa tayi d'aga jikin sadiq ta fita tana saukowa downstairs ta hango baba jinmai na shigowa da k'aya niqi niqi wani irin ihu ta saki ta ruga da gudu wajan ta ta rungume ta sadiq da ke qoqarin shiga toilet ya fito da sauri ya rife part din shi chak ya tsaya a up stairs yana mamakin rashin hankali na fatuha guntun saki yaja ya juya ,kallo baba jinmai tabi fatuha da shi tana mamakin rigar da ta gani jikin ta dan murmushi tayi Wanda iya Karshi lips din ta, fatuha ta katse mata tunanin da cewa baba shikenan sai ki tafi ki barni ni ka dai a gida nan? dan Allah yi hakuri fatuha wallahi hidimomine suka min yawa kuma b'ada niyar Dade wa naje ba niyata nayi kwana biyu na d'awo toh shinkenan bari nayi sauri nayi wanka dauko jidda zamuyi d'aga gidan Anuty bilki toh baba tace fatuha ta wuce bedroom baba jinmai ta bita da kallan tuhuma Allah ya rufa asiri sannan ta dau ledar tsaraba k'ayan miya ta shige kitchen

*_Taku har kullun salma mas'ud nadabo_*
*_CAPTAIN SADIQ_*
👮🏽‍♂️

*_Writing by_*
*_Salma mas'ud nadabo_*

*_Edit by_*
*_Raheenat_*

📘 *_REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM_*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*_Email_* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*_Facebook_* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

65_66

Bayan ta tsala wanka ta shafe jikin ta da lotion mai kamshi da sanyi dadi, riga da sket tasa na atamfa mai ratsin pink green blue masha Allah k'ayan sun mata kyau sai suka qara fitowa da haskyan ta daura dan kwali tayi ya zauna sosai a kanta ta janyo green veil din ta sa sannan ta sura takalman ta black tare da fesa turare ,b'ayan ta kamala ta fito d'aga bedroom parlour ba kowa sai kamshin girki baba jinmai da ke ta tashi,

Part din sadiq ta wuce a hankali ta bude kofar parlour, ba kowa sai sanyi AC d'ake tashi cikin natsuwa ta nufi bedroom ta burda handle din kofar tsaye ta hango sadiq gaban dressing mirror sanye da blue riga mai gajeran hannu sai blue Jeans ya gyara sajan shi yayi luf luf haka sumar kanshi ta kwanta yayi kyau sosai ,juyowa yayi su kayi ido hudu da fatuha kashe mata ido yayi yace kallan fa murmushi tayi ta kauda kai tana qoqarin fita yace wallahi kika fita ban zuwa da ke make kafada tayi tare da qarasa shigowa murmushi yayi yace "Good girl" yana qoqarin saka mabalin rigar shi b'ayan ya kamala ya dauki car key din shi da wayan shi dake bedside drowe ya nufo inda fatuha take yace inyee yan'mata ansha kyau ashe dai yan kauye sun iya

gayu, dariya fatuha tayi ta rufe fuskar ta tana aika mai harara oya tashi mu tafi a tare suka fito d'aga part din shi lokaci yayi dai dai da fitowar rabi'a zata tafi gida  kallo tabi so da shi tana mamaki yaushe sadiq ya fara wannan wasan tap, koma dai minene ai fatuha yarinya ce akan yan'matan dake mai layi kumama ko giyar wake yasha abinda take tunani ba shi bane watsar da zancan tayi tare da yin gaba fatuha ce ta kira sunan ta rabi'a waigowa tayi a dan tsorace tare da sakin murmushin da iyakar shi labanta ,har zaki tafi eh wallahi na gama aiki na kuma dama gashi baba jinmai ta dawo toh ki gaida gida gida zai ji fatuha ta Sakai ta fita.

Suna fitowa k'allo ya koma Kansu ola jiki na bari ya nufo sadiq har qasa ya gaisheshi imeka da Sunday duk sai da suka kwashi gaisuwa, sannan ya bude murfin mota ya shige haka ma fatuha ya ja motar suka bar harabar gidan cikin natsuwa yake driven din waigowa yayi ya kallin fatuha da ta rakufe guri daya yace "Fatuha "na'am yau anfito bude ido ko Dan smile tayi tace tunda nazo birni wannan ce fita tana na biyu ai qara haka  saboda bana san to much of yawa um kina san karatu saurin d'aga kai tayi inna saki school kina so kirinqa karatu kina kulla da angel zaki iya saurin d'aga kai tayi ga farin ciki shinfide a fuskar ta insha Allah zan saki kin ji, lokacin yayi dai dai da  tsayawar motar su bakin geta din gidan Anuty bilki horn yayi mai gadi ya bude masu ya kunna hancin motar shi,

Dai dai parking space yayi parking tare da kashe motar ,fatuha ta fito shima ya fito yana gaba fatuha bayan shi knocking din kofar sukayi baba larai ce ta bude masu washe da baki har qasa ta gaishe da su sannan ta basu hanya suka shigo cikin sallama Anuty bilki da ke parlour zaune saman three star tana kallo washe da baki ta amsa sannu da zuwa baby  saman two star ya zauna fatuha kuma ta zauna a qasa kusa da sadiq tare da gaishe da Anuty bilki, cikin fara'a ta amsa kwallawa baba larai kira tayi ta kawo masu kayan motsa baki aiko ko 5 minute batayi ba ta d'awo riqe da tray cike da kayan motsa baki ta aje gaban Sadiq ,kallan fatuha yayi dake zaune gefan shi a qasa tayi shuru itama shi din take kalla harara ya aika mata yace tashi ki zauna a kujera Anuty bilki smile tayi tace aiko dai tayi zaune qasa abin ta ni ban ma gane ta ba wallahi naga ta girma sosai raban dana ganta tunda su mom suka tafi yau kusan 2month kenan, ai jiyama mukayi waya dasu mom insha Allah ranar Friday zasu dawo tare da yaya jawad, aini fushi nake da su sun barni ni ka dai a gida  ai sun kyau dama shagwabar ka ta ishemu ya kamata ka zo kayi aure haka naga har wata yar qiba kayi fatuha dake zaune saman one star ce ta kalli sadiq shima ita yake kalla ji tayi gaban ta ya yanke ya fadi da furicin Anuty bilki kauda kai tayi. Kalla ta Anuty bilki tayi tace na aiki su hanan ne amma yanzu kinga sun d'awo bata ida rufe bakin ta ba suka shigo da gudu angel ta fada jikin daddy murmushi Sadiq ya saki daddy I miss u miss u more angel kissing di kumatunta yayi itama tayi mai hanan cikin fara'a ta nufi fatuha basma kuma na gefe tsaye tana satar kallan sadiq kasancewa ta zo Hutu gidan Anuty bilki, gaishe da sadiq sukayi ya amsa a takaice sannan hanan taja fatuha suka wuce dakin ta  angel kuma na maqale da daddy

Suna shiga d'akin hanan basma ta cire mayafin kanta ta fada saman bed,  itama hanan bed ta hau fatuha kuma ta  zauna saman sofa, laa fatuha baki zama saman bed a'a bari a nan ma yayi wallahi basma kinga wadda nake fada maki mai gashin nan d'ago kai tayi ta kalli fatuha ta

dan yi smile sannu ki fa yauwa inji fatuha hira suka shiga zubawa kasan Cewar duk sa'anin junane amma dai basma ta dan girme su dan yanzu ita SS2 zata hanan kuma SS1 kunsan a tare suke komai da hanan da basma duk da basma Anuty ce a wajan hanan sosai fatuha ta saki jikin ta amma sai dai tana dan dari dari da basma , kiran sallah magrib ne ya tashe su d'aga fira alwala suka dauro suka gabatar da sallah bayan sun idar angel ta shigo da gudu d'akin tace "Anuty fatuha daddy yace ki fito mu tafi?" to tace tare da yafa mayafin ta a tare suka fito d'asu hanan parlour a tsaye suka tada sadiq Anuty bilki ce ta bata rai tace haba baby kabari kuyi dinner mana sai ku tafi a'a gaskiya yau girkin baba jinmai zanci I miss her food ohni ba kayi missing din nawa ba ko ba haka bane sis so kike muyi barnan na gida ko toh shikenan a gaida gida dan ko rakiyar banyi langwabe kai sadiq yayi pls kar muyi haka mana harara wasa ta kaima sannan ta ja veil din ta dake saman kujera suka fito a tare hira suke sosai kamar karsu bari , bude murfin mota sadiq yayi angel ta shige gaba fatuha na b'aya sannan ya ja motar be zame dasu ko ina ba sai shop right shiga su kayi yayi masu siyaya sosai ice cream teddy's duk ya kwaso kayan wasa kamar be jin kudin ya cika boot da su sannan suka juyo gidan a gajiye likis.

Yana horn bala mai gadi ya bude mai geta yayi parking sannan yayi masu ola nuni da su kwaso kayan boot lokaci ma jidda tayi bacci, fatuha ce ta dauko ta suka shige gida upstairs sadiq ya haye fatuha ta shige bedroom kaya kawai ta cire ma jidda tasa mata na bacci, tana qoqarin cire nata akayi knocking din kofar zura hijabi tayi ta bude ola ne riqe da trolley din jidda da k'ayan wasan ta duk ya aje sannan ya mata sai da safe rufe kofar tayi ta rage kayan jikin ta ta wuce toilet tayi wanka ta fito daure da towel tsane jikin ta ta yi ta shafa mai sannan tasa rigar baccin ta gown dai dai gwiya white n brown mai zanan cartoons sannan ta saki gashin kanta tare da daukar jidda part din sadiq ta wuce da ita a parlour ta same shi yana k'allan news ,sanye da k'ayan baccin shi maroon riga da wando mai dogwan hannu bedroom ta shige ta shinfidar da jidda sannan ta fito har yadda ta barshi a parlour har yanzu haka yake qoqarin fita take yace fatuha ki kawo min dinner nan to ta ce mai sannan ta fita.

Direct dining area ta wuce ta zubo mai tuwan shinkafa miryar taushe tasha naman rago sai kamshi ke tashi ,sannan ta wuce part nashi saman stool ta aje mai plate din zata fice riqo hannu ta Sadiq yayi tare da cewa "Fatuha, waya bata makin rai tunda muka dawo naga baki farin ciki? ko bros ya maki laifine?" laa Allah ba abinda kamin kawai na gajine yau munsha hira da su hanan toh naji amma ai ba kiyi dinner ba bana jin yunwa ice cream din dana sha ya cika min ciki wallahi ok tunda hakane na fasa kai ki school din zaro ido waje fatuha tayi dan Allah kayi hakuri Allah zanci tam oya zo zauna muci zame hannu ta tayi daga ruqwan da sadiq ya mata ta zauna a qasa tare da janyo plate din gaban ta shima sadiq din zama qasa yayi cikin natsuwa ta fara kai loma daya sannan ta debo ta kaima sadiq amsa yayi wata lomar ta debo ta kai mai baki hadawa yayi da yatsanta ya ciza yar qarasa ta saki tana yar fe hannu ta dariya sadiq ya saki ,kuka ta fara mai tana kaimai bugun wasa riqe hannu yayi yana dariya ya rungume ta sorry sis yana magana yana shafa bayan ta lamo tayi a fadandan qirjin sa tana maida numfashi dago da fuskar ta yayi yace sis yau baki surutu kamar ankule maki baki gashi kin bata min night dress da miya gaskiya ba zan yadda ba ya fadi a dan shagwabe, kallan shi fatuha tayi ta lumshe ido tare da cewa yi hakuri mai kyau bazan sake ba good girl to fada min

Fushin nan name to um um dama ina so naje kauye ne kwana biyu wajan inna kafin na fara zuwa makaranta wannan shine damuwar eh ok karki damu insha Allah zan kai ki zame jikin ta fatuha tayi daga na sadiq riqe habar ta Sadiq yayi yace fatuha ki dauke ni kamar yayan ki duk abinda ke damun ki ki fada Mani na maki alqawarin samamaki farin ciki kamar yadda kika samamin fatuha murmushi ta saki wanda ya bayana fararan hakuran ta daukar plate din abinci tayi zata fita sadiq ya rako ta har kitchen ta aje plate din ta wanke hannu ta.

sai da ta zo b'akin kofar Shiga bedroom sadiq ya mata pack a goshi itama ta mashi a kumatu sannan ta shige bedroom shima ya haura upstairs.

B'ayan kwana biyu h'aka rayuwa ta cigaba da tafiya inda sadiq ke b'awa fatuha da jidda kulawa sosai haka suma suna faran tamai rai duk wanda yaga sadiq a yanzu yasan b'aya fama da wata matsala ,sai wani kyau da yake ta qarawa bangaran karatun adini kuwa fatuha tayi nisa sosai tana mai da hankali yadda ya kamata  kuma a yanzu duk duniya bata da aboki ko qawa sama da captain shine uwar ta shine uban  b'ata bari yayi fushi da ita ko kadan baba jinmai ko duk yadda ta bigi cikin fatuha ta fada mata wani abu na daban sai ta gane abinda take tunanin ba haka bane zala shaquwace kawai tsakin sadiq da fatuha.

Dr yakub yafi kowa farinciki da canji irin na sadiq har mamaki yake da hamdala da sadiq yaji shawarar shi.

Kwana biyu ko d'aya je wajan ammi ma taji d'adi ganin canjin shi h'aka majid da kwana shi biyu da dawowa d'aga Lego's anmai transfer ya d'awo kano da aikin sosai sadiq yaji d'adi hak'a ko ba komai dan uwan shi ya d'awo kusa da shi.

Kasancewa yau ta k'ama friday shiye shiye ake sosai na tarbar su mom ,yau zasu d'awo Nigeria tare da yaya jawad h'aka Anuty bilki  ta kwaso duka yaranta tazo dasu  anata aiki , fatuha na h'ango sanye da uniform din ta na yan'aiki wanda ta Dade raban data sasu sun mata kyau sosai part din sadiq ta wuce riqe da cup ganin b'aya parlour yasa ta tura qofar d'akin yana tsaye gaban dressing mirror sanye da shada blue ta sha aiki da dark blue zare yana combing din gashi kan shi, murmushi ya saki tare da qarasowa wajan fatuha amshe cup din yayi ya aje saman stool kallo tabi shi da shi dan yau ba qaramin kyau ya mata ba har mamakin kanta take har yau ta kasa ganin wanda yafi sadiq kyau da komai gashi kullun qara kyau yake ,hura mata iskar da akayi ya sata ware manyan idanuwan ta tana kallan sadiq, smile yayi yace "Tunanin fa? kin hanani tunani amma ke gashi kinayi yanzu" ah bafa tunani nake ba to mikikeyi bayan gashi na gani um kayi kyau thanks  ke  ma kinyi kyau a haka din eh mana cup din ya dauka ya kai bakin shi hmmm ya lumshe ido lalai fatuha ta iya hada coffee gaskiya zani  da ke dariya tayi tace "Allah idan na biye ma sai mu kwana anan muna surutu hehe" ko tam shikenan tafi tunda tafiya zakiyi ni bana so kiyi aikin shiyasa nace akiramin ke amma tunda kin fi so ki wahala

shikenan tafi munma bata, langwabe kai fatuha tayi tace "Kayi hakuri ka ga su mom ne zasu d'awo kaji" ok  amma sai kin min pack ko kina tafiya to tace tare da yimai pack a goshi sannan ta fice d'aga d'akin sadiq ya bita da k'allo.

*_taku har kullun salma mas'ud nadabo_*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best ★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

67_68

Da misalin karfe 1:00pm flight din su mom ya sauka Nigeria lokacin har Sadiq ya Isa airport da yaran shi ,kusan mota uku akayi ta tarbar su mom da abba a hankali suke saukowa d'aga matatakalar jirgin mom na sanye da lace ash mai ratsin pink blue abba na sanye da shada brown tasha aiki da dark brown zare yaya jawad da Anuty shukura na b'aya suma sunsha shigar alfarma tana riqe da baby ta , jawahir yana riqe da hannu baban shi cikin fara'a suka qaraso gaban motocin.

Cikin sasarfa sadiq ya qarasa ya kai ma mom hug, dan murmushi ta saki baby wai yau she

zaka girma ne? inji abba dake gefe mom b'ata fuska sadiq yayi irin na shagwaba tare da cewa "Danma banyi kuka ba kun tafi kun barni yar dariya jawad yayi sannan yaran sadiq suka bude masu motocin suka shige .

A tare motocin suka kunno kai gida bala mai gadi ya wage geta washe da baki yana daga masu hannu, dai-dai parking space motocin suka faka suka fara fitowa tun k'afin su shigo gida yan gida suka fito kowa ka kalla kasan cike yake da farin ciki ,haka jikokin a tare suka shige parlour su ola suka shige da k'ayan su ciki.

Murna wajan sadiq ba'a magana saboda d'ama yayi missing din mom din shi dakuna suka shige matafiyan suka sheqa wanka, sai misalin karfe 3:00pm aka halara a dining area duk wanda ka kalla cikin farin ciki yake cikin natsuwa suke lunch din inda jawad da sadiq suke ta zuba hira Anuty bilki da shukura matar jawad amma duk wannan hira sadiq na kalle kalle ya ga ta inda fatuha zata fito, abinci ne gaban shi amma ya qasa ci saboda yanzu ya saba tare suke ci da fatuha ko tayi feeding din shi loma biyu zuwa uku yayi ya ture abincin.

Bangaran fatuha ko tunda ta kamala aiki cikin ta ke nukurkusa duke take a daki sai kuka take zubarwa, qoqarin miqewa take ta kasa saboda cikin ba qaramin kullewa yayi ba bude kofar da a kayi yasa fatuha d'ago jajayan idanuwan ta hanan ce tsaye bakin kofar cikin sauri ta qaraso fatuha meke damunki ta fadi a dan tsura ce kuka ta kuma saki tana riqe da marata, ganin ba abinda fatuha take cewa yasa hanan fita lokaci kowa na parlour ana zuba hira Momi tace cikin rawar murya kowa ya waigo Momi fatuha ba lafiya gata can kwance tana kuka wai cikin ta mikewa tsaye sadiq yayi har suna yar rige rige da Anuty bilki h'aka mom ta biyu bayan su suna Shiga suma a durkushe suka same ta ,sai kuka da take ta fama rairawa Anuty bilki ta matso kusa da ita tare da cewa "Fatuha minene ?" cikin kuka kuka tace "Ciki na Momi " sorry tashi a kaiki asibiti kinji bana iya tashi ta fadi tana qara sakin saban kuka Anuty bilki ce ta taimaka mata ta tashi gabaki daya sket din ta ya baci da jini ashe aladace ta fara, sannu kin ji kallan mom Anuty bilki tayi ta mata nunu da ta kori su sadiq waje aiko haka akayi aka tasa keyar su waje.

Sannu kinji fatuha girmane ya zo kinji ba wani abu bane, yanzu Shiga toilet ki wanke jikin ki sai kin fito na gwada maki yadda ake d'aga kai fatuha tayi ta shige toilet a duduke Anuty bilki ta fita taba sadiq kudi ya siyo pant ya d'awo kallo ya bita da shi tare da cewa ki bar kudin bari naje na siyo, murmushi tayi ta maida kudin ta cikin handbag sannan sadiq ya fita ko minti 10 beyi ba ya d'awo ya miqa mata part din, ta qara komawa lokacin fatuha ta fito duk yadda ake anfani da part haka Anuty bilki ta gwada ma fatuha tare da bata yan shawarwari na gyara jikin ta saboda yanzu ita ba yarin ya bace sosai ta ji dadin sannan ta bata magani tasha saman bed ta koma ta kwanta bacci ya sure ta Anuty bilki ta fita.

Basu suka bar parlour ba sai da akayi kiran sallah magrib yasa suka wuce masallaci ,su kuma matan suka wuce part din mom basu suka dawo ba sai bayan isha'i jawad ya wuce part din su sadiq ya shige gida parlour ba kowa bedroom din fatuha ya wuce a hankali ya bude kofar

kwance ya hango ta saman bed ta dunqule waje daya rife kofar yayi tare da qarasa shigowa gaban bed din yayi kneel down a hankali ya kai hannu yana shafa mata gashin kanta a hankali ta ware idanuwan ta kan sadiq, kuka ta saka mai mai cike da shagwaba da yarin ta, "shhh kukan ya Isa haka mana um kamo hannu shi tayi tana qoqarin kai mai inda ke mata ciwo sauri kauda hannu yayi tare da wayin cewa dan ya lura har yanzu fatuha yarin yace shiyasa take haka mai kyau na'am Sister dai ciwo eh mana gobe da kin tashi zaki ji kin warke kin ji sis to ta ce mai tare da riqe hannu shi tana wasa da su kamar an tsunkune shi ya tashi ya fita fatuha ta bishi da kallo.

Kitchen ya shige ya d'auko mata fresh milk mai sanyi ya d'awo bedroom din har yanzu tana yadda ya bar ta bata fresh milk din yayi ta Kafa kai ta shaye sannan ya mata pack tare da yi mata good night ya fice.

Kun san kwanan fatuha 4 tana period tayi wanka mom ta gwada mata duk yadda ake h'aka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin jin dadi inda yanzu duk gidan ba wanda bai san shaquwar fatuha da sadiq ba, mom ko in ban da dadi ba abinda take ji dan gani take fatuha alheri ce a rayuwar su sannan sadiq ya sheda mata zai kai fatuha school kuma tayi na'am da zancan.

Harhada k'ayan ta d'ana jidda take a trolley saboda yau zasu je wudil, baki har kunne b'ayan ta gama hada kayan ta wuce part din sadiq zaune a parlour ta same shi harara ya aika mata tare da kauda kai, dan bata fuska fatuha tayi tare da matsawa kusa da sadiq mai kyau! qara kauda kai yayi, yi hakuri innama laifi ta mike zata fita ruqo ta yayi tare da wace shine dan zaki tafi gida shine ko ki leqo da safe yi hakuri, ka hada kayan naka ?nop to na hada ma eh yace a taqaice aiko d'akin ta shige ta h'ada mai nashi k'ayan cikin trolley ta fito da su d'ama shima ya shirya saboda tsabar zumudi ko break ta qasayi haka mom ta mata shatara na arziki har bakin mota ta rako su ace warsu kwana biyu zasuyi su dawo saboda ankusa komawa school da sun dawo fatuha zata fara zuwa.

Sannan sadiq ya ja mota suka bar harabar gidan angel sai murna take tare da zuba masu surutu har bacci ya kwashe ta.

Ko 2 hours basuyi ba suka Isa wudil tunda suka iso fatuha ke bin kauyan da kallo ,rayuwar ta da fatsima ta d'awo mata sabuwa dai dai kofar gidan su fatuha akayi parking har yanzu gidan na yadda yake sai dai dan tsufa da ya fara sai yar kofar da akasa cikin sauri ta shige gidan,

Inna na zaune saman kujera tayani gulma tana tankade, fatuha ta shigo da gudu ta fada jikin

ta dagowa inna tayi a dan  tsorace washe baki tayi ganin fatuha binta inna tayi da ido dan dai fatuha na diyar ta da tace ba diyar ta bace saboda girma da haske da ta qara sallamar sadiq ce ta katse mata tunani, kinga inna na bar mai kyau waje shida jidda fita tayi tare da ba sadiq hakuri ta ruqo jidda suka shigo har qasa sadiq ya gaishe da inna, fatuha tayi ma inna bayani aiko inna hannu biyu biyu ta amshe su dan ta yaba da hankalin sadiq jidda gani tayi ta samu kaka ta maqalewa inna da gudu fatuha fita daga gidan sadiq ya fita da ido bata zame ko ina ba sai gidan su fatsima tana Shiga ta shiga kwalla mata kira ba fatsima ba har gwago a rude suka fito saboda jin muryar da suka dade suna kewa, da gudu fatsima ta fada cikin fatuha tare da sakin kukan farin cikin murna ba'a magana d'akin ta ja fatuha sai dai yanzu fatsima duk tayi sanyi nan take taba fatuha labari ranar daurin auranta mijin ya rasu fatuha sai da ta tausaya mata sannan suka koma gida a tare lokacin inna har ta bama Sadiq masauki tare da kayan motsa baki jidda kuma na maqale da ita.

Kun san a tare suka wani da fatsima inda sadiq ke ta fushi fatuha ta barshi shi d'aya, basu suka rabu da fatsima ba sai gab da magrib lokacin baffa ya dawo shima cike da farin cikin inda ya dinga jan sadiq a jiki suna  taba hira Sama sama. inda inna ta cika mai fura da nono da tuwan dawa miyar kuka tasha manshanu sosai sadiq ya saki jiki yaci abincin.

Misalin karfe 8:30pm b'ayan sun d'awo d'aga masallaci sadiq ya wuce masaukin shi, b'ayan fatuha ta gama sa k'ayan bacci ta shirya jidda itama cikin nata sannan ta h'ada ma sadiq coffee kamar yadda ta saba a gida ta ja hannu angel suka wuce masaukin cikin sallama ta d'aga labilan d'akin suka shigo, amsawa yayi a taqaice ta aje mai coffee ya amsa tare da aika mata harara wasa hannuwanta biyu tasa a kunne alamar bada hakuri hira sukayi sama sama inda angel ke ta zuba qiriniya har bacci ya kwashe ta daukar ta fatuha tayi tana qoqarin fita sadiq ya masu pack a tare suka wuce d'akin fatuha.

*Washe gari*

Tunda safe fatuha ta tashi ta share tsakar gida tasses, ta hura icce ta dora koko tare da dumama tuwan jiya, ta juye a kwanan samira tana qoqarin fitowa d'aga kitchen din inna ta fito d'aga uwar daka washe da baki tana bin tsakar gida da kallo , alalai fatuha anyi hankali har qasa ta gaida inna ta amsa cikin fara'a sannan ta shige qurya ta fido jidda ta wanke ta tas ta shirya ta cikin jean n t-shirts masu kyau sannan itama ta shige kewaye tayi wanka, b'ayan ta fito ta shirya cikin riga da sket na lace red mai kyau sai yar huda d'ata murza da lipstick ba qaramin kyau tayi ba sannan ta dau kwanonin da tasama sadiq abinci ta nufi d'akin inna da ke surfa gero tace "Aiko dazu da sasafe tare suka fita da baffa ki gona" murmushi fatuha ta saki tace shine baffa beje dani ba ko? ta zuburo b'aki tare da shigewa ciki ta aje mai abincin tana fitowa ta ci qaro da fatsima washe da baki ta tarbeta kusan a tare su kayi kallaci sannan suka fita yawo ganin gari duk inda fatuha ta wuce sai antanka da irin kyanda tayi da natsuwar da ta qara haka aka rinqa Layin ganin ta inda ta rinqa baje tsaraba tana rabawa fatsima ko tasha tsaraba kamar ba gobe.

Kwana su biyu a kauye inda yan kauye ke cewa fatuha ta zo da larabawa sun sha yawo da sadiq har rafi sai da ta kai shi, da gona mai gari inda suke satar mangwaro a da, sosai ya ji d'adi kauyan ba dan k'adan ba,

Fatuha ce riqe da trolley tana rusa kuka ita bata komawa, sai da inna tayi da gaske sannan ta shige mota sadiq yasa trolley a boot tare da yima baffa shatara na arziqi  baffa duk yadda baffa yaqi amsa haka sadiq ya matsa mai amsa tare da samai albarka fatsima har da yar kwallata sannan suka dau hanyar kano.
********** ********** ******

Akwana atashi ba wuya wajan sallah fatuha dai ta fara zuwa makaranta inda aka sata jss1 sosai take maida hankali kuma tana gane karatun gashi Allah ya zuba mata qoqari  na ban mamaki, dan har tafi masu qoqarin ajin a yanzu a tare suke zuwa da jidda a yanzu jidda na primary 2 kusan duk makarantar su d'aya da su hanan da basma hakan ya qarasa suka shaqu duk inda kaga hanan to zakaga fatuha ko basma sosai suke maida hankali akan karatunsu.

K'amar yadda aka saba tashin su misalin karfe 3:30pm driven yayi parking suka bale murfi motar suka fito a tare, sanye fatuha take da uniform din ta riga mai dagwan hannu milk sai sket dark green dai -dai gwiwa sai dan qaramin hijab milk jidda kuma biri da wando milk a ciki rigar saman green kallo d'aya zaka masu kasan sun gaji likis tun a parlour jidda ta fara wurgi da jakar ta, ohno why this angel bari dai grandma ta fito ta Zane ki, sama nayi da ido ina tunanin wake wurgo wannan turancin kamar a mafarki ashe fatuha ce ohni salma😧, daukar bag din jidda tayi tana zunburo baki ta kai bedroom din ta,

Har fatuha ta shiga bedroom din ta ta fara cire mabalin rigar ta, ta tuna da ice cream din ta d'ake bedroom din sadiq cikin fridge da sauri ta fito ta haura upstairs a h'ankali ta bude part din ta shige  parlour ba kowa sai kamshi d'ake tashi, bedroom ta shige tare da nufar fridge din ganin Sadiq tsaye yana qoqarin cire rigar uniform din shi tace uncle waigowa yayi cikin smile yes dear um, ya naga ka d'awo yau da wuri haka uncle? na gama  aiki ne gobe da safe flight dina na zuwa  london ze tashi zani wani course ne ba zata ya zo min h'ada kayana na d'awo yi  , dan bata fuska tayi tare nufar fridge ta dau ice cream tana ta kunbure kunbure ta fice Sadiq ya bita da kallo.

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*

*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.CM

*69_70*

*_👏🏽Godiya gare ku mosayan ❤wannan novell din, ina jin d'adin y'adda kuk'e comments😍 ana mugun tare irin sosai din nan._*🤸🏽‍♀️🤸🏽‍♀️

*_wannan shafin naki ne Maimuna Lawal Allah ya bar zuminci har ya'ya da jikoki Ameen🤝._*

*F* atuha na shig'a bedroom din ta, ta aje ice cream din saman bedside drowe d'an gabaki d'aya ice cream din yafita ran ta, a duniya ba abinda ta tsana kamar mai kyau yayi nisa da ita, ita kanta har mamakin h'akan take jiki ba qwari ta ida cire school uniform din ta tare da shigewa bathroom ta sheqa wanka ta fito, b'ayan ta tsane jikin ta tabi da lotion mai kamshi tare da sanya black after dress din ta mai Stone's d'aure gashin kanta tayi kamar ganmo tare da Murza yar hod'a  da lipstick masha Allah fatuha ba qaramin kyau tayi ba, fitowa tayi d'aga bedroom din ta wuce na mom cikin sallama ta shiga mom Na tsaye gaban dress Mirror tana shirin da alama fita za tayi cikin fara'a ta amsa,tace "Mom fita zakiyi ne?", eh wallahi zani gidan ammi ne, d'ama yanzu nake cewa ko zaki raka ni ?dan murmushi fatuha tayi itama tana san zuwa wajan ammi din nan amma tunda ta zo sau biyu ta taba zuwa g'ashi tana san ganin basma, amma Assignment ba zai bari ba gashi malam anjima zaizo , mom kin manta yau Wednesday, oh haka fa na manta fa shafa next time munje kuma wallahi mom ina san zuwa basma har ce min take bani da kirki bana zuwa, ai ta fada duk zaryar da suke maki b'aki zuwa masu kema kin fara k'oyan h'alin uncle din naki, dan smile fatuha ta saki mai cike da jin d'adi ita dai duk abinda za'a

ce d'aga mai kyau yake so take ,mom ai baya san yawo uncle shiyasa. ke kuma sai biye mai kike ko? zuminci fa abin wasa bane mom ta ida zancan tana daukar handbag din ta kusan a tare suka fito, angel na zaune a parlour tana k'allan cartoon ganin grandma zata fita yasa ta tashi grandma zan biki please nop yau malam zaizo zuburo b'aki tayi gab'a tana sanyin kuka please grandma ki je dani,angel kiyi h'akuri grandma ta je kin ji? muma ranar Friday mun tafi kinji? d'aga kai jidda tayi b'adan taso, ba har b'akin mota suka raka ta suka juyo.

A dai-dai b'akin kofa suka ci qaro da sadiq sanye da 3 quarter black da white t-shirts da alama gym zashi, k'auda kai fatuha ta yi ala dole fushi take da sadiq, smile yayi tare da d'aga angel sama yana mata wasa tana d'ariya ko k'allan inda fatuha take beyi ba saboda ya lura yau rigima take ji, rabawa tayi ta gefan shi zata wuce ta cika tap qiris take jira ta fashe, ruqo hannu ta yayi h'akan yasa ta tsaya chak a wajan, ta kasa kwace hannu ta sai binshi da take da kallo, aje jidda yayi qasa yana aje ta kamar jira take tayi cikin gida da gudu, fisko fatuha yayi ta fado fafadan qirjin shi har tana jin bugun zuciyar shi lamo tayi a qirjin nashi, a hankali ya d'ago da habar ta yana kallan ta lumshe ido yayi tare da ware su kan fatuha cikin cool voice din shi yace "Fushin na menene?" um dan b'ata rai tayi tana qoqarin zamewa d'aga jikin shi tunda be san fushin me take ba, dan matse ta yayi da karfi ta saki yar qara, ta fara matsar kwalla, d'aga nace zanyi tafiya sai fushi fatuha 3 days fa kawai zanyi kin ji dear, turo b'aki tayi gaba ni ba fushi nake ba. to me kike? ba komai, ok tunda ba fushi kike ba please ki h'ada min k'ayana na rasa k'ayan da zansaka ki riga kin shagwaba uncle da yawa, dan zunburo b'aki ta kuma yi maicike da shagwaba, please karki ce bakiyi, zanyi mana promise ,promise good girl sannan ya mata pack a goshi ya fita.

B'ayan ta kamala h'ada mai k'ayan sannan ta kalli agogon d'ake mane a d'aki kusan karfe 4:30 sauri fitowa tayi d'aga part din ta wuce bedroom, d'auro alwala tayi tare da gabatar da sallah tana gamawa ta d'auko alQur'anin ta saboda yau laraba, alqur'ani kawai suke yi tare da janyo hijab din jidda tun a parlour ta zura mata suka fita a tare, lokacin har malam ya zo karatu suka yi sosai INSA malam y'a masu qarin bayin akan hadisi, sai gab da magrib suka shigo cikin gida, alwala k'awai suka gabatar tare da yin sallah b'ayan ta idar ta tsaya yin lazimi sannan tayima jidda assignment tayi nata kiran sallah isha ne ya tashe su bayan sun gabatar suka fito parlour sukayi dinner sannan kowa ya wuce bedroom din shi saboda sun gaji likis.

*Asuba ta gari*

Sallah asuba fatuha tayi tare da yin wanka, mai kawai ta shafa tare da sa yar gown iya karta gwiwa sannan ta fito bedroom din jidda ta shiga tayi mata wanka tare da shirya ta cikin unform sannan ta bar d'akin, kitchen ta shiga cikin sallama baba jinmai nata jefa bafanke gaishe ta fatuha tayi cikin fara'a ta amsa sannan suka gaisa da rabi'a, bude fridge tayi tare da fido yan cikin rago ta gyara ta d'aura kan wuta tare da zama tana taya su baba jinmai aiki ,sai hanata suke amma taqi sai da farfesun yayi ta juye a kola tare da h'ada coffee tasa a tray direct part din sadiq ta wuce ,a hankali ta murda k'ofar parlour ba kowa aje tray din tayi saman stool ta nufi bedroom din tsaye ta h'ango sadiq yana qoqarin sa necktie sallama tayi tare da gaisheshi cikin

fara'a ya amsa sannan ta qaraso ta amshi  necktie din tana samai bayan ta samai ta kalle shi uncle u looking so handsome tare da mai pack shima pack ya mata tare da daukar suit din shi black ya riqe a hannu ta ,janyo trolley din tayi suka fito parlour lokacin angel ta turo kofar tare da cewa "Daddy ta fada jikin sadiq" hug nata yayi d'an shagwabe fuska angel tayi daddy am going to miss u daddy, me to angel, amma daddy zaka min tsaraba teddys yes angel washe b'aki tayi tace "Anuty fatuha k'ema ki fadama daddy tsarabar da zaimaki" smile tayi tare da cewa "Duk abinda daddy yake so shi nake so yamin tsaraba" kallan ta sadiq yake me cike da so sannan ya zauna saman one star tray ta janyo ta zuba mai farfesun a ball saboda sadiq mutun ne mai san farfesu shiyasa fatuha kullun sai ta mai dan ta faran ta mai, feeding din shi farfesun ta fara yana sha angel itama tana bashi haka suka rinqa feeding din juna su cikin jin d'adi happy family sannan suka fito tray din fatuha ta kai kitchen ta wuce bedroom tasa uniform tare da d'auko school bag din ta.

Fitowar ta parlour yayi dai dai da fitowar su mom da abba cikin natsuwa ta gaishe su pack sadiq ya masu shida angel itama fatuha pack tayi ma mom suka fice a tare mota d'aya suka shiga da sadiq driver na ja sai da aka zo school din su yayi parking, gaba ki daya idanunta sukayi rau rau alamun zatayi kuka, suka bama sadiq hug suka fice yana kallan su har suka shige classes sannan driver ya ja mota sai airport.

Tunda sadiq ya tafi su angel suke missing nashi mom har mamaki suke, bata ko yar rahanan sun daina inkaga suna raha to sadiq ne ya kira waya haka shima can cike yake da kewar su inda yake jin kamar wata yayi ba kwana uku ba.

Akwana a tashi ba wuya wajan Allah yau kwana sadiq biyar kuma yaune ranar dawowar shi, zo ku ga murna wajan su fatuha sai zuba rawar kai ake mom sai janta take dan yanzu fatuha ta tashi d'aga yar aiki dan tuni sadiq ya yan'tata duk wani abinci da sadiq ke so fatuha ita da kanta ta mai sannan ta jera a dining area.

Bedroom ta shige tare da yin wanka, k'aya ta fido  ta rasa wanda zata sa duk wanda ta fido sai ta maida can ta h'ango wata red gown me Stone's, aje ta tayi a gefe ta tsantsara kawalliya ba qaramin kyau tayi ba sannan ta zura riga masha Allah indai maganar kyau ake fatuha ta kai, angel ce ta shigo da gudu itama sanye da gown pink tace "Anuty daddy ya dawo?" waigowa tayi tare da yin fari da ido suka fito a tare  shigowar sadiq parlour kenan su fatuha suka fito, k'allo sadiq ya bisu da shi mai cike da so rugawa su kayi a tare suka rungume sadiq d'ariya ya saki zaku ka dani ya fadi mom dake saukowa d'aga upstairs dariya ta saki tace "Sadiq kai da yaran ka kuna dirama wallahi" smile yayi tare da hug din mom in taqaice maku duk wani girki da fatuha tayi sai da sadiq ya ci inda yake ta binta da k'allo.

B'ayan ya hutu ya fido tsaraba yabama fatuha I phone 6 waya dadi da murna wajan fatuha ba'a magana jidda kuma Tap Apple mai shegyan kyau tare da new Teddy's h'aka suka dinqa zuba murna baki har kunne.

*2years letter*

Wata kyakyawar matashiyar budurwace da baza ta wuce 16 years ba ta rugu da gudu d'aga upstairs gudu take amma komai na jikin ta amsawa yake sanye take da 3 quarter pink sai riga white mai gajeran hannu ban gaje mutun da tayi ne ya sata tsayawa chak, cikin cool voice din ta tace "Sorry tare da rabawa ta gefan shi ta wuce" mutuwa tsaye majeed yayi yana binta da k'allo kafadar shi ya d'aga tare da sakin killing smile yabi stair's din da k'allo ,wai gowa ya kuma yi ko zai ga yarinyar amma ba alamar mutun. sama ya hau direct part din sadiq ya wuce a hankali ya murda handle din kofar ya shigo sadiq na zaune saman three star yana kallan news cikin sallama ya qaraso amsa mai sallamar yayi tare da aika mai harara wasa, sai yau zaka nemeni dan raini senses? dariya majeed ya saki tare da cewa "Sorry " ya zauna ni dai yanzu ba wannan zancan ba wacece na gani yanzu kamar d'aga part din nan ta fito? gaban sadiq ne ya yanke ya fadi qaqaro murmushi k'arfin h'ali yayi yace "Fatuha ce" *(Ohni salma🤦‍♀️ yaushe fatuha ta waye haka🙄lol)* ok majeed yace tare da cije lips dinsa  yana ayana  wasu abubuwa a ransa......hmmmm

*Muje zuwa fan's😘*

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏽‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best ★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

71_72

*_Ina matukar Godiya ga masoyan wannan novel, ina jin d'adin yadd'a kuke bani goyan b'aya wannan shafin naku ne duk masoyin CAPTAIN SADIQ._*

Ko da fatuha ta shig'a bedroom wayar tace ta hau ruri d'ake bedside drowe, cikin fara'a ta d'auka saboda sunan dak'e maqale a screen din wato hanan, daukar wayar tayi tare da kallan screen din kasancewar video call ne saman bed ta haye, "Hey yan'mata ya kike?" lafiya lau, wai yaushe zaki zo gida ne? ina so muje gidan ammi birthday din basma ya kusa, a ina za'ayi birthday din? inji fatuha kema kin san ba'a gida za'ayi ba, tap aikin san h'alin uncle wallahi ba ze barni naje ba, nifa matsala ta d'ake kenan wallahi, ke komai uncle komai . Eh naji din, yanzu dai ki mai dubara sai muje , gaskiya ina tsoran fushin shin kin manta randa muka je birthday din haoula kenan, wallahi ban manta ba ina sane ras, toh yayi kyau , amma fa zan shigo insha Allah .to shikenan ki gaishe min da angel tam ta katse wayar tare da kwaciyar ta.

Kamar yadd'a suka saba in suka h'adu haka suka rinqa zuba hira tare da yin musu, d'ama sun saba baza su taba rabuwa ba tare da sunyi musu ba, amma duk wannan hirar da su majeed suke tunanin fatuha na maqale a ransa, kiran sallah magrib ne ya tashe suka d'auro alwala suka wuce masallaci. basu suka dawo ba sai bayan sallah isha, ko da suka dawo majeed bai shiga gidan ba d'aga waje ya tsaya tare da jan motar shi yana tunanin ta inda zai bulo ma fatuha dan a gaskiya a shirye yake da ya aure ta kota halin kaka.......hmmm tofa🤭

Ko da sadiq ya shigo gidan mom na zaune a parlour ita da angel suna kallo, kallan parlour sadiq yayi tare da cewa "Angel ina Anuty?" tana bedroom Ddy. ok yace sannan ya haura sama ko minutes 5 bai yi ba ya dawo parlour tare da wuce wa bedroom din fatuha, zaune take saman bed tana assignment da laptop din ta sanye take da rigar bacci dai-dai gwiwa sai gashin k'anta data nanade shi k'amar ganmo,

Bud'e kofar da akayi ne yasa ta d'aga eye's ball's din ta ture laptop din tayi tana qoqarin tashi, harara sadiq ya aika mata, tare da cewa "Ina car Key's dina?" zuburo baki tayi gaba, wato kin rai nani ko? shine zan fita kika d'auke min car Key's kika boye . sorry uncle wallahi bana so ka fita ne ka sha rana, Kuma da ka fita ai da bakwan ka be same ka ba am sorry tasa hannuwata biyu a kunne Allah yaba ka hakuri. matsowa sadiq yayi kusa da ita har tana jin saukar numfashin shi ja mata baki yayi har sai da ta saki yar qara, tabe baki tayi tana shirin yin kuka kul kika min kuka wallahi yau sai kin kwana kina kneel down kuma kin san zan iya, bani Key's din, bedside drowe ta bude tare da zaro Key's din ta miqa mai tana qoqarin komawa

saman bed  janyo hannu ta yayi yana qare mata kallo ba qaramin kyau ta mai ba, lumshe ido yayi tare da ware su a k'anta murmushi fatuha ta saki mai cike da sakwanni iri-iri, rufe idanuwan ki kiga wani abu cikin sauri da zakuwa ta lumshe idanuwan ta wani dan kit ya fido tare da bude kit din oya bud'e wata hadadiyar sarkar gold ce wani irin ihu fatuha tasaki   tare da rungume sadiq ,shima rungume ta yayi tare da kai hannu saman gashin ta yawarware daurin data mai. cikin cool voice din shi yace "Gashin ki yafi kyau a h'aka" smile tayi tare da dagowa d'aga fafadan qirjin shi ta juya baya tana facing din dressing mirror tare da matsar da gashin ta gefe samata sarkar sadiq yayi ba qaramin kyau sarkar ta mata ba juyowa tayi tare da cewa "Uncle na gode" murmushi sadiq yayi nike da Godiya fatuha yau kusan shekarana uku bana tunanin, bana zuwa asibiti .murmushi ta saki tare da fita d'aga d'akin tana Isa parlour ta fad'a jikin mom, mom kin ga sarkar da uncle ya siya min? murmushi mom tayi irin nasu na manya amma dai gaskiya mun gode wannan kyau ta haka, lokacin yayi dai-dai da fito warshi d'aga bedroom din fatuha, angel ce ta turo baki tace "Daddy ni fa☹?" ja mata kumatu yayi tare da fido mata zube na gold ya sa mata murmushi ta saki love u daddy tare da yimai pack, lalai abin ma yar h'aka ce kenan? yaran ka kawai ka Sani ni Kuma ko oho mom ta fada, bayan mom yaje tare da zuro kanshi ta wuyan ta sorry mom next time ke zan siyawa kin ji Dan smile tayi sannan shima ya zagayu ya zauna sun dade suna hira sannan kowa ya wuce bedroom din shi.

Bangaran majeed ko cikin farin ciki ya koma gida, ko da umma ta tanbaye shi sai ce mata yayi ya kusa cika mata burin ta, murna ko har ba'a magana ko da ya koma d'akin shi da ya rintsa ido fatuha yake gani h'aka ya rinqa juyi saman bed har bacci barawo ya sace shi.

*Asuba ta gari*

Kasan Cewar yau weekend fatuha ta shiga kitchen tare da su baba jinmai suna aikin suna zuba hira kunsan a tare suka gama komai ,da misalin karfe 10:30 take tsaye gaban dining tana jera kayan abincin  cikin natsuwa  sallamar da kayi ne yasata dagowa tare da kallan kofar ta amsa a taqaice majeed ne ,sanye da shada ash tasha aiki sai kamshi yake zubawa dining area yanufo tare da yin smile fararan hakoran sa suka bayana. gyara murya yayi tare da cewa "Dama ashe kyawawa na aiki, gaskiya kamata yayi ace warhaka kina barcci ?" dagowa fatuha ta danyi a tunanin ta tuntuni ya shige ciki dan tasan kowaye a gidan saboda tasha ganin pics nashi dan murmushi ta saki cikin yauki tace "Suwaye kyawawa anan? naga dai ni kadai ce  ta ida zancan tana wai gawa"  murmushi ya Kuma saki a qaro na biyu fatuha kenan duk inda wata kyakyawa take kin kai ai, idanma b'aki sani bâ to y au zan fada miki."wallahi kin h'ada d'uk wani abun da ake nema wajen wata y'a mace, yar dariya ta saki wallahi yau uncle da tsoka ka zo gidan nan ko?yau dai  ranar tsokana ce? b'ata ida rufe b'akin ta ba sadiq ya shigo sanye da kayan gym din shi da alama d'aga gym ya d'awo, tunda yaga fatuha da majeed tsaye gabaki daya anurin fuskar shi ya sauya kamar an aiko mai da mutuwa daurewa yayi ya qaqaro murmushi my man yaushe ka shigo? wallahi yanzu na shiga bama kowa parlour sai wannan kyakyawar d'ake ta zuba aiki, Ni fa ko kallan ta ma kake ya Isa ya kosar da mutun d'aga yunwa .wani irin kallo sadiq ya wurga ma fatuha tare da bin kayan jikin ta da kallo gown ce mai kyau sai dai ya matseta duk

wata sura na jikin ta ana gani, ganin kallan da sadiq ya mata yasa ta barin parlour ba shiri ,majeed Kuma ya bita da kallo har yana cewa har zaki gudu? ko tanka mai ba tayi ba ta shige bedroom ,wai gowa yayi yana kallan sadiq ko lura da irin canjin da fuskar shi yayi bai lura ba ya haura upstairs, sadiq ya biyo bayan shi bayan sadiq yayi wanka ya shirya cikin kanana k'aya d'aya saba sawa suka fito tare da majeed dining area suka nufa, lokacin kowa ya halara gaishe da su mom sukayi a tare, tare da jan kojera suka zauna, a'a yau wanake gani a gidan ?dan murmushi majeed yayi yana sosa keya lalai ka kyauta, amma dai wuni ka zo yi? eh mana ki sha kurimin ki mom nama kusa kwaso  kayana na dawo nan da zama ya ida zancan sa yana sunkuyar da kan sa kasa, dariya mom da abba sukayi sadiq ko ya cika fam kamar zai fashe. janyo plate fatuha tayi zatayi saving din sadiq kamar yadda ta saba, sai da ta gama samin nashi zatayi saving din majeed ya fakaici idanuwan su ya riqe hannu  fatuha alamar kar ta zuba bata dau abin komai ba a tunanin hutar da ita yake son yi, ta zauna ta fara cin abincin ta sadiq ne yayi saving din   majeed da kanshi sannan suka fara break duk wata loma da majeed zai kai sai ya kai kallan shi ga fatuha idan sukayi ido hudu ya aika mata killing smile din shi duk wannan abun a qwayar idanuwa sadiq, cikin bacin rai ya ture plate din shi cike da masifa da zafin rai ya bar dining,  kallo su M'y suka  bishi da shi, fatuha ce tayi qoqarin tashi mom tace "Kyale shi ki cigaba da cin abincin ki ,tunda kika ga h'aka ba qaramin bata mai rai a qayi ba d'aga kafada majeed yayi tare da cewa " Indai sadiq ne ai ba yau ya saba haka ba" tunda sadiq ya bar dining fatuha ta rasa natsuwar ta ,tunda safe ta lura yake d'acin rai ta rasa dalili...hmm!

Ko da ya shiga part din shi a parlour ya zauna tare da lumshe ido wani irin bacin rai na damun shi ,Kuma  gashi ya rasa dalilin h'aka dafa shin da akayi ne yasashi ware eye's ball's din shi fatuha ce tsaye da plate a hannu ta cikin cool voice din tace "Uncle pls kayi break koma waye ya bata ma rai kayi hakuri ta ida zancan tare da zama tana miqa mika ma plate din" amsa yayi ya aje gefe yana kallan fatuha kamar me neman wani abu a fuskar ta can Kuma ya kauda kai tare da  cewa zanci kin ji tashi ki je bana san magana ne ya fadi yana lumshe ido fita ta zo yi lokacin yayi dai-dai da shigowar majeed  bigewa su kayi da junnan su, "ohshh majeed yace" haka ma fatuha tayi b'aya waigowa sadiq yayi yana kallan su wani miyau mai daci ya hadiya. dariya fatuha ta saki tare da cewa "Sorry , majeed" yace tunda nazo gidan nan kike bige ni, har saida kika bige zuciya ta. zaro ido waje fatuha tayi tana dan kule bakin ta tace "Kai uncle ba ruwana ta fadi zancan tana ida fita" ritse ido sadiq yayi tare da dunqule hannuwa shi yana mai da numfashi sama sama majeed ne ya dafa shi lumshe ido yayi a hankali yana janyo natsuwar shi zagayuwa yayi ya zauna , big man ina tunanin ka daina zafin ranan ashe har yanzu kana yi , wai ma waya bata ma rai haka big man?kawai am not in the mood shiyasa eyya sorry ko alura ce ta motso ya fadi yana dariyar shaqiyanci pillow kujera sadiq ya wurga wa majeed wallahi ka rainani kai naka bai tashi ba sai nawa, hhhh, kasan me ammi tace a'a tace wallahi next meeting in bamu fido mata ba wallahi auran dole zata mana. Ni dai nayi mata wallahi very soon zaku Santa ,amma kai ban sani ba kana nan kana ruwan idon nan naka, dan tab'e baki sadiq yayi tare da cewa "Ba wani ruwan ido har yanzu b'anga wadda ta d'ace d'ani bane shiyasa?ko za kayi bayani sanda ammi zata kwasoma yar kauye. Dariyar yake  sadiq yayi tare da daukar remote control...

*_Fan's ku d'anyi h'akuri da page din nan am to busy wallahi hakanan nayi page din dan farin cikin ku A na tare🤝_*

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏽‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www. Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.COM

73_74

*_this page is for you ummin mama_*

Sai baya'n sallah isha majeed ya bar gidan su sadiq, bayan sadiq ya d'awo party din shi ya wuce yana shiga yaci qaro da angel na kallo cartoon, murmushi ya saki tare da cewa, "Angel? ya qaraso kusa da ita ya zauna pack ya mata a goshi" daddy yes dear please gobe muje shan ice cream please, sweetheart gobe ba time kin ga akwai work amma inna dawo da wuri zamu je kijin angel ok daddy, daddy yau a nan zan kwana? ta ida zancan ta cikin shagwaba ." dan ja mata h'anci sadiq yayi tare da cewa "Yanzu kin zama big girlfa? ko baki gani yanzu fa u are 9 year old ko baki Sani baby?" smile tayi ta ce "Haka kuma nima daddy zan zama kamar Anuty fatuha ko idan na girma?" yes mana smile ta saki tare da yimai pack a goshi, good night daddy,

night angel.

Fatuha ce tsaye g'aban dressing mirror tana feshe jikin ta da turare da alama shirin bacci take, dan kayan bacci ne a jikin ta pink da ratsin green riga ce dai-dai gwiwa mai dan siririn hannu bayan ta kamala shirin ta, ta baza gashin ta har gadan bayanta. tsurawa dressing mirror din ido tayi tana tuna lokaci da sadiq yasa mata sarka lumshi ido tayi tare da daurasu a wuyan ta saurin ware ido tayi tare da cewa "U are very stupid fatuha tare da fita d'aga daki'n" bedroom din angel ta shiga lokacin har ta shirya cikin night dress din ta, tana kwace cikin blanket a hankali fatuha qaraso kusa da ita ware ido angel tayi kasan cewa bacci be dauke ta ba shafa gashin kanta fatuha tayi tace "Angel bakiyi bacci ba?" um yanzu na d'awo d'aga party din daddy, ok pack fatuha tayi mata tare da gyara mata blanket din ta kashe haskyan daki'n tare da rage gudun AC dakin ta fita.

Ko da fatuha ta fita kitchen ta shige ta had'a coffee sannan ta daura cup din a dan qaramin plate na glass ta haura saman, a hankali tayi knocking din part din come in aka ce hakan yasa fatuha bude kofar a hankali ta shigo. sanyi AC ke tashi da kamshi na musanman cikin fara'a ta qarasa shigowa sadiq na zaune saman three star sanye da night dress din shi maroon wando da riga, cikin natsuwa ta samu guri ta zauna saman one star, miqa mai glass cup din tayi amsa yayi yana smile kurba biyu zuwa uku yayi tare da kallan fatuha yace kamar akwai magana a bakin ki dan murmushi tayi tana wasa da yatsun hannu ta, ina jin ki! uncle dama dama um gobe ina so naje family house ne ni da hanan wani irin miyau sadiq ya h'ade take nan coffee din ya fara fita ranshi ,waza taje gani family house ?ya fada cikin zuciyar sa qara h'ada rai yayi kamar an aiko mai da saqwan mutuwa majeed ne ya fado mai a rai qara tsuke fuska yayi yace "Ban shirya ma zuwan ki family house ba" ya fadi a taqaice, uncle... d'aga mata hannu yayi yace "Yawon yayi yawa ina laifin kije gidan Anuty bilki, next time kin je can din ?ya fadi a taqaice dan murmushi tayi wanda iya karshi laban ta, saboda bata san gardama da sadiq ko dan karya bata rain shi, qoqarin fita ta take jiki ba qwari janyo ta sadiq yayi ta fado saman fafadan qirjin shi dariya fatuha ta saki tare da dan dukan qirjin shi cikin wasa, murmushi ya saki tare da d'ago da habarta yace " Na dauka kinyi fushi da uncle ne" dan bata fuska tayi tare da taba gefan fuskar shi tace ba " Ba Komai uncle,  Kuma dama can gidan Mami nayi niyar zuwa hanan ce tace na tanbaye ka muje can" qarewa lips din ta kallo sadiq yake har ta kai aya, sannan yace "Ok!" zame jikin ta d'aga na Sadiq tayi tace "Uncle bari na tafi" ok har kin fara jin bacci ne na dauka hira kika zo taya ni dan smile tayi wanda ya bayana fararan hakoran ta tace "Ba bacci nake ji ba kawai zan tafi ne saboda bana san dare yamin a nan ina jin tsora fita ni ka dai" d'aga gira sadiq yayi ok good night, har ta kai bakin kofa ta jiyu tace "Oncle zaka taya ni hira kafin bacci ya dauke ni?" yap ok zan kira ka video call ina je bedroom dawowa tayi ta mai pack a goshi sannan ta fice d'aga part din.

Ko da ta koma bedroom laptop din ta ta kuna, a bangaran sadiq ma haka kiran fatuha ya shigo laptop din sadiq dauk'a yayi yana kallan ta kamar tana gaban shi surutu ta cigaba da zuba

mai yana dariya har cikin shi na kulewa haka itama sosai sukayi hira inda sadiq yake jin bacin rain d'ake damun shi ya sauka har tayi bacci suna video call smile sadiq yayi ganin fatuha tayi bacci sannan shima ya kwanta, amma duk da haka ya kasa kashe laptop din kuma ya kasa kauda idanuwashi d'aga kanta yarasa dalilin da yasa inda yana tare da fatuha yake bata guri na musanman a zuciyar shi ita ka dai ce macan d'ake ganin murmushin shi fara'a shi da halin da wannan tunanin bacci ya dauke sadiq ba tare da ya kashe laptop din ba.

*Asuba ta gari*

Addu'a cike a bakin ta tashi tana miqa d'auke, laptop din ta dake saman bed take qoqarin sadiq ta hango kwance yana bacci , murmushi tayi tana qare ma kyakyawar face din shi kallo hannu ta kai kan screen din laptop din can kuma ta janye hannu ta daukar laptop din tayi ta aje saman sofa yadda zata riqa hango shi duk abinda take, toilet ta shige ta watsa ruwa tare da dauro alwala  daure da towel ta fito ko da ta fito lokacin sadiq shima ya tashi dan ba alamar shi ta cikin laptop din bed ba kowa sama ,cikin Sauri ta shirya tare da gabatar da sallah sket din makarantar ta ta janyo tasa tana gama sawa ta zura rigata tana bale ma balin riga ta, ta hango sadiq tsaye shima yana bale nashi dariya suka saki a tare morning uncle, morning too dear kin rigani tashi na riga ki shiryawa baki da sauri dan turo baki fatuha tayi dama can ka tashi idan ba hhhhh, kwarankwatsi ban tashi ba fashe wa fatuha tayi da dariya saboda tasan tsokanar ta yake kashe laptop din yayi domin ta qarasa shirya wa.

Kusan a tare suka fito lokacin angel har ta shirya cikin uniform din ta tana dining area ita da mom da abba cikn natsuwa suka qaraso, gaishe da su mom su kayi suka amsa a tare sannan suka ja kujera suka zauna saving din su fatuha tayi sannan suka fara break cikin jin dadi bayan sun kamala pack sukayi ma mom, abba ne yace lalai gidan nan ana gwada min banbanci jiya ina kallo mom dinku kukayi ma pack ni kuma ko oho ba komai zan rama dariya sukayi su duka tare da ba abba  hakuri kusan a tare suka fito mom ta rako su har bakin kofa yaran sadiq sai qamewa suke, shigewa motoci sukayi abba ya shige nashi suka bar harabar gidan.

Sosai yau sun sha karatu har da test sai da sukayi na history sosai fatuha ke maida hankalin ita da kawayan ta, Nana da Zara sune kawayan ta na makaranta kuma yan'yan masu kudi ne masu ji da Wayewa da yan matanci,   fatuha ko tun tana jss2 ta zana JSSCE saboda qoqarin da hazaqa yanzu haka SS2 take hanan na SS3 Basma kuma ta gama, Nana ce ta kalle ta bayan uncle ya fita daga class tace "Niko fatuha ina wannan uncle din nan naki mai kyau?" kallan ta fatuha tayi tare da aika mata harara ina ruwan ki da uncle dina, laaa fatuha yaushe kika zama haka? inji Nana, Zara d'ake gafe tace "Karki ga laifin ta wallahi ai dani ce fatuha da tuni na canza zani wallahi, hmmm ku wai me kuke nufi ban fa gane wannan hausar taku fatuha ta fada, hehe Zara da Nana sukayi lokaci daya, wallahi rainin hankalin nan namin dadi serious, to bari kiji ki zauna nan kwado ya maki kafa wallahi dani na sami damar ki da tuni na dama wallahi inji nana, ku dai Baku da aikin yi ni ina da . uncle kuma   nifa a matsayin wana na d'auke shi ba

komai ba Allahu Akbar bugu fatuha ta kaima Nana da Zara da littafin dake hannu ta.

Basma ce zaune ita da umma tana taya ta kwalema a d'akin ta, pic din sadiq ne ya fado hannu ta kai ta dauka ta kurawa pic din ido umma ce ta taba ta firgigit ta dawo d'aga duniyar tunani tare da qoqarin aje pic. din murmushi umma ta saki yar auta me ke damun kine kwana biyu naga duk kin rame kin zabge kamar mara lafiya hawayan d'ake maqale a idanuwan tane suka zubu tare da riqe hannu umma, tace " Umma na rasa me ke damuna tun zuwan da yaya sadiq yayi kwanaki na rasa meke damuna wallahi umma😭 ina son yaya sadiq ta ida zancan tare da rushewa da kuka" lalashin ta umma ta shigayi haba auta me abin kuka? share mata hawaye umma tayi duk wata mace mai lafiya dole taso sadiq saboda ya tare duk abinda mata ke so basma insha Allah zan taya ki da addu'a, idan sadiq alheri ne a gare ki Allah ya baki shi inko haka ta faru sai nafi kowa farin ciki da kinga sai a h'ada da naki dana majeed tunda shima jiya yake fada min ya samu wadda yake dai-dai tawa da ita , murmushi basma ta saki tare da fita d'aga dakin da gudu umma ta bita da kallo tayi murmushi irin nasu Na Manya.

Misalin karfe 12:30pm suka tashi dag'a makaranta kasan cewa yau friday angel na gefan ta suna jiran drive, hadadiyar motace baka ta faka gaban su fatuha kauda kai fatuha tayi kamar motar ba gaban su ta tsaya ba ,saboda glass din motar tinted ne ko na ciki ba'a gani zuge glass din akayi hakan yasa angel washe baki tare da cewa "Second daddy?" majeed sanye cikin uniform din shi na aiki murmushi ya saki bale murfin motar angel tayi kamar tana jira ta shige gaishe shi fatuha tayi a taqaice tare da cewa angel fito kin san driver ne zai zo daukar mu ta fada, murmushi majeed yayi yace "To ni zan d'auki kyankyawa yau na kai ta har gida dan tun dazu na kori driven" dan zaro ido waje fatuha tayi tace "Sokake uncle ya Mani fada KO?" ah uncle ba zai maki fada ba ai yasan ni zan dauke ku dan smile fatuha tayi wanda iyakar shi laban ta ta bude murfin motar ta shiga cikin natsuwa ya ja motar inda yana driven yana kallan fatuha ta cikin mirror .sai da ya zo dai dai b'akin geta yayi horn bala mai gadi ya bude mai geta parking yayi su fatuha suka fito tare da mai Godiya sai da suka shige cikin gida yayi ribas ya fita.

Shiga office din majeed sadiq yayi amma wayam ba majeed dan tabe baki yayi tare da fitowa d'aga office din ,da khaleed ya ci karo wanda shigowar shi yanzu kenan cikin fara'a sadiq ya tarbe shi, "Ah wai har yanzu majeed be dawo ba?" oh kama san da fita kenan eh munyi waya nace mai zanzo shine yace min yaje daukar baby shin d'aga school, baby sadiq ya maimai ta wallahi bansan sanda majeed zaiyi hankali ba wallahi mtww yaja Khaleed suka wuce office din shin.

Bayan sunyi lunch fatuha ta shirya tsaf cikin lace din ta maroon anmata dinkin bubu da lace din sosai kayan sun fido ta ,dan kwalin ta ta daura shi hawan hawan daurin ya zauna kamar gwagwaro janbaki ta shafa maroon da yar hod'a kwalliya sosai ta zauna ta tsantsara veil din ta

ta dauk'o white ta yafa masha Allah fatuha ba qaramin kyau ta zuba ba,

Tana fitowa parlour ta sami mom da majeed sunata zuba hira yana sanye da blue shad'a tasha aiki, cikin zazakar muryata fatuha tace "Mom zan je gidan mami, to, shikenan ki gaishe min da su zasu ji, majeed ne yayi karaf yace " Tunda tafiya nima zanyi bari na aje ki a can?" to! fatuha tace tare da yin gaba majeed yabi bayan ta shida kanshi ya bude mata murfin mota ta zauna  sannan ya bude ma kanshi ya shiga,

Ko 20 minutes basu dauka ba suka Isa gidan Anuty bilki, inda majeed keta janta da surutu har ta dan saki jiki da shi yana yin horn mai gadi ya bude ya shigo da motar tare da yin parking qoqarin fita d'aga motar take majeed yace "Baki ji ba, waigowa tayi sannan yace karfe nawa zaki koma gida?" da yama ta fada a taqaice. toh! shikenan zanzo daukar ki Godiya ta mai tare da shigewa cikin gidan.

Da gudu hanan ta rugo ta rungume ta kai amma naji dad'i wallahi, gaishe da mami tayi dake zaune parlour tana kallo sannan hanan ta ja ta bedroom suka baje suna ta zuba hira cikin jin dadi kai ka ce yan'uwane yadda suke nuna ma juna so sai kusan yama likis majeed ya zo gidan Anuty bilki inda ta rinqa zuba mai shaqiyanci shida sadiq sun raina ta basu san zuwa gidan ta sai da dalili shi dai  Sosa keya kawai yake sannan suka bar gidan suka nufo gidan,

Tunda sadiq ya kunno kai da motar sa driven na ja shi kuma yana b'aya, gyaran murya yayi yace "Wancan motar kamar ta majeed? yallabai ita ce ai dazu dana zo daukar fatuha, Hajiya tace min ai majeed ya kaita to qila sun dawo ne, wani qulolin bakin ciki ya tsayawa sadiq har yana jin ya qasa hadiye miyau kusan a tare suka shigo gidan sai da fatuha ta fito majeed shima ya fito murmushi fatuha ta saki tana ma majeed godiya, qoqarin bude kofar motar driver keyi yi sadiq yayi magana a tsawace karka bude ya fadi, shi kan shi driver  terere yayi da mamakin canji sadiq lokaci d'aya .zaunawa sukayi a motar sadiq na hango fatuha da majeed, har tayi gaba ta dawo ,oh na manta wayana a motar smile majeed yayi tare da bude motar ya curo wayar ya bata, tare da cewa gaskiya yadda na dako wayar nan ya kamata ki bani number ki dan murmushi tayi tace uncle number ta eh mana ya fada ko baza'a bani ba zan baka mana curo wayar shi yayi d'ake gaban aljihu ya bama fatuha ta rubuta mai number ta sannan ya shige mota ya bar harabar gidan.

Yana fita sadiq ya bude murfin motar cikin zafi, shigar fatuha bedroom ke da wuya taji an banka do  kofar cikin zafin rai waigowa tayi a dan tsorace fisgota sadiq yayi tare da fizge wayar da  dake hannu ta yayi wurgi da ita ta bigi Bango ta dawo a tarwatse ware ido fatuha tayi tare da sakin kuka, manna ta sadiq yayi da b'ango ya koma mata kamar zaki idanuwashi sunyi jawur kamar garwashi cikin kakausar murya yace "Waya baki izini fita gidan nan bada driver ba?" kuka fatuha ta kuma saki ko bakin magana ta rasa ganin bata da niyar bashi amsa yasa sadiq sakinta tare nufar kofar fita ya banka  ta da karfi ya fita hata mom dake part din ta sai da taji

bugun kofar da sadiq yayi. zame wa fatuha tayi awurin tare da sakin kuka, koda sadiq ya Shiga part nashi cili yayi da bribriefcase din shi saman three star ya zauna tare da lumshe ido yana maida numfashe sama sama. ware idanuwan shi yayi saboda d'aya rintse fatuha da majeed ya yake gani shafa ganshin kanshi yayi da hannu yace nooooooooo! Cikin d'aga murya........

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.co m/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_ speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.COM

75_76

Sai da fatuha taci kuka ta gaji sannan taja jiki ta hau saman bed ,tarasa dalilin da yasa mai kyau yake yin irin haka. kuka ta kuma rushewa da shi data tuna a irin yana yin data ganshi, h'aka ta riqa raira kuka kiran sallah magrib yasata tashi jiki ba qwari ta dauro alwala tare da gabatar da sallah. zaune tayi bisa daduma abin tausayi ganin tunanin be fishe ta yasa ta janyo AlQur'ani tana karantawa har aka kira sallah ishi bayan ta idar da sallah ta ja jiki ta koma bed ta cigaba da raira kukanta abin tausayi turo kofar da akayi ne yasata miqewa tana kallan kofar, angel ce tsaye bakin kofar qarasowa tayi d'akin tare da hawa saman bed din tace "Anuty waya saki kuka?" murmushi fatuha ta qaqaro wanda iya karshi laban ta tace "Ido nane ke ciwo" sorry Anuty , ki fito parlour kuyi dinner naji shuru ne baki fito ba ke da daddy shiyasa na biyo ki. dadday dai yace ya koshi, ko kema kin koshine? ta fadi zancan tana kallan fatuha Dan smile tayi tace ban qoshi ba ina nan zuwa naci komin dare fita jidda tayi d'aga daki'n fatuha ta cigaba da raira kukan ta har sai da kanta ya fara ciwo, ganin bame lalashin ta yasa tayi shuru tana

sauke ajiyar zuciya bacci barawo ya sace ta.

Bangaran sadiq in ban da juyi saman bed ba abinda yak'e da kyar ya samu ya rintsa.

*Asuba ta gar'i*

Ko da fatuha ta tashi jiki ba qwari tayi sallah sannan ta qara komawa ta kwanta saboda kanta dake mata ciwo. Kuma taci sa'a yau weekend ba ita ta tashi ba sai karfe 11:30pm ware ido tayi tare da kallan agogan d'ake makale a daki'n, cikin sauri ta mike tare da shiga toilet ta watsa ruwa. ko da ta fito mai kawai ta murza sai after dress d'ata zura parlour ta fito ba kowa dining area ta wuce tare da bude kulolin dak'e jere wanjan chpis ne da farfesun yan'ciki zuba wa tayi a plate tare da had'a ruwan tea sannan ta zauna. loma biyu zuwa uku tayi ta ture plate din dan kwata kwata bata jin d'adi abincin.

Babban abinda ke daure mata kai ta rasa laifin da tayi ,yanke shawarar zuwa bama sadiq hakuri tayi duk da bata san laifin data mai ba dan bata iya jurewa wannan horan. tashi tayi tare da kwashe kwanikan ta kai kitchen sai da suka dan taba hira da su baba jinmai sannan ta fito.

Direct part din Sadiq ta wuce a hankali ta murda handle din kofar tare da shigowa cikin sallama zaune sadiq yake saman two star da laptop gaban shi kallo d'aya zaka mai kasan babu annuri a fuskar shi. dogo kai yayi ya kalli fatuha tare da lumshe ido ya kauda kai yace "Just leave me alone" sadiq ya fada a tsiwace tare da tatara takadun d'ake gaban shi da laptop din ya shige bedroom tare da buga kofar da karfi. kuka fatuha ta saki tare da fita d'aga part din da gudu jin ta fita yasa sadiq jinji Na da kofar bedroom ya lumshe ido.

Da gudu ta wuce mom a parlour ta shige daki saman bed ta fada tare da sakin kuka mai cinrai. kuka taci ta gaji, mom d'ake parlour bin fatuha tayi da kallo tana mamakin mai ya h'ada su, koma dai minene ai sun saba zasu shirya ne amma abin mamaki basa kai haka kauda zancan mom tayi tare da cigaba da kallan ta, duk yinin yau babu wanda yaci abinci cikin su fatuha inban da kuka ba abinda take shi ko sadiq sai baki'n rai dayake fama da shi,

Iskace mai sanyi da ke ta kadawa da alama ruwa za'ayi saboda damuna data fara shigowa. qara cida ce kawai ke tashi b'akin widow sadiq ya tsaya a hankali ruwa ke saukowa kallan ruwan yake yanda yake saukowa da karfi a wannan karan lumshe ido yayi tare da ware su, ya koma saman bed ya kwanta bangaran fatuha tunda aka fara ruwa tak'e lilibe cikin blanket

Gaba ki d'aya yini yau ba wanda yayi ma wani magana  cikin fatuha da sadiq, horan dak'i sukayi wa kansu ba tare da sun nemi abin sama bakin sallatin su ba , har bacci ya kwashe su.

Shiryawa yake cikin manyan kayan shi kasan cewar yau zasu je family meeting, fatuha ce ta fado mai a rai kawar da tunanin yayi dan har yanzu be huce ba ko yana hucewa sai ya d'awo dag'a meeting cikin Isa yake saukowa d'aga upstairs ,lokacin har su mom sun shirya suna parlour zaune suna jiran fitowar sadiq da fatuha ganin sadiq ya sako yasa mom cewa angel, kira Anuty mu wuce , ko da angel ta shiga d'akin kwance ta samu fatuha qudindine cikin blanket , fitowa tayi da sauri d'aga bedroom din tace "Grandma Anuty bacci take" toh fa! amma ai fatuha bata kai haka tana bacci .shiga d'akin mom tayi tare da qarasawa wajan bed din fatuha tace a hankali, a hankali fatuha ware idanuwan ta da suka yi nauyi saboda tsabar kuka, kallanta mom tayi tace "Mike damun kin fatuha?" dafe kai tayi tare da cewa mom "Kai nane ke ciwo" eyya sorry dama meeting zamu tunda b'aki jin dad'i ki zauna kawai a gida to kawai tace tare da shigewa blanket, sannan mom ta fita ko da ta fita sadiq ta aika ma harara tare da ayana ma ranta in sun dawo zatayima abin tufkar hanci.

Katafarin parlour su da aka ware danyi meeting suke zaune, tunda sadiq ya shigo gaban shi ke yankewa yana faduwa yarasa dalilin h'akan addu'a da ke bakin shi ya furta dan samun na tsuwa. majeed ya shigo tare da zama gefen sadiq tare da miqa mai hannu suka gaisa da kyar sadiq ke danne zuciyar shi kan majeed tare da bata hakuri, Alhaji babba ne ya shugo sanye da babba riga tasha aiki sai sheqe kayan suke, cikin sallama ya shigo tare da zama a kujerar sa ta musanman wato kakan su sadiq, ammi na gefan shi ta dama sauran jikoki da iyaye na gefe da yan uwa .

Taro ya fara budewa da addu'a sannan ya fara jawabin cikin natsuwa kamar yadda kuka Sani Inayi maku murna da zuwa wannan taro na qara dankwan zuminci. tare da yi maku albishir da abubuwa da yawa na farin cikin a wannan shekara mun samu kimani naira billion dari cikin riba kasuwancin mu sannan mun talafawa gidan marayu tare da asibitoci sannan anbiyawa mutun 30 kujera maka , kabara wajan ya dauka tare da hamdala, sannan Kuma ga muhimiyar sanawa ita ce majeed ya samu matar da zai aura, sadiq dake zaune saman kujera gaban shi ya qara yankewa ya fadi, muryar Alhaji babba ce ta dawo mai dodan kunne, ba kowa bace sai yar gidan ibrahim wanda yake ruqu fatuha Kuma har gidan iyayan ta muje munyi bin cike ashe ma akwai sanaya a tsakanin mu Kuma sun aminci sun bada. wani irin gumi ne ya karyo ma sadiq mai matsanan cin zafi take nan ya fara ji wutar shi na dauke wa ba sadiq ba hata mom sai da ta girgiza da wannan furin cin, wata kalmar ya qara jefowa a karo na biyu sadiq Kuma mun yanke shawarar bashi kanwar sa basma tare da sharadi idan har ya kawo wadda yake so nan da sati daya kamin asa biki to za'a basa dama ya auri wadda yake so basma ma kuma ta hakura zabin shi wannan shine hukuncin dana yanke. sannan ya kalli baban basma Alhaji khabiru cika mana taro da addu'a.

Gabaki d'aya parlour juyawa sadiq yake da kyar ya samu ya miqe, majeed in ban da washe baki da yake ba abunda yake dan ko ta kan sadiq bai bi ba haka basma baki har kunne sadiq ne ka dai da mom basu farin ciki sai hanan. yana fitowa d'aga parlour parking space ya nufa

cikin sauri ya bale murfin motar ya shiga da gudu ya fisgi motar ya harba kan titi gudu yake tsulawa kamar zai tashi sama yana isowa gida ya danna horn bala mai gadi na bude mai geta yace "Subhanalal " saboda yadda sadiq ya shigo da motar yana shigowa ko dai-daita parking ya kasa ya bale murfin motar ya fito cikin sauri ya wuce part din shi yana shiga ya zame bakin kofa tare da dafe kanshi🤦‍♀️ maganar Alhaji babba na dawo mai. mikewa yayi ya shige bedroom saboda har yanzu bai dai na ganin jiri ba, wani irin kuka sadiq ya saki mai tsuma zuciyar mai saurare kneel down yayi a wurin can Kuma ya mike yashiga fatali da kayan d'akin kamar saban kamu. sai da yayima d'akin fata fata ya shiga toilet da kayan jikin shi sakar ma kanshi shower yayi, maganganun Alhaji babba namai yawo a brain wata zuciyar tace "Wato jiya fatuha tabama majeed izinin turawa gidan su?" hadeye  kukan da yake yayi tare da fitowa sharkaf ya zauna kasan carpet be damu da kayan dake jikin shi ba.

Bangaran fatuhu ko tunda su mom suka fita gabanta ke faduwa, ta rasa dalilin haka ta rasa suku nin ta jin an bude kofar d'akin ya sata waigowa mom ce tsaye bakin kofa murmushi fatuha ta saki wanda iya karshi laban ta, mom har kun dawo da wuri haka? eh tace tana qoqarin danne damuwar ta tare da qarasa shigowa zama tayi kusa da fatuha cikin sanyi murya tace "Fatuha gobe da safe ki shirya zaki je wudil baffa nasan ganin ki?" sannan ta tashi ta fita kallo fatuha tabi mom da shi take nan jikin ta ya haubari da tsoro tsoro ko dai uncle ya kai qarata kauda zancan tayi tasan ma ba zanyi hak'a ba ,amma zuciyar ta na cike da tanbayoyi, ganin bata da amsa ta hakura.

Ola sadiq ya kira a waya bugu d'aya zuwa biyu ya dauka ina san ganin ka sadiq ya fada a taqaice ,ko da ola ya zo ganin Watsin da akayima dakin tsoro ya bashi kallan sadiq yayi da magana a bakin shi ganin fuskar sadiq ba annuri yaja baki ya tsuke. nuni ya mai d'aya gyara d'akin shi Kuma ya shigida saman sofa hawaye daya na bin daya kamar ba soja ba,

Gabaki d'aya gidan Alhaji Ibrahim ba wanda ya rintsa, d'aga angel sai abba ne kawai suka samu bacci bangaran sadiq inban da kukan zuci ba abinda yake, fatuha tunanin me yasa baffa ke neman ta? take ko dai inna ce ta rasu? ba'a San fada mata girgiza kai kawai  tayi.

Tunda safe fatuha ta tashi ta shirya cikin riga da sket din ta na atamfa yellow mai ratsin white a jiki masha Allah kayan sun hauta sai fuskar fayau, bayan ta kamala ta fito parlour cikin natsuwa ta gaida mom da abba d'ake ta break angel na gefe itama ganin bata ga sadiq ba yasa gaban ta ya qara faduwa a karo na biyar jiki ba qwari ta zo ta hada tea kurba biyu zuwa uku ta aje , mom ce tace "Fatuha har kin koshi?" eh mom dama in zan yi tafiya bana wani cin abinci to mom tace , sannan ta qara da cewa ga driver nan zan h'ada ku da shi in ya kai ki yau zai maido ki ki gaida mutun gida sannan inkin Isa ki kira ni ki fada min. lagwabe kai fatuha tayi tace "Wallahi mom jiya wayar ta lalace" garin yaya? fadowa tayi d'aga dressing mirror ta dauke, eyya to bari na baki baby Nokia in kin dawo a sake wata to fatuha tace tare da shi ga daki ta dauko sim din ta miqa mata wayar .mom tayi ta zura sim din ciki har ta kai bakin kofa ta dawo tare da haurawa sama part din sadiq ta nufa a hankali ta murda handle din kofar taji Kule gam tsoro ne

ya kamata amma ba yadda ta iya haka ta dawo tare da yima mom sallama angel ko sai rigama take sai tabi fatuha mom ta hana.

Shigewa mota tayi driver ya harba da su kan titi cikin dan qanqanin lokaci suka Isa wudil. cikin kwatan can fatuha har driver ya kawo ta gidan fitowa tayi a hankali tana qare ma gidan su kallo gabaki daya gidan ya canza a yadda ta San sa mamaki ne ya bayana a fuskar ta qarasa Shiga tayi cikin sallamah inna d'ake parlour ce ta fito tare da yima fatuha maraba da zuwa duk da fatuha ba'a cikin jin dadi take ba bata yadda inna ta gane ba, parlour ta janta suka Shiga har yanzu mamaki ne shifide a fuskar ta tace cikin sanyin murya "inna waya gyara gidan nan?" murmushi inna ta saki ina yaran nan sadiq wallahi shi ya mana abin arzikin nan murmushi fatuha ta saki mai cike da jin dadi baffa ne ya yaye labilan ya shigo har qasa fatuha ta tsugunna ta gaisheshi amsa mata yayi a taqaice sannan ya samu wuri ya zauna. itama fatuha qasa tayima kanta mazauni tana jiran jawabin baffa gyaran murya baffa yayi tare da cewa "Fatuha nasan cewa na maki laifi amma kiyi hakuri ina fatan bazaki watsamin qasa a ido ba? ina fata bazaki bani kunya ba ?duk wannan jawabin da baffa keyi kan fatuha na qasa ,d'ago kai tayi tace "insha Allah baffa bazan baka kunya ba" yauwa diyar albarka, dama dan uwan sadiq ne ya zo neman auran ki tare da iyayan shi jiya da dare, mukanmu munyi mamaki da wannan zuwa fatuha ganin halacin da zura'a suka mana gashi nasan baban yaran hakan yasa na aminсe dan na lura yaran mai natsuwa ne Kuma dama neman auran budurwan anso iyayanta su zaba mata miji Na gari da wannan nayi la'akari na zaba maki majeed a matsayin miji. dagowa fatuha tayi a razane dan sai yanzu ta fahimci inda aka dosa idanuwan ta tap da kwalla suka ciko nan take hawaye suka fara anbaliya a fuskar ta me yasa mai kyau zai mata irin wannan horan me yasa fita tayi d'aga parlour da gudu ta fada dakin inna ta saki kuka mai tsanani mai ban tausayi, inna ce ta dafa bayan ta tana lalashin ta, haba fatuha bai kamata ki watsawa muta nan qasa a ido ba Kuma kowani mutun da qadarar dake zuwa mashi .fatuha idan dai majeed alkairi ne a gare ki Allah ya tabatar haka inna ta riqa bitana tausar fatuha har ta samu tayi shuru tana sakin ajiyar zuciya ko ruwa kasa sha fatuha tayi sai bayan sallah la'asar suka dau hanyar kano wayar tace dake cikin jaka taji qara message sai a lokacin ta tuna da mom tace ta kira ta curo wayar tayi ta karanta message din kamar haka,

_Sister ina matukar farin cikin Sanar d'ake yau buri na ya cika, tun jiya nake qoqarin kiran ki wayar takin Shiga ba wani albishir bane ila yaya sadiq ya kusa zama miji a gare ni ,sannan ina taya ki murnar zama inlow a gidan mu cikin family din mu d'aga basma._

Wani irin kuka fatuha ta saki mai cinrai ko ida karanta sakwan ba tayi ba wayar ta fadi jikinta in banda bari ba abin da yake. ashuru driver ya juyo haba fatuha komai yayi zafi maganin shi Allah bai kamata kina kuka irin h'aka ba ,duk wannan magana da ashuru yake fatuha ba jin shi take ba kalmar sadiq yazama miji Na kawai qwawalwarta ke fada mata har suka iso garin kano fatuha na sheka kuka kamar ranta zaifi ta, ko da ashuru yayi horn aka bude geta kafin ya tsada motar ta bale murfin motar ta fita da gudu sadiq da yanzu ya ji Qarar shigowar mota d'aga labila yayi tare da koma ya cigaba da zarya a bedroom din.

Da gudu fatuha ta haura sama ko kallan muta nan parlour batayi ba part din sadiq ta wuce

Allah ya bata sa'a tana bude kofar ya bude, ganin bata gashin a parlour ba yasa ta shigewa bedroom da gudu . fadawa tayi jikin sadiq tare da sakin kuka mai cinrai ,rintse ido sadiq yayi yana jin yadda fatuha ke sheqa kuka cikin sarkewar murya tace "Uncle dan Allah karkamin wannan horan wallah bazan iya dauka ba, dama ace mafarki nake abin da nake ji ba gaske bane ta ida zancan tare da sakin saban kuka ta zame kasa.......

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.co m/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_ speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.COM

75_76

Sai da fatuha taci kuka ta gaji sannan taja jiki ta hau saman bed ,tarasa dalilin da yasa mai kyau yake yin irin haka. kuka ta kuma rushewa da shi data tuna a irin yana yin data ganshi, h'aka ta riqa raira kuka kiran sallah magrib yasata tashi jiki ba qwari ta dauro alwala tare da gabatar da sallah. zaune tayi bisa daduma abin tausayi ganin tunanin be fishe ta yasa ta janyo AlQur'ani tana karantawa har aka kira sallah ishi bayan ta idar da sallah ta ja jiki ta koma bed ta cigaba da raira kukanta abin tausayi turo kofar da akayi ne yasata miqewa tana kallan kofar, angel ce tsaye bakin kofar qarasowa tayi d'akin tare da hawa saman bed din tace "Anuty waya saki kuka?" murmushi fatuha ta qaqaro wanda iya karshi laban ta tace "Ido nane ke ciwo" sorry Anuty , ki fito parlour kuyi dinner naji shuru ne baki fito ba ke da daddy shiyasa na biyo ki. dadday dai yace ya koshi, ko kema kin koshine? ta fadi zancan tana kallan fatuha Dan smile

tayi tace ban qoshi ba ina nan zuwa naci komin dare fita jidda tayi d'aga daki'n fatuha ta cigaba da raira kukan ta har sai da kanta ya fara ciwo, ganin bame lalashin ta yasa tayi shuru tana sauke ajiyar zuciya bacci barawo ya sace ta.

Bangaran sadiq in ban da juyi saman bed ba abinda yak'e da kyar ya samu ya rintsa.

*Asuba ta gar'i*

Ko da fatuha ta tashi jiki ba qwari tayi sallah sannan ta qara komawa ta kwanta saboda kanta dake  mata ciwo. Kuma taci sa'a yau weekend ba ita ta tashi ba sai karfe 11:30pm ware ido tayi tare da kallan agogan d'ake makale a daki'n, cikin sauri ta mike tare da shiga toilet ta watsa ruwa. ko da ta fito mai kawai ta murza sai after dress d'ata zura parlour ta fito ba kowa dining area ta wuce tare da bude kulolin dak'e jere wanjan chpis ne da farfesun yan'ciki zuba wa tayi a plate tare da had'a ruwan tea sannan ta zauna. loma biyu zuwa uku tayi ta ture plate din dan kwata kwata bata jin d'adi abincin.

Babban abinda ke daure mata kai ta rasa laifin da tayi ,yanke shawarar zuwa bama sadiq hakuri tayi duk da bata san laifin data mai ba dan bata iya jurewa wannan horan. tashi tayi tare da kwashe kwanikan ta kai kitchen sai da suka dan taba hira da su baba jinmai sannan ta fito.

Direct part din Sadiq ta wuce a hankali ta murda handle din kofar tare da shigowa cikin sallama zaune sadiq yake saman two star da laptop gaban shi kallo d'aya zaka mai kasan babu annuri a fuskar shi. dogo kai yayi ya kalli fatuha tare da lumshe ido ya kauda kai yace "Just leave me alone" sadiq ya fada a tsiwace tare da tatara takadun d'ake gaban shi da laptop din ya shige bedroom tare da buga kofar da karfi. kuka fatuha ta saki tare da fita d'aga part din da gudu jin ta fita yasa sadiq jinji Na da kofar bedroom ya lumshe ido.

Da gudu ta wuce mom a parlour ta shige daki saman bed ta fada tare da sakin kuka mai cinrai. kuka taci ta gaji, mom d'ake parlour bin fatuha tayi da kallo tana mamakin mai ya h'ada su, koma dai minene ai sun saba zasu shirya ne amma abin mamaki basa kai haka kauda zancan mom tayi tare da cigaba da kallan ta, duk yinin yau babu wanda yaci abinci cikin su fatuha inban da kuka ba abinda take shi ko sadiq sai baki'n rai dayake fama da shi,

Iskace mai sanyi da ke ta kadawa da alama ruwa za'ayi saboda damuna data fara shigowa. qara cida ce kawai ke tashi b'akin widow sadiq ya tsaya a hankali ruwa ke saukowa kallan ruwan yake yanda yake saukowa da karfi a wannan karan lumshe ido yayi tare da ware su, ya koma saman bed ya kwanta bangaran fatuha tunda aka fara ruwa tak'e lilibe cikin blanket

Gaba ki d'aya yini yau ba wanda yayi ma wani magana  cikin fatuha da sadiq, horan dak'i

sukayi wa kansu ba tare da sun nemi abin sama bakin sallatin su ba , har bacci ya kwashe su.

Shiryawa yake cikin manyan kayan shi kasan cewar yau zasu je family meeting, fatuha ce ta fado mai a rai kawar da tunanin yayi dan har yanzu be huce ba ko yana hucewa sai ya d'awo dag'a meeting cikin Isa yake saukowa d'aga upstairs ,lokacin har su mom sun shirya suna parlour zaune suna jiran fitowar sadiq da fatuha ganin sadiq ya sako yasa mom cewa angel, kira Anuty mu wuce , ko da angel ta shiga d'akin kwance ta samu fatuha qudindine cikin blanket , fitowa tayi da sauri d'aga bedroom din tace "Grandma Anuty bacci take" toh fa! amma ai fatuha bata kai haka tana bacci .shiga d'akin mom tayi tare da qarasawa wajan bed din fatuha tace a hankali, a hankali fatuha ware idanuwan ta da suka yi nauyi saboda tsabar kuka, kallanta mom tayi tace "Mike damun kin fatuha?" dafe kai tayi tare da cewa mom "Kai nane ke ciwo" eyya sorry dama meeting zamu tunda b'aki jin dad'i ki zauna kawai a gida to kawai tace tare da shigewa blanket, sannan mom ta fita ko da ta fita sadiq ta aika ma harara tare da ayana ma ranta in sun dawo zatayima abin tufkar hanci.

Katafarin parlour su da aka ware danyi meeting suke zaune, tunda sadiq ya shigo gaban shi ke yankewa yana faduwa yarasa dalilin h'akan addu'a da ke bakin shi ya furta dan samun na tsuwa. majeed ya shigo tare da zama gefen sadiq tare da miqa mai hannu suka gaisa da kyar sadiq ke danne zuciyar shi kan majeed tare da bata hakuri, Alhaji babba ne ya shugo sanye da babba riga tasha aiki sai sheqe kayan suke, cikin sallama ya shigo tare da zama a kujerar sa ta musanman wato kakan su sadiq, ammi na gefan shi ta dama sauran jikoki da iyaye na gefe da yan uwa .

Taro ya fara budewa da addu'a sannan ya fara jawabin cikin natsuwa kamar yadda kuka Sani Inayi maku murna da zuwa wannan taro na qara dankwan zuminci. tare da yi maku albishir da abubuwa da yawa na farin cikin a wannan shekara mun samu kimani naira billion dari cikin riba kasuwancin mu sannan mun talafawa gidan marayu tare da asibitoci sannan anbiyawa mutun 30 kujera maka , kabara wajan ya dauka tare da hamdala, sannan Kuma ga muhimiyar sanawa ita ce majeed ya samu matar da zai aura, sadiq dake zaune saman kujera gaban shi ya qara yankewa ya fadi, muryar Alhaji babba ce ta dawo mai dodan kunne, ba kowa bace sai yar gidan ibrahim wanda yake ruqu fatuha Kuma har gidan iyayan ta muje munyi bin cike ashe ma akwai sanaya a tsakanin mu Kuma sun aminci sun bada. wani irin gumi ne ya karyo ma sadiq mai matsanan cin zafi take nan ya fara ji wutar shi na dauke wa ba sadiq ba hata mom sai da ta girgiza da wannan furin cin, wata kalmar ya qara jefowa a karo na biyu sadiq Kuma mun yanke shawarar bashi kanwar sa basma tare da sharadi idan har ya kawo wadda yake so nan da sati daya kamin asa biki to za'a basa dama ya auri wadda yake so basma ma kuma ta hakura zabin shi wannan shine hukuncin dana yanke. sannan ya kalli baban basma Alhaji khabiru cika mana taro da addu'a.

Gabaki d'aya parlour juyawa sadiq yake da kyar ya samu ya miqe, majeed in ban da washe

baki da yake ba abunda yake dan ko ta kan sadiq bai bi ba haka basma baki har kunne sadiq ne ka dai da mom basu farin ciki sai hanan. yana fitowa d'aga parlour parking space ya nufa cikin sauri ya bale murfin motar ya shiga da gudu ya fisgi motar ya harba kan titi gudu yake tsulawa kamar zai tashi sama yana isowa gida ya danna horn bala mai gadi na bude mai geta yace "Subhanalal " saboda yadda sadiq ya shigo da motar yana shigowa ko dai-daita parking ya kasa ya bale murfin motar ya fito cikin sauri ya wuce part din shi yana shiga ya zame bakin kofa tare da dafe kanshi🤦‍♀️ maganar Alhaji babba na dawo mai. mikewa yayi ya shige bedroom saboda har yanzu bai dai na ganin jiri ba, wani irin kuka sadiq ya saki mai tsuma zuciyar mai saurare kneel down yayi a wurin can Kuma ya mike yashiga fatali da kayan d'akin kamar saban kamu. sai da yayima d'akin fata fata ya shiga toilet da kayan jikin shi sakar ma kanshi shower yayi, maganganun Alhaji babba namai yawo a brain wata zuciyar tace "Wato jiya fatuha tabama majeed izinin turawa gidan su?" hadeye kukan da yake yayi tare da fitowa sharkaf ya zauna kasan carpet be damu da kayan dake jikin shi ba.

Bangaran fatuhu ko tunda su mom suka fita gabanta ke faduwa, ta rasa dalilin haka ta rasa suku nin ta jin an bude kofar d'akin ya sata waigowa mom ce tsaye bakin kofa murmushi fatuha ta saki wanda iya karshi laban ta, mom har kun dawo da wuri haka? eh tace tana qoqarin danne damuwar ta tare da qarasa shigowa zama tayi kusa da fatuha cikin sanyi murya tace "Fatuha gobe da safe ki shirya zaki je wudil baffa nasan ganin ki?" sannan ta tashi ta fita kallo fatuha tabi mom da shi take nan jikin ta ya haubari da tsoro tsoro ko dai uncle ya kai qarata kauda zancan tayi tasan ma ba zanyi hak'a ba ,amma zuciyar ta na cike da tanbayoyi, ganin bata da amsa ta hakura.

Ola sadiq ya kira a waya bugu d'aya zuwa biyu ya dauka ina san ganin ka sadiq ya fada a taqaice ,ko da ola ya zo ganin Watsin da akayima dakin tsoro ya bashi kallan sadiq yayi da magana a bakin shi ganin fuskar sadiq ba annuri yaja baki ya tsuke. nuni ya mai d'aya gyara d'akin shi Kuma ya shigida saman sofa hawaye daya na bin daya kamar ba soja ba,

Gabaki d'aya gidan Alhaji Ibrahim ba wanda ya rintsa, d'aga angel sai abba ne kawai suka samu bacci bangaran sadiq inban da kukan zuci ba abinda yake, fatuha tunanin me yasa baffa ke neman ta? take ko dai inna ce ta rasu? ba'a San fada mata girgiza kai kawai tayi.

Tunda safe fatuha ta tashi ta shirya cikin riga da sket din ta na atamfa yellow mai ratsin white a jiki masha Allah kayan sun hauta sai fuskar fayau, bayan ta kamala ta fito parlour cikin natsuwa ta gaida mom da abba d'ake ta break angel na gefe itama ganin bata ga sadiq ba yasa gaban ta ya qara faduwa a karo na biyar jiki ba qwari ta zo ta hada tea kurba biyu zuwa uku ta aje , mom ce tace "Fatuha har kin koshi?" eh mom dama in zan yi tafiya bana wani cin abinci to mom tace , sannan ta qara da cewa ga driver nan zan h'ada ku da shi in ya kai ki yau zai maido ki ki gaida mutun gida sannan inkin Isa ki kira ni ki fada min. lagwabe kai fatuha tayi tace "Wallahi mom jiya wayar ta lalace" garin yaya? fadowa tayi d'aga dressing mirror ta dauke, eyya to bari na baki baby Nokia in kin dawo a sake wata to fatuha tace tare da shi ga daki ta dauko

sim din ta miqa mata wayar .mom tayi ta zura sim din ciki har ta kai bakin kofa ta dawo tare da haurawa sama part din sadiq ta nufa a hankali ta murda handle din kofar taji Kule gam tsoro ne ya kamata amma ba yadda ta iya haka ta dawo tare da yima mom sallama angel ko sai rigama take sai tabi fatuha mom ta hana.

Shigewa mota tayi driver ya harba da su kan titi cikin dan qanqanin lokaci suka Isa wudil. cikin kwatan can fatuha har driver ya kawo ta gidan fitowa tayi a hankali tana qare ma gidan su kallo gabaki daya gidan ya canza a yadda ta San sa mamaki ne ya bayana a fuskar ta qarasa Shiga tayi cikin sallamah inna d'ake parlour ce ta fito tare da yima fatuha maraba da zuwa duk da fatuha ba'a cikin jin dadi take ba bata yadda inna ta gane ba, parlour ta janta suka Shiga har yanzu mamaki ne shifide a fuskar ta tace cikin sanyin murya "inna waya gyara gidan nan?" murmushi inna ta saki ina yaran nan sadiq wallahi shi ya mana abin arzikin nan murmushi fatuha ta saki mai cike da jin dadi baffa ne ya yaye labilan ya shigo har qasa fatuha ta tsugunna ta gaisheshi amsa mata yayi a taqaice sannan ya samu wuri ya zauna. itama fatuha qasa tayima kanta mazauni tana jiran jawabin baffa gyaran murya baffa yayi tare da cewa "Fatuha nasan cewa na maki laifi amma kiyi hakuri ina fatan bazaki watsamin qasa a ido ba? ina fata bazaki bani kunya ba ?duk wannan jawabin da baffa keyi kan fatuha na qasa ,d'ago kai tayi tace "insha Allah baffa bazan baka kunya ba" yauwa diyar albarka, dama dan uwan sadiq ne ya zo neman auran ki tare da iyayan shi jiya da dare, mukanmu munyi mamaki da wannan zuwa fatuha ganin halacin da zura'a suka mana gashi nasan baban yaran hakan yasa na amince dan na lura yaran mai natsuwa ne Kuma dama neman auran budurwan anso iyayanta su zaba mata miji Na gari da wannan nayi la'akari na zaba maki majeed a matsayin miji. dagowa fatuha tayi a razane dan sai yanzu ta fahimci inda aka dosa idanuwan ta tap da kwalla suka ciko nan take hawaye suka fara anbaliya a fuskar ta me yasa mai kyau zai mata irin wannan horan me yasa fita tayi d'aga parlour da gudu ta fada dakin inna ta saki kuka mai tsanani mai ban tausayi, inna ce ta dafa bayan ta tana lalashin ta, haba fatuha bai kamata ki watsawa muta nan qasa a ido ba Kuma kowani mutun da qadarar dake zuwa mashi .fatuha idan dai majeed alkairi ne a gare ki Allah ya tabatar haka inna ta riqa bitana tausar fatuha har ta samu tayi shuru tana sakin ajiyar zuciya ko ruwa kasa sha fatuha tayi sai bayan sallah la'asar suka dau hanyar kano wayar tace dake cikin jaka taji qara message sai a lokacin ta tuna da mom tace ta kira ta curo wayar tayi ta karanta message din kamar haka,

_Sister ina matukar farin cikin Sanar d'ake yau buri na ya cika, tun jiya nake qoqarin kiran ki wayar takin Shiga ba wani albishir bane ila yaya sadiq ya kusa zama miji a gare ni ,sannan ina taya ki murnar zama inlow a gidan mu cikin family din mu d'aga basma._

Wani irin kuka fatuha ta saki mai cinrai ko ida karanta sakwan ba tayi ba wayar ta fadi jikinta in banda bari ba abin da yake. ashuru driver ya juyo haba fatuha komai yayi zafi maganin shi Allah bai kamata kina kuka irin h'aka ba ,duk wannan magana da ashuru yake fatuha ba jin shi take ba kalmar sadiq yazama miji Na kawai qwawalwarta ke fada mata har suka iso garin kano fatuha na sheka kuka kamar ranta zaifi ta, ko da ashuru yayi horn aka bude geta kafin ya tsada motar ta bale murfin motar ta fita da gudu sadiq da yanzu ya ji Qarar shigowar mota d'aga labila yayi tare da koma ya cigaba da zarya a bedroom din.

Da gudu fatuha ta haura sama ko kallan muta nan parlour batayi ba part din sadiq ta wuce Allah ya bata sa'a tana bude kofar ya bude, ganin bata gashin a parlour ba yasa ta shigewa bedroom da gudu . fadawa tayi jikin sadiq tare da sakin kuka mai cinrai ,rintse ido sadiq yayi yana jin yadda fatuha ke sheqa kuka cikin sarkewar murya tace "Uncle dan Allah karkamin wannan horan wallah bazan iya dauka ba, dama ace mafarki nake abin da nake ji ba gaske bane ta ida zancan tare da sakin saban kuka ta zame kasa.......

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*.
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn= H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERS FORUM.COM

77_78

Kuka fatuha ke rairawa Kamar ranta zai futa. gabaki d'aya jikin ta rawa yake qafafuwan sadiq ta riqe cikin shashekar kuka tace, "Please uncle I beg u in the of name of God a janye maganar auran nan wallahi ban shirya yin aure yanzu ba taqara rushewa da wani saban kuka" har yanzu jikin fatuha bar'i yake ,uncle ya zanyi da karatu na? bayan duk duniya ba abinda nake so sama da shi, wallahi uncle ba abinda ke tsakanina da majeed kaji ta qara sakin kuka mai cin rai ( *ko ni salma sai da na matse kwalla*😥) da kyar sadiq ya sai ta kanshi tare da hade hawayan d'ake maqale a kwayar idanuwan shi ya juya, d'ago fatuha yayi d'aga zaune da take ya zaunar da ita zaman bed amma duk da h'aka ba daina kukan tayi ba .fridge ya bude ya curo robar ruwa ya

tsiyaya a cup ya miqa mata .kuka kawai take baji ba gani, aje cup din yayi bedside drowe ciki cool voice din shi sadiq yace "Fatuha!" tsagaita kukan tayi tana kallan sadiq , lalashin ta sadiq ya shigayi cikin sanyi murya yace, "Fatuha ina so ki sani ko kadan bani na maki haka dan na hora ki" daura hannu shi yayi a fuskarta, h'aka itama fatuha ta daura nata saman hannu shi tana sauke ajiyar zuciya. ya cigaba da cewa "Bayan na dau alqawarin samamaki farin ciki har qarshan rayuwar ki fatuha? dan meyasa zan rusa maki mafarkin ki? ina so ki kasan ce mai daukar qadara mai kyau da mara kyau, da anyi shawara dani fatuha ba abinda zai sa na amince a katse maki karatun ki? ko yanzu nasan majeed zai barki kiyi karatu kinji, ki kasan ce me yima iyayan ki biyaya zaki ga riba haka, kuma insha Allah zaki so majeed saboda majeed nada kyawawan hali kuma yana sanki zai b'aki duk wata kulawa .ba zai bari ki taba zubar da hawayan ki a kanshi ba, ki daure ko so d'aya ne ki sama ranki son majeed ko dan yana dan uwa na" wasu zafafan hawaye ne suka gangarowa fatuha tana bin sadiq da kallo, dan ko bakin magana ta rasa, sadiq ko in ban da daurewa ba abinda yake dan numfashin shi neman yankewa yake ,sai ya numfasa yake cigaba da maganar saboda zafi da quna da qirjin shi ke mai, glass cup din sadiq ya miqa ma fatuha ta kafa kai ta shanye ruwan a hankali taji sanyin ruwan na ratsata, shiru suka dauka na mintina ba wanda ya tanka, can sadiq yace "Fatuha kimin promise baza ki tada hankalin ki ba, da kyar fatuha ta iya furta to wasu hawayan suka sulalo, jiki ba qwari ta tashi tana qoqarin fita sadiq ya bita da kallo dan bejin zai iya tsaida ta saboda ganin tama qara famamai ciwo a ransa".

Tana fita sadiq ya kafa rubar ruwan ya shanye yana maida numfashi tare da ganin wasu taurari namai yawo,

Tsayawa tayi b'akin stairs ta share hawayan ta dan bata san mom ta gani cikin natsuwa ta sako, mom da fitowar daga kitchen kenan ita da baba jinmai murmushi ta saki ah fatuha har kin dawo eh tace tana qoqarin hadiye hawayan idanuwan ta, masha Allah ya su inna? lafiya lau tace, sannan mom tace ina fata baffa bai maki dole ba d'aga kai kawai tayi alamar a'a, baba jinmai ce ta shafa fuskarta tace "Alhamdulillah hajiya ni dai bani da abin cewa kun gama min komai a rayuwa ta ida zancan tana matsar kwalla" d'aga kawo fatuha aiki sai gashi ta zama yar gida har zaku aura da ita hajiya na gode na gode Allah ya bar zuminci baba jinmai ta fada tana share kwalla idanuwan ta, haba baba ai duk mun zama d'aya ai fatuha ta cancanci abinda yafi haka, haka baba jinmai ta rinqa zuba Godiya sannan tasa kai ta fita, fatuha kuma ta shige bed ko da shiga d'akin sana'ar ta fara wato kuka dan ya zamar mata jiki d'aga shekaran jiya zuwa yau. bedside drowe ta bude ta Ciro sarkar da sadiq ya bata tana kuka sai ta ci kuka ta gaji sannan bacci ya dauke ta

Bangaran basma in ban da murna ba abinda take take, duk wasu qawayan ta ta fesawawa zata auri handsome, har wani jin ta take a sama yanzu, majeed ko ya kira layin fatuha har ya gaji yanke shawarar zuwa gidan gobe yaga sanyin idaniyan shi, sannan ya juya ya gyara kwanciyar shi .

Kiran sallah ne ya tashi fatuha jiki ba qwari ta shiga toilet tare da sheqa waka ta dauro alwala wani irin jiri ke dibar ta saboda kukan da tasha jiya ,da kyar ta iya gabatar da sallah ta zura uniform dinta tare da daukar school bag din ta ta fito,

Ko da ta qaraso dining area mom ce da abba sai angel dake gefe cikin natsuwa ta gaishe su kamar kullun taja kujera ta zauna .ruwan tea kawai ta iya hadawa tana sha kamar tana shan magani kamshin turaran da taji ne yasata dagowa sadiq ne cikin uniform din shi yana riqe da briefcase din shi yasha kyau har ya gaji sai dai fuskar shi ba walwala angel ce ta gaishe shi ya amsa tare da yi mata pack, kallan shi fatuha take har ta kasa kauda idanuwan ta haka shima sadiq ita yake kalla tuni idanuwan ta sun cika da kwalla girgiza mata kai sadiq yayi alamar kar tayi kuka lumshe ido tayi tare da qoqarin hadiye kukan da ke niyar kuboce mata, sallamar majeed ce ta doki dodon kunan ta. ware ido tayi tana kallan kofar sanye yake da uniform din shi sai sheqi yake qarasowa yayi tare da gaishe da su mom amsawa tayi cikin fara'a, tare da cewa yasu umma? umma lafiya lau mom , sadiq d'ake tsaye take fara'a shi ta dauke daurewa yayi ya tataro natsuwar shi tare da sakin murmushin karfin hali, my man yau kai ne da safenan Sosa keya majeed yayi tare da kallan fatuha kauda kai tayi ta cigaba da juya tea din dan ba sha take ba.

Haka sadiq ya rinqa danne zuciyar shi, fatuha kuma haka ta gama juya tea din ta tashi tare da daukar school bag din ta ta ja hannu jidda suka fice tare da yima mom sai sun dawo .tana fita majeed yabi bayan ta haka shima sadiq kasancewar office zasu ,

Zata shiga mota majeed yace baki ji, daure fuska fatuha tayi dan wata tsanar majeed take ji juyowa tayi a fusace dan ta gayamai mara dadi hango sadiq tayi bakin mota da alama su yake kallo , kauda kai sadiq yayi yana wani jin suya a zuciyar shi da radadi bale murfin mota yayi ya shige, murmushi fatuha ta saki wanda iyakar shi laban ta tace uncle majeed inakwana, cikin zaquwa yace lafiya lau my love, cikin sunyi murya yace "Fatuha!" na'am tace a taqaice dan da kyar take mai magana saboda tsanar shi da ke bin zuciyar ta, nasan na maki laifi my love naje nayi abu bada sanin ki ba amma please kiyi hakuri wasu Sabin hawaye fatuha ta h'ade tace "Ba komai tana qoqarin bale murfin motar, idan dai kin hakura please ki bini nayi dropping din ki? daure fuska fatuha tayi dan bata jin zata iya bin majeed a yanzu, lagwabe kai majeed yayi yace please ki bani dama duk da nasan bani da mazauni a zuciyar ki,Am ma Dan Allah Kiyi hakuri kisoni koda kadane,tunda nataso bantaba samun yarinyar DA ta kwanta min a rai kamarki, fatuha please ki bani dama na gwada maki soyayyar da nake maki haka majeed ya rinqa magiya da kyar ya samu fatuha ta shiga motar shima sai da jidda suka shige ya ja motar.

Sadiq dake zaune cikin mota yana k'allan duk yadda suke ,da kyar ya iya saita numfashin shi, tabas yasan ranar da fatuha zata zama malakin majeed ba abin da zai hana shi zama gawa .da kyar ya iya bude baki ya ce ma driver ya jasu,ba musu yabi umarnin ogansa suka bar haraban gidan.suna zuwa wajen aikinsu SadiQ ya bude motar yafito tare DA daukar jakarsa

,ahankali yake tafiya kamar kazar DA kwai ya fahema aciki. Duk inda ya wuce ma'aikata Nata gaisheshi hannu kawai yake daga masu, domin jiyake bakinsa yayi masa nauyi. Yana zuwa office dinsa yabude yashiga ,yayi jifa DA breekfest dinsa ya zauna bisa kujira wani kuka ne ya subuce masa Mai radadi DA ciwo, jiyake duniyar nayi masa zafi,bai tab a sanin yana kaunar fautuha ba sai yanzu DA yake shirin rasata. Way majeed ! Me yasa zakamin haka? Me yasa kake Neman ruashemin farinciki na? Me yasa zakace kanason Fatuha alhalin nafika bukatarka a yan " DA karfin tsiya ya d'aki teburin d'ake gabanshi yace nooooo Fatuha tawace insha Allah wani murmushin karfin hal'i yayi (DA Ni Salma nakasa gane ma'anar hakan).

Majeed nayin parking a harabar makarantar Fatuha ta Kama murfin motar zata bude ,DA sauri ya Dana wani remot ya rufe koffofin motar ,cike DA tsiwa ta dubeshi suna hada ido dashi ta sunkuyar DA kasa, batasan meyasa majeed yake Mata korjini duk yanda taso yimasa rashin kunya suna h'ada ido zata nemi natsuwar ta tarasa. Murmushi majeed yayi yace, "Haba My love ,ya za'ayi kifita kibar mijinki DA tsananin tunanin ki? Ya kamata kifada min wata kalma DA zaisani tunanin ki koda Ina office plsss matata kada kice min aa". Takaicine ya lulube Fatuha ,banda iskanci gidan uban wa aka d'aura mana aure d'ashi  DA har zai kirani matarsa taja tsaki a ranta mtsss ,a fili kuma tace " Plsss oncl kabarni natafi Dan Allah ta karasa maganar kamar zata Mai kuka" Sorry my lovely Zaki tafi amma Dan Allah Kiyi min murmushi KO Zan samu tsuwar zuciyata?" Fatuha tace a ranta "Dan iska shege mugu kawai Allah yasa zuciyar ka ya dawama DA bakinciki k'amar yand'a kak'e ko'kari'n sani". A fili kuma tayi murmushi DA iyakarshi lebenta, majeed ya b'ude masu kofa'r DA sauri ta fita tayi gaba, jeedah nako'kari'n binta majeed yaciro kudi masu yawa yaba jeedah shi kansa baisan KO nawane. tayi Mai godiya tare DA Mai piek a kumatu ta tafi DA gudu domin har Fatuha tayi Mata nitsa, shima majeed cike DA farinciki ya bar harabar makarantar....

*_Kuyi h'akuri da wannan page din, b'ana samun time sabod'a yanzu na k'oma  skul._*

*Taku h'ar kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum

RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

79_80

Ko da fatuha ta shiga class ba wani walwala, haka su nana suka rinqa tanbayar ta "Ta fada masu meke damun ta?" amma firtaqi gaya masu damuwar ta, Nana ce tace, "Haba fatuha kenan baki daukemu a matsayin qawayan ki ba? da har zaki boye mana abun dake damun ki" Zara ce ta budi baki tace, "Kyale ta Nana ai dai mun san matsayin mu yanzu "Zara na qoqarin jan nana subar seat din , fatuha ta riqe Zara please kuyi hakuri, zan fada maku damuwa ta ida zancan hawaye na sulalo mata. duk abin ya faru haka fatuha ta kwashe ta fada masu, Zara taji haushi ba kadan ba haka suka rinqa bama fatuha hakuri tana raira kuka da kyar suka shawo kanta.

Bangaran majeed inbanda dad'i ba abinda yake ji ,zuciyar shi fes take d'aya lumshe ido kyakyawar fuskar fatuha yake hagowa sai ya qara sakin smile,

Jingine yak'e saman kujera office ya rasa sukunin shi, idanuwan shi na lumshe saboda nauyin da suka mai har wata masasara ke rufe shi ga qirjin shi dak'e mai zafi. a hankali ya ware sexy eye's ball's din shi da suka rine sukayi jaa wayar shi dak'e ruri cikin aljinhun shi ya curo sabuwar number ce baro baro a screen din, da kamar ba zai dauka ba sai ya daure ya dauka tare da karawa a kunne. Cikin zazakar muryata cikin yauki basma ta mai sallama, amsawa yayi a taqaice tare da tanbayar wake magana? gyara kwanciyar tayi d'aga inda take tare da kankame wayar dan wani irin sanyi ke ratsata, dan gyaran murya tayi cike da shagwaba tace, "Yaya sadiq ni ce fa basma? ko number ta ashe baka da ita? ta ida zancan cikin shagwaba" Sadiq d'ake kishingide saman kujera, ranshine ya qara suya dan shi duduniya ba macan dak'e birge shi ko bashi sha'awa kamar fatuha, ko wannan magana ma da take yi jiyake kamar tana watsa mai ruwan zafi, tsuke fuska sadiq yayi kamar tana ganin shi yace, "Yanzu ina wani aiki ne letter mayi magana in na dawo" be jira ce wata ba ya katse wayar tare da yin wurgi da ita ta dak'i bango ta dawo watse ko ta kanta be bi ba ya sa kai ya fice d'aga office din.domin idan ya cigaba da zama tabas kwakwalwar shi da zuciyar sa suna iya bugawa. bin wayar tayi da kallo tare da dan bata fuska , ta aje wayar ta kwanta.

Ko da aka tashi su fatuha majeed ne ya zo daukar su ,ganin shine yasa ta had'a gira sama

data kasa dan ba abinda ta tsana kamar ganin shi. ba yadda ta so haka ta bale murfin motar ta shiga tare da gaishe shi, kallan ta yake me cike da so da kauna , sannan yace "My love d'aga gani yau kin sha wuya da yawa? ina fata dai kina kulla min da kanki?" dan guntun tsaki fatuha ta ja ciki ciki sannan tace a cikin zuciyar ta "Har wani Kira kake na kulla ma da kaina mtww dan iska kawai" muryar majeed ce ta doki dodan kunnan ta a karo na biyu yace "My love! ko duk gajiyar ce tasa ko magana ba'a San yimin?" dan smile fatuha tayi wanda iyakar shi laban ta tace "A'a" murmushi majeed yayi tare da cigaba da driven din shin, haka ya rinqa janta da surutu tana amsa mai sama sama sannan ya wuce da su bakery yayi masu siyaya ice cream da cake. jidda ko sai dadi take ji dan har yanzu bata san inda aka dosaba.

Suna kunna hancin motar su. suka ci karo da sadiq wanda shima dawowar shi kenan wani irin dogwan numfashi sadiq yaja a duk lokacin da yaga majeed da fatuha, numfashin shi sai ya nemi ya dauke ko qirjin shi ya rinqa mai zafi. da kyar ya iya d'aga kafar sa dan baya so ko fuskar su ya gani sun fito a tare, amma sai dai kash majeed ya riga ya kira sunan shi. lumshe ido yayi ya tsaya chak! sai da ya kwashe yan mintina sannan ya waigo tare da sakin smile din karfin hali, ta gaban shi fatuha ta raba ta wuce jidda nata zuba mai surutu sannan itama ta shige, miqa mashi hannu majeed yayi suka gaisa, big man duk yau ban ganka a office ba oh ina cikin office ina wani aiki ne gobe ma nake so na wuce Lego's , Lego's kuma ?me zaka je yi loges? inji majeed zan je nayi 2week ne cikin ruwa na dawo , Eyya to Allah ya taimaka ameen yana qoqarin shigewa majeed yace, "Baby!" yes yace a taqaice dama ina so muyi wata magana ok mu shiga ciki ok majeed yace tare da bin bayan sadiq suka shiga part din sadiq briefcase din shi sadiq ya aje tare da rage kayan jikin shi ya shiga toilet, ya dade a toilet din beyi wankan ba yana kukan bakin ciki sannan ya tashi yayi wanka sanye da bathrobe ya fito qaramin towel a hannu shi yana goge jikin shi. majeed na zaune saman sofa shima tashi yayi ya shige toilet ya sheqa wanka ya fito ko da ya fito lokacin sadiq ya shirya cikin black 3 quarter din shi da white shirt mai gajeran hannu, yana zaune saman sofa idanuwan shi lumshe, shiryawa majeed yayi a tsanake sannan ya bude wardrobe din sadiq ya ciro riga da wando riga blue sai dark blue jeans sannan ya bude fridge ya curo fresh milk ya tsiyaya a cups ya miqama sadiq ya amsa, zama yayi kusa da sadiq yace, "Please ina so kamin taimako guda please?" ok inajin ka indai baifi karfina. murmushi majeed ya saki yace "Befi karfin ka ba" gyara zama sadiq yayi yana sauraran majeed riqe hannu shi majeed yayi cikin lagwabe kai please baby kamin hanya fatuha ta so ni .tsura mashi ido sadiq yayi da idanuwashin da suka cika da kwalla hadiye su yayi yana saurara majeed, baby wallahi ina san fatuha ban taba jin San wata ba kamarta ba baby karkayi tunanin irin sanda nake ma sauran yan'mata nea nake mata a'a santa nake da gaske wallahi inna rasata zan iya rasa rai na majeed ya fada. sadiq dai binshi yake da ido kamar sakarai gabaki daya jikin shi ya mutu sai zuciyar shi dake ta har bawa da sauri kamar zata fito waje ,dan matse hannu shi da majeed yayine ya sasa dawowa d'aga duniyar tunanin .smile ya saki, haba my man karka damu kaji dan jama aji take amma nasan zata so ka kaji Kasan yadda mata suke amma nasan zata so ka har ku dai-daita .murmushi majeed ya saki tare da kaima sadiq hug hawaye suka cigaba da yima sadiq anbaliya dan ko yasan ya rasa fatuha Dan baya fatan abinda zai samu majeed dan uwan shi abokin shi bashi da aboki dan uwa saman da majeed.

lokaci yayi da ya kamata ya ba zuciyar shi hakuri jin majeed zai zame jikin shi yasa sadiq saurin share hawayan shin tare da sai ta kanshi murmushi suka sakar ma junan su, fira suka fara sama sama kiran sallah magrib ne ya tashe su,

*1week letter*

Shirye shirye aketayi a family house, kasancewa yau za'a sa rana biki duk wanda ka kalla cikin farin ciki yake musanman basma da majeed, zaune suke cikin daki'n yan'mata ana zuba hira muryar basma k'adai ke tashi fatuha na gefe tana matsar kwalla dan har yanzu gani take kamar wasa ,kamar mafarki tashi tayi ta fita dag'a dakin ganin kayan da ake ta wucewa da sune yasa jiki fatuha ya qara sanyi. fitowa tayi d'aga parlour hango qanan baban ta tayi su baba barau wasu hawaye masu zafi suka sulalo mata yanzu ta tabatar za'a Samata rana da wanda bata so a matsayin miji kuka ne ya ci karfin ta. fita tayi d'aga gidan gabaki daya dan ko sanin inda zata ba dan inda zata ba. can baba jinmai ta fado mata a rai kekenapap ta tara ta shige tace "A kaita gadan qaya" kasan cewar gidan baba jinmai kan titi yake bata wani sha wahala ba ganin gidan. kukan da take yasa mai kekenapap din bar mata kudin saboda ya tausaya mata ko sallama bata cika ba ta shige gidan, baba jinmai dake qoqari fita, fatuha ce ta fada jikin ta tare da sakin kuka kamar ranta zai fita. rudewa baba jinmai tayi tana kallan ta baki saké, zaunar da ita tayi saman kujera tana tanbayar ta lafiya? kuka take sosai, cikin shasheqar kuka tace "Wallahi baba bana san majeed bana jin zan iya zaman aure da shi ta ida zancan tana rushewa da kuka" sallati baba jinmai ta hauyi tare da tafi na Shiga uku ni jinmai , me nake ji haka fatuha sokike ki ja mana abin fade ?toh in ba majeed din ba wakike so? kuka ta kuma saki cikin shasheqar kuka bakin ta na rawa tace "Baba sadiq nake so! wallahi ina rasa sadiq mutuwa zanyi" ta ida zancan tana kuka mai tsuma zuciya, zaro ido waje baba jinmai tayi na Shiga uku ni jinmai. rungume fatuha tayi tana lalashi dan ita kanta ta tausayama fatuha ita kanta taso ace da sadiq din za'ayi ,amma ya zasuyi tunda shi be ce yana so ba? d'ago da fatuha tayi tana share mata hawayan ta kiyi hakuri fatuha kinji ki cigaba da addu'a Allah yana tare dak'e Allah zai dubi zuciyar ki ya baki mafi alheri fatuha kisama zuciyar ki sallama kinji .ajiyar zuciya kawai take saki tayi lamo a jikin baba jinmai.

In banda tari ba abinda yake har wani jiri yake gani ,majeed d'ake gefan shi sai sannu yake mai. toilet ya shige da sauri yana cigaba da tarin gaban zing kallan mirror d'ake manne jikin zing din yayi jini da ya ganine gefan bakin shi ya sashi zaro ido! hannu ya kai ya taba ganin kamar jinine yasa gaban shi ya qara faduwa hawayan dake maqale a idanuwashi suka sulalo.zamewa yayi a qasan toilet din yayi yana mai da numfashi sama sama miqewa yayi da sauri ya fito duk da yana jin jiri .majeed dak'e zaman jiranshi ne ya ta shi yana mai sannu ko amsa mai sadiq ya kasa, wardrobe din shi ya bude ya janyo trolley ya fara zuba kayan shi yana zubawa jiri na dibar shi ga tarin sai zuwa yake tare da jini amma duk wannan abun yaki yadda majeed ya gane sai da ya gama had'a kayan shi tsaf majid na gefe tsaye riqe shi yayi yace "Baby wai me ke faruwa ne? naga muna lafiya lau lokaci daya ka rude" murmushi yayi yace "Karka damu tunawa nayi da flight dina na zuwa Lego's yau zai tashi kuma gashi saura 10 minutes ya tashi" ok muje nayi

dropping naka ka barshi kawai nayi ma driver magana kaji? ok ya ce mai tare da yi mai pack sannan ya sa kai ya fita da kyar ya iya jan trolley ya fita waje yana tafiya yana tari tunkan ya qara so ashuru driver ya bude mai murfin mota amsar trolley din yayi yasa a boot sadiq yana Shiga mota ya fara b'ale bottle din rigar shi saboda zafi ga numfashin shi d'ake daukewa yana dawowa. ko da ashuru driver ya shigo mota ja yayi suka bar harabar gidan ta cikin mirror ya fara ganin halin da sadiq yake ciki. yallabai! yace a tsorace cikin murya da kyar da kyar sadiq ya iya furta kaini wajan Dr yakub aiko da gudu ashuru ya fisgi mota sai asibitin Dr yakub suna Isa asibiti sadiq ya bude murfin motar duk da yana ganin jiri ga numfashin shi dake mai sama sama office din Dr yakub ya nufa yana bude kofar ya fadi sumame a wajan...🙆‍♀️😰

Muje zuwa fan's

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

81_82

Mikewa Dr yakub yayi dan kawowa sadiq taimakwan gagawa. gabaki d'aya shima ya rude kwalawa norses kira ya shiga yi da sauran ma aikatan asibitin kafi kace me har an daura sadiq a gadan asibiti ,ashuru driver da shigowar shi yanzu ya gani bin gadan yayi yana matsar kwalla, ba'a zame da sadiq ko ina ba sai emergency, ashura na ganin hak'a ya ci birki bakin kofar yana zarya yar wayar da ke aljihu shi ya zaro dan ya kira gida amma sai dai wayar ba chaji kuma bai iya tafiya ya bar sadiq a yanzu dan ana iya buqatar wani abu. h'aka ya rinqa zarya baki'n kofar ga baki d'aya ya rude.

Hak'a baba jinmai ta rinqa lalashin fatuha sannan tayi shuru, fatuha  tashi kiga mu koma tunda dai kin san aiki na can na jira na ? matsar kwalla ta fara cikin sanyin murya tace "Dan Allah baba ki barni a nan wallahi bana san zuwa, bana san jin hayaniyar kowa! mudin na cigaba da ganin abinda ake a gida ina iya shiga wani hali" duk yadda baba jinmai taso ta tafi da fatuha firtaqi ba yanda ta iya shiya ta barta ta tafi ko da baba jinmai ta fita kuka fatuha ta dasa.

Shewace ke tashi yadda kasan yaune daurin auran. zuhura ce ta shigo da sauri ta fada jikin basma tare da cewa "Ansa biki wata d'aya" washe baki basma tayi tare da curo wayar ta fara kiran sadiq duk wannan kira da take ba'a dauka ba tabe baki tayi tare da cewa duk kayi ka gama aure sai munyi duk wulaqanci da kake zubamin bashi zai sa na daina san ka bâ,ta ida maganar tare da jan dan guntun tsaki, hanan ce tashigo jiki a sanyaye basma ce tace "Ke kuma lafiyar ki kuwa?" wallahi tun dazu nake neman fatuha a gidan nan narasa  inda ta shiga? na kira wayarta yafi aqirga" toh fa! dazu dai tanan cikinmu har tace min "Kanta na ciwo na bata magani, namayi tunanin bacci tayi?" ok qila ta koma gida. amma bari inmun gama abinda muke sai muje ko? eh gaskiya sannan hanan tasa kai ta fita.

Bangaran iyaye angama komai inda mom ta yanke shawarar basma ta koma can gidan yadda za'a ji dadin kula da amaran. waje daya kuma kowa ya amince da shawara.

Haka doctors sukayi cha a kan sadiq dan ceto rayuwar shi inda suka ci sa'a ciwo zuciyar bai dade da kamashi ba, daya sha magunguna yadda ya kamata zai warke sai da yama likis aka fito da shi. ashiru yabi bayan su aka ba sadiq daki, har lokacin sadiq na kwance yana bacci sai qarin jini dak'e mai wanda doctor yakub ya bada nashi, ashiru zama yayi d'aya dag'a cikin kujerin dakin sai da ya dan jima sannan ya wuce office din Dr .ko da ya shiga lokaci yakub ya fita ganin wasu marasa lafiyar haka ya wuce gida dan sanar masu  halin da sadiq yake ciki.

A hankali yake ware sexy eye's ball's din shi da yamai nauyi, bude kofar akayi a ka shigo ba kowa bane sai Dr yakub qarasowa yayi gadan tare da zama gefe a hankali ya kai hannu goshin sadiq har yanzu da zafi rau cikin sanyi murya Dr ya fara magana "Captain me yasa  kake wahalar da zuciyar ka da tunani tuntuni? nayi tunanin ka daina tunani amma yanzu ka dawo da shi ?sadiq har kaja ma kanka ciwo zuciya" lumshe ido sadiq yayi kawai yana sauraran Dr. na rasa wanne irin tunani kake wannan sadiq? ciwo nan da kake gani yana iya jama ka rasa aikin ka sadiq, da ace asibitin mu ka je ai da yanzu an farama shirin sallama. rike hannu sadiq yakub yayi tare da sake cewa p"Please ka fada min damuwar ka please sadiq?" hawaye ne masu zafi daya ke bin daya a fuskar sadiq shi kan shi yakub ya firgita da yanayi da sadiq ya koma yanzu, cikin sanyin murya Dr yace "Tunda baka iya fada min ya kamata a gida a san damuwar ka ya fadi hakan yana qoqarin fita" riqe hannun sa sadiq yayi tare da ware idanuwashi da suka zama ja y'a ce  "Please karkamin haka Dr bana fata kowa yasan abinda ke damuna a yanzu please kamin alqawarin baza ka fada ma kowa ba?"zame hannun shi Dr yayi dan baya jin wannan

karan zaiyi shuru .har ya kai bakin kofa sadiq yace " Dan Allah karka fadi please ya ida zancan yana kuka mai cinrai" chak Dr yakub ya tsaya dan gabaki daya tausayin sadiq ya lulube shi dawowa yayi da sauri saboda tarin da yake taimako gagawa ya bama sadiq tare da yimai allura samun hutu. ya fita ko da ya shiga office ya kasa zaune ya kasa tsaye yana tunanin inda matsala sadiq take dan yanzu ya lura ko yasha maganin indai zai cigaba da tunanin da yake zai zama anyi ba ayi ba.

Ko da ashiru driver ya koma gida har yanzu basu dawo ba, suna family house juya wa zaiyi da motar ya wuce family house kenan, sai ga fatuha mai kekenapap ya ajeta ta fito sukuku ba alamar walwala dan itama a tunanin ta sun dawo. ashuru ne yayi parking tare da qarasowa ida take gaishe shi tayi a taqaice tana qoqarin shigewa gida, fatuha "Na'am" tace tare da waigowa dama dama gaban tane ya yanke ya fadi saboda yadda ashurun ke magana kamar wanda yayi ma sarki qarya. me ya faru ta fada a taqaice ?dama yallabai ne ba lafiya yanzu haka yana asibiti na zo fada maku ne kuma har yanzu basu dawo ba, zaro ido fatuha tayi tare da dafe qirjin ta tuni hawaye suka fara mata anbaliya, me ya same shi? ta fada bakin ta na rawa, muje ka kaini asibitin sai inka ajeni sai ka biya family house ka fadi da sauri ta shiga motar ashuru ya ja sai asibiti. suna Isa ta bale murfin motar ashuru na gaba tana biye tana kuka suna Isa dakin ashuru ya juya fatuha ta shige ganin halin da sadiq yake yasa fatuha qara sakin wani saban kukan tare da qarasowa bakin gadan, a hankali ta kai hannu ta saman kan sadiq hawayan na sulalo mata ruwan hawayan ta ne ya d'iga a saman idan sadiq. a hankali ya fara ware idanuwashi ya sauke su kan fatuha da taci kuka ta gaji riqe hannu shi tayi tace "Uncle meke damun ka?" murmushi ya qaqaro wanda iya karshi laban shi ya kai hannu ya gogewa fatuha hawayan ta lumshe ido yayi tare da cewa "My dear bana so ina ganin ki kina kuka kinji? ba wani abu bane ke damuna ba kawai fever ne saboda na daina ganin smile din ki ya fadi zancan yana ja mata hanci" smile fatuha ta saki mai kuka kuka tare da kai mai pack a goshi Dr yakub da yanzu ya turo kofa ya shigo. ko sannin ya shigo basuyi ba . tsayawa yayi yana kallan su yana tu a ni, musanman yadda ya ga lokaci daya sadiq ya sauya, gashin kanta ya taba wanda ya leko waje yace fatuha "Na'am" tace tana kallan shi cike da so da kauna, me yasa kika daina kulla da gashin ki? hawaye ne suka sulalo mata ta bude baki za tayi magana sadiq ya daura yatsanshi sama lips din ta shhh a hankali ya kwance dankwalin kanta gashin ya baje a gadan bayan ta ba wai wanke kan ne batayi ba. a'a duk wasu mayuka masu sa kan sheqi ta daina shafawa saboda ko lokacin hakan bata da shi, har yanzu baki son majeed ko? kuka ta saka mai mai cin rai har da shesheqa. rintse ido sadiq yayi tare da shafa gefan face nata kukan ya Isa haka mana bana so naga kina kuka kinji? d'aga mai kai kawai fatuha tayi tare da daura hannuta saman nashi. tace "Shikenan uncle yanzu basma zaka aura? ta zama matar ka? angel ta zama diyarta ko?" kuka ta kuma saki mai cin rai shima haka sadiq bakin ciki kawai ke cin shi smile yayi yace "Nace fa ki daina kuka kuma angel diyarki ce ai" daga kai tayi yace "good!" haka kuma nima naki ne? ko baki so na auri basma? in baki so sai na fasa ya fada yana smile. ba wai bana so bane um bata inda zancan ba Dr yakub yayi sallama dan ya lura sai su kwana suna hira gashi fira da ya ji suna yi kamar cike take da matsala da rudani inya fahimta kenan, sauri tayi ta daura dankwallin ta tare da gaishe da Dr alura ya ma sadiq tare da cewa wanake gani kamar fatuha murmushi ta saki tace "Ni ce" gaskiya naga kin canza, ko duk amarcin ne ya fada yana kallan

face din sadiq? take annurin sadiq ya fara daukewa haka fatuha dake zaune kusa da shi kawar da zan can yayi dama face nasu yake so ya karanta idan har ya gane suna son junan su, amma sai dai kowane wani da ban zai aura, insha Allah zai taya su da addu'ar cikar burin su.

Ko da ashuru ya je gida ya fada kusan motar biyu sukayi ko 10 minutes basuyi ba suka iso asibiti,a lokaci fatuha na feeding din sadiq abinci yana ci suna dariya dan ji yake gabaki daya kamar ya warke. turo qofar da akayi ne yasa su waigowa majeed ne ya fara shigowa turus yaja ya tsaya yana mamaki yaushe fatuha ta zo? haka basma dake bayan shi da umma da mom, ashuru ne da shigowar su yanzu shi da su abban ya fada masu yadda a kayi har ta zo dan sakin jikin majeed yayi amma har yanzu ya kasa kauda ido daga abinda ya gani. duk kunya ce ta kama fatuha aje plate din tayi tana qoqarin tashi, sadiq ya riqe hannu ta yadda baza ta iya matsawa daga kusa da shi, dan be iya hakuri da rashin ta kusa da shi kallan shi take tana mai alama ya sake ta amma yaqi dainawa. sai wasa dayake  da hannu ta ganin ba yadda za tayi yasa ta hakura basma ko ta cika fam dan ita taso ace ita take kusa da shi ba fatuha ba. shima majeed ba laifi ya dan shaka amma yaki yadda zuciyar shi ta fadi abinda take tunani sai ma watsar da zancan da yayi shi ko sadiq yaqi sankin hannu ta da sunyi ido biyu sai ya sakar mata da lalausan murmushi, mom da ke lura da yana yin su sai suka bata tausayi dan dai kar tayi magana ace gashi, da ba abinda zai sa tace a basa auran amma da tayi magana tasan abinda zai biyo baya ko da su abba suka tanbayi Dr yakub me ke damu sadiq fever ya ce masu a taqaice .

Kiran sallah magrib ne yasa Sadiq ya saki fatuha dan ta dauro alwala lokaci har su mom sun tafi. daga ita sai basma sai majeed da shima yanzu ya wuce masallaci  tana Shiga toilet basma ta matso ta zauna kusa da sadiq kasancewar ita Hutu take, ya jikin tace mai cikin yauki da kisisina. lumshi ido yayi tare da cewa "Da sauki" Allah ya baka lafiya sweetheart miqewa tayi daniyar ta mai pack lokacin yayi dai dai da fitowar fatuha daga toilet, bin gadan tayi da kallo ga wani irin kishi dak'e cin ta wanda ita kanta bata san tana da shi ba. juyawa baya sadiq yayi tare da cewa cikin cool voice din shi "Basma kai na ciwo koya naji an tsayamin a kai nauyi yake min ya fada yana kallan fatuha da saura qiris ta fashe" fita tayi d'aga daki'n da sauri ko da ta fita kuka ta saki mai ban tausayi. ta Dade tana kuka sannan ta samu guri a wajen tayi sallah...

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52&red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

83_84

Bayan ta idar da sallah tana qoqarin nade daduma majeed ya shigo lalausan murmushi ya sakarmata tare da qarasowa kusa da ita. duqar da kai tayi qasa tana wasa da carpet din hannu ta, a hankali majeed yasa hannu ya d'ago da fuskar ta, kallan fuskar majeed yake cikin so da kauna. cikin sanyin murya yace "My love me ya saki kuka?" kamar jira take ya tanbaye ta ta fashe mai da saban kuka. rungume ta majeed yayi yana lalashin ta tare da samun daya d'aga cikin kujerin wajan suka zauna. daura kanta yayi a kafadar shi yana shafa mata bayan ta a hankalin cikin sanyi murya yace "My love bana so naga kina kuka? idan kina kuka sai naji nima kamar nayi, meke damun ki ki fada min koma minene zan samamaki indai zai saki farin?" cin da gowa fatuha tayi ta kaleshi, a cikin azuciyar ta tace "Ba komai zakamin ba, ila ka ce ka fasa aure na! ka barni da muradin raina da zabin zuciya ta ,abinda nake son gani safe rana dare wanda bana gajiya da ganin shi, wanda bana gajiya da sauraran shi ta qara rushewa da kuka" gabaki daya majeed rudewa yayi da yanayi fatuha sai aikin lalashin ta yake da kyar ya samu ta daina kuka sai faman ajiyar zuciya da take. daura kanta yayi saman kafadarshi yana wasa da yan yatsun ta masu laushi sun dau mintina suna a h'aka sannan fatuha ta zame kanta daga kafadar shi tana qoqarin tashi .d'ago fuskar ta yayi yasa lalausan hannu shi ya goge mata hawayan ta tare da yi mata pack a goshi runtse ido fatuha tayi tana jin wani irin suya da zuciyar ta kema ta mai cike da tsanar majeed ,hannun ta ya riqe suka miqe a tare sannan ya amshi dadumar hannuta a hankali suka bude kofar d'akin suka shigo .har yanzu sadiq na kwance amma ba bacci yake ba sai basma na gefan shi tana zuba mai iyayi yana saurara, shigowar su fatuha ce tasa shi dan dagowa ya jingi idanuwashi ne suka hango mai hannun fatuha cikin na majeed, wani irin b'akin ciki ne ya taso mai tabas wannan ba jinya aka zo ba zuwa akayi aga gawar shi, lumshe ido yayi dan baya iya jurewa ganin baki'n cikin .zame hannun ta fatuha tayi tare da zama tana facing din sadiq,

Majeed qarasawa yayi wajan sadiq tare da shafa sumar shi yace "Baby!" bude idanuwashi sadiq yayi tare da sakin murmushi riqe hannun shi majeed yayi tare da zama, aika ma sadiq harar wasa yayi tare da cewa "Shine baka da lafiya kakasa fada min baby? wai me yasa

kakemin haka ?in abu na damun ka baka fada min saboda ban kai matsayin ba ko ?" ya fada yana lagwabe kai dan shagwabe. fuska sadiq yayi yace "Sorry banyi tunanin fever ya kai haka ba, nayi tunanin har sai naje Lego's nasha magani" um please next time karka sake haka, tam yace tare da mitsin shi na wasa kaci abinci, no! me yasa baka jin yunwa ?so kake ciwo ya cigaba da riqe min kai ko?" plate majeed ya janyo ya zuba abinci shinkafa da miya tasha naman rago a hankali ya shiga feeding din sadiq yana amsa cike da son dan uwa na shi yana ci yana jan shi da hira mai cike da nishadi. dariya sadiq yake can kuma yayi shuru yana bin majeed da kallo , murmushi majeed yayi tare da aje plate din yace "Kallan fa?" smile Sadiq yayi yace "Ba komai" juyawa majeed yayi ya kalli fatuha yace "Sweetheart ku tashi muje na saukeku gida" ok fatuha tace tare da tamiqewa . basma ko pack ta ma sadiq tare da mai sai da safe ta fita. hadiyar zuciya ne ka dai fatuha ba tayi ba sannan suka fice har sun kai bakin kofar mota, fatuha tace "Tayi mantuwa" sa sauri ta koma daki'n sadiq lokaci idanuwashi na lumshe.

A hankali fatuha ta qaraso ta shafa sumar kanshi. bude ido yayi yana kallan ta yace "Fatuha kin dawo ne ki kulla da uncle?" murmushi ta saki tace "Mantuwa nayi um" mekika manta? pack ta mai a goshi sannan tace "Kaga abinda na manta" smile sadiq ya saki tare da janyo ta ta fado saman qirjin shi har tana jin bugun zuciyar shi ,lips din ta yabi da kallo a hankali ya daura finger din shi saman lips din fatuha. kallan shi take me cike da kauna haka shima tafiyar tsutsa sadiq ya rinqa yi mata a lips din . riqe hannu tayi tare da dan cizan shi dariya fatuha ta saki dan shagwabe fuska yayi ta koma kamar baby face , sorry fatuha tace tare da riqe kunnan ta. ja mata hanci sadiq yayi tare da yi mata pack a kumatu, um uncle bari na tafi nabar mutane na jirana a waje ?sauri tayi ta daga daga saman bed din riqe hannun ta sadiq yayi yana binta da kallo itama shi take kalla sannan tasa kai ta fita. tana fita taci qaro da majeed gabanta ne ya yanke ya fadi lokaci daya .ta dan da birce kallan ta kawai majeed yayi bai ce komai ba suka shige mota suka bar asibitin.

Kwanan sadiq uku asibiti aka sallame shi. sosai ya samu kullawa wajan yan'uwan shi tare da soyayyar su, zaune suke saman dining area suna lunch har da basma saboda yanzu ta dawo gidan da zama angel na gefe tana zubama sadiq shagwaba sai ya kai ta shan ice cream mom sai tsiya take mata, basma ce ta kalli sadiq tare da jefa mai kallan so murmushi ya mata wanda iyakar shi laban shi fatuha na zaune tana lura da hakan gabaki daya annurin ta ya dauke dan ji take ma abincin ya isheta. ture plate din tayi tare da tashi ta barwurin kallo sadiq ya bita da shi tana shiga bedroom ta fada saman bed tare da sakin kuka ,sai da taci kuka ta gaji sannan ta bude bedside drowa wani album ta curo tana kalla pics din tane ita da angel da sadiq tana kallan tana dariya da murmushi mai kuka. haka ta rinqa kallan pics din har bacci ya dauke ta,

Bayan sun gama lunch suka koma parlour suna kallo basma sai jan sadiq take da labari tun be biya mata har ya dan fara sakar mata. amma duk bayan mintina sai ya kalli bedroom din fatuha sallamar majeed ce ta katse mai tunani, da sauri basma ta qarasa wajan shi bros I miss u? miss u more sis yasu umma ta fada suna nan lafiya lau, dan bata fuska majeed yayi matsala

ta dake shegyan surutu ko bari bakiyi na huta kin fara tanbayata, haka zaki rinqa yima sadiq? murmushi ta saki tare da rufe fuskarta tabe baki sadiq yayi tare da kauda kai. qarasowa majeed yayi ya zauna kusa da sadiq suka gaisa, sannan yace ina my love? wani irin kishi ne ya rufe sadiq shuru yayi be tanka ba. basma cikin zakuwa tace tana bedroom zunbur ya miqe ya shige a hankali ya bude kofar kwance ya hango ta saman bed smile yayi tare da qarasowa, bacci take rungume da album din a hankali yasa hannu ya zare album din bude album din yayi yana kalla pic din ta da sadiq ya fara gani, kanta na bisa kafadar sadiq suna dariya ya Dade yana kallan pic din, sannan ya bude d'aya shafin ya gansu su uku cikin pic din suna shan ice cream haka majeed ya rinqa bin pics din yana kallo musanman in yaga wanda fatuha da sadiq ne pic din har mamakin irin shaquwar da sukayi yake be taba tunanin shaquwar su har ta kai haka ba ,aje album din yayi yana qoqarin fita yaga sadiq bakin kofa fuskarsa a ha...

*Kuyi hakuri da wanan ina busy Im sorry fan's👏 insha Allah zuwa gobe zaku samu page mai yauwa love u all*

*ku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www. Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.CM

87_88

*_this page is for u Anuty Raheenat ina jin dadi yadda kike bani goyan baya tare da min good editing and every single person that always comment on this novel, I am in love with ur comments_*

Firgigit sadiq yamike yana sauke ajiyar zuciya, ya jiqe sharkaf da zufa da kyar ya iya miqewa ya bude fridge ya tsiyayo ruwa yana sha . tarine ya zomai lokaci guda da gudu ya shige toilet yana yi jini na fita da kyar ya saita kanshi ya dawo saman bed yana furta duk addu'ar da ta zo bakin shi. bai taba mumunar mafarki irin h'aka ba, kuka ne ya kubuce mai dan baya fatan ranar da majeed zai rasa rayuwar sa saboda furicin shi a kan fatuha, wayar shi yayi sauri rarimowa ya fara kiran layin majeed kira biyu zuwa uku majeed ya dauka da alamama yayi nisan bacci, hello baby, hamdala sadiq yayi tare da sauke ajiyar zuciya, dama wani abu zan tanbaye ka tunda bacci kake shikenan sannan sadiq ya katse wayar tare da komawa toilet ya dauro alwala yana rokwan Allah ya rage mai san fatuha a rai shi.

Kiran sallah asuba ne ya tashi fatuha alwala kawai ta daura tare da gabatar da sallah .bayan ta idar ne ta wuce daki'n angel a hankali ta murda kofar taci sa'a ta bude cikin natsuwa ta shigo angel da fitowar ta d'aga toilet ke nan daure fuska tayi tare da janyo hijabin ta tada sallah. baki'n gado fatuha ta samu ta zauna tana jiran jidda ta idar da sallah, ko da ta idar bata kalli inda fatuha take ba sai qoqarin barmata daki'n da take. riqe hannun ta fatuha tayi cikin sanyi murya tace "Angel fushi kike dani ko?" shuru tayi kamar ba da ita fatuha take ba sai ma qoqari zame hannuta jin ta kasa zamewa ya sata saki'n kuka tana cewa, "Ni ki kyale ni tunda baki san babana? kin zabi ki zauna da wani ba daddy na ba" hawaye ne suk'a fara yima fatuha zarya tana girgiza ma jidda kai, tace "Angel ya za ayi nace bana san abban ki? please ki daina fushi dani fatuha ta fada tana shafa fuskar angel" cire hannu angel tayi tace "Idan har kuna so ku ga farin cikina to ku fasa auran da zakuyi d'aga ke har daddy ta fada cikin d'aga murya sannan ta fita ta barma fatuha daki'n" kuka fatuha ta saki na shiga uku wannan wani irin abune gabaki d:aya duniya ta mana kunci. ya Allah ka kawo mana mafita fatuha ta fada tare da tashi ta bar daki'n.

Haka angel ta rinqa fushi da su fatuha Dan ko saurarasu ba tayi .duk abin yabi ya dame su idan kun angel na magana to da mom tak'e gashi ta daurawa basma karan tsana dan ko bari batayi ta taba abu itama ta taba. abin duk yabi ya damu Sadiq tun basma bata dauka abinda zafi har abin ya fara bata mata rai ga uban na mata diyar na mata,

Yauma kamar kullun mai gyaran jikin ta zo. kurkur tayi masu tabi ko ina na jikin su dashi da saqoqo sannan ta had'a masu Zuma cokali 3 madara peak ta ruwa rabin gwangwani da white egg 3 da lemon tsami d'aya ta had'a ta buga su ta murje amaran dasu ga wasu turaru ka masu kamshi da suke wanka da su a tsimin lale. tuni fatar su ta fara canza launi ga wani sheqi da suke abunka da fararen mata ko kaya suka cire kamshi suke.

Bangaran kayan ni'ima ba'a magana dan wasu mom da kanta take h'ada masu ,na kaza dana tantabara gashi kullun sai an basu madara da zuma sun sha kayan fruit ko har turewa

suke su Kansu sun san tsumu nayi masu, mom ta saki murmushi tace "Kai amma wannan gyaran yana yi sosai? ji yadda suka murje yaran nan nan ku ni da nake mace ina taba fatar su biyo ni take ina jin dadi bale kuma angwayan" rufe fuskar su suka dan mom ba qaramar kunya ta basu ba. bayan a kama gyaran jikin mom ta raka batul mai gyaran jikin har baki'n motar ta sannan ta juyo ko da ta dawo cewa tayi su fatuha su h'ada duk abinda suke buqata dan jibi za'a koma family housa a fara gudanar da biki,

Jikin fatuha ne yayi sanyi ,dan yanzu har ta fara fidda tsamani ya zamar mata dole ta koyawa kanta son majeed. Ko da ta shiga bedroom dinta kayan ta ta shiga hadawa tana hadawa tana sana'ar wato kuka sannan ta aje trolley din a gefe,

Baki'n wani hadadan gida naga sadiq ya tsaya da motar shi horn yayi mai gad'i ya bude gate. gaishe shi mai gadi'n yayi a taqaice sannan yayi parking din motar suka fito tare da majeed kallan gidan majeed yayi yace "Big man gaskiya gidan nan na da kyau?" murmushi sadiq yayi yace "Taho mu Shiga" babu abinda ba'a zubaba na mure rayuwa ciki'n gidan .iyakar haduwa ya hadu, sai dai kash ba muradin ranshi bace zata kasan ce da shi ba a wannan gidan hak'a suka gama zagaya gidan sannan suka wuce gidan majeed masha Allah shima gidan iyakar haduwa ya hadu dan sun kashewa gida jan kudi bana wasa ba. bayan duk sun gama dubawa sadiq ya aje majeed a gida sannan shima ya nufo gidan Su,

Cikin sallama ya shigo angel na parlour zaune tana kallo ,ciki ciki ta amsa sallamar tana qoqarin barin parlour janyo ta sadiq yayi tare da langwabe kai yace, "Angel nasan sarai kin san ba kyau fushi da iyaye ?me yasa kike fushi da daddy kin ?um nasan nayi laifi amma ya kamata by now an yafe min" kuka ta samai tana cewa "Ni daddy Anuty fatuha nake so?idan ka aure ta ma hama min komai" d'ago da fuskar ta sadiq yayi yace "Me yasa bak'i san Anuty basma? tana fa sonki angel ?tana maki'n duk abinda kike so?" bata rai tayi tace "Ni bana son ka aure ta that is all ,ni Anuty fatuha nake so fuuuu ta wuce sadiq tayi dak'i" tsaye sadiq yayi yana mamakin irin kafewar jidda .fatuha dak'e qoqarin fitowa d'aga kitchen tayi lamo tana jin duk abinda suke. haurawa sama yayi ya wuce part din shi fatuha tana ganin haka sai ta bi bayan shi a hankali ta bude kofar daki'n. tsaye ta ganshi a hankali ta Isa ta rungume shi ta baya wani irin yar sadiq ya ji har itama fatuha di'n, juyo da ita yayi yana smile dan ja mata hanci yayi yana binta da wani irin kallo ba qaramin kyau tayi mashi ba. a hankali ya kai mata pack a goshi itama pack ta mai tare da zame jikin ta ta zauna zaman sofa, biyota sadiq yayi tare da yin kneel down a wajan yana kallan kyakyawar fuskar ta, yace "Fatuha kinyi kyau?" yar dariya tayi tare da rufe fuskar ta. murmushi sadiq yayi a hankali yasa hannu ya cire hannu ta dak'e fuskar ta. hawaye ya gani suna mata zarya, langwabe kai sadiq yayi dan shima da zai samu dama da kukan zaiyi. tashi yayi ya zauna saman sofa tare da janyo ta jikin shi yana lalashi'n ta, "Please fatuha ki daina kukan please bana so?" lamo tayi a fafadan qirjin shi tana jin bugun zuciyar shi tare da wani irin feeling na da ban wanda bata taba jin shi ba sai akan Sadiq, hak'a yake ji a hankali take sauke ajiyar zuciyar. d'ago da fuskar ta sadiq yayi yana bin ta da kallo mai cike da so. zuciyar shi sai

bijuro mai da wasu abubuwa tak'e zame jikin shi yayi tare da komawa saman bed ya zauna yana kallan fatuha,  itama di'n shi take kallan. kauda kai tayi tana wasa da yan yatsun hannun ta. miqewa tayi tana qoqari tashi sadiq ya ruqo hannu ta tare da janyo ta ta fada jikin shi, murmushi ta saki tana kallan shi a hankali ya daura lips din shi saman nata ya fara kissing nata kasan cewa fatuha tasha tsimi har ta gaji hakan  yasa ta kasa hana shi.  sai da yayi kissing nata san rai shi sannan ya sake ta, yana bin ta da kallo yana sauke numfashi cikin cool voice sadiq yace "Fatuha!" lamo tayi tana jin shi dan har bata san abinda zai sa ta matsa kusa dashi. shafa gashin kanta ya Shiga yi a hankali  hakan ba qaramin dad'i yake ma fatuha ba can kamar an mitsine sadiq ya miqe yana tari da sauri ya shige toilet fatuha ta biyo bayan shi tun kafi ta iso ya kule toilet din da key dan baya so taga halin da yake ciki ,tari yake mai jini ya Dade a toilet din yana abu d'aya. fatuha ko duk ta rude sai faman kiran suna shi take yana bude toilet tace  "Mai kyau me ke damun ka please ka fada min?" ta fada ta shafa mai gefen fuska ,saman bed ya hau tare da cewa b)"Ba komai kawai na kware ne haka fatuha ta rinqa mai sannu sannan tasa kai  ta fita.

*Washe gari*

Bayan fatuha tayi wanka ta shirya cikin lace dinta maroon mai kyau masha Allah tayi kyau har ta gaji. ko da ta fito parlour ba kowa bedroom din angel ta shiga kwance ta hango ta dan girgiza kai fatuha tayi tare da bud'e wardrobe din ta tafido trolley din ta ta fara zuba mata kayan ta sai da ta gama zuba kayan tsaf ta aje trolley din tana qoqarin fita angel ta tashi "Anuty?" tace cikin sanyin murya juyowa fatuha tayi tana kallan jidda idanuwan ta tap da kwalla da gudu jidda ta rugu ta rungume fatuha tare sakin kuka itama fatuha kamar jira take ta fara nata kukan ba mai lalashin wani sai da suka ci kuka san ransu sannan suka yi shuru suna sauke ajiyar zuciya a tare, angel ce ta dago tace "Anuty shikenan yanzu bazaki auri daddy ba?" dan smile fatuha tayi tare da cewa "Angel bai kamata kina damun kanki ba kinji? idan kina san bina sai ki bini mu zauna tare". bata fuska angel tayi tace " Aini nafi so na ganki da daddy bada kowa ba" haka dai fatuha ta rinqa lalashin angel sannan ta tafi ,

Direct part din Sadiq ta wuce a hankali ta bude kofar part din ta shiga. parlour ba kowa sai kamshi dak'e tashi bedroom ta shiga kwance ta hango shi qudidine cikin blanket a hankali ta qarasa zama tayi gefen bed din. a hankali ta fara janye blanket din tana kallan face din sadiq a hankali ta kai mai pack a goshi , ya ware sexy eye's ball's din shi ya sauke su kan fatuha smile ya saki tare da juyawa ya gyara kwanciya dai dai saitin kunan shi tace cikin  cool voice din ta "Uncle ka tashi kowa ya gama shiryawa kai ka dai ake jira?" ware idanuwa yayi yana Kallan ta janyo ta yayi ta fad'a saman fafadan qirjin shi yace "Fatuha me yasa kike so ki katsemin bacci?" um lamo tayi a qirjin shi tace "Saboda na rinqa kallan ka kafin muyi nisa da juna ta fada idanuwan ta tap da kwalla" tashi zaune sadiq yayi yana facing nata shima ji yake kamar yasa kuka, langwabe kai fatuha tayi tace "Ka h'ada kayan ka ne?" no, ok bari na h'ada ma,

Haka fatuha ta shiga hada ma sadiq kayan shi yana kallan ta saida ta gama hada kayan tsaf tabi daki'n da kallo. kuka ya kubuce mata saboda tunowa da rayuwa da sukayi yanzu rayuwar ta zama tarihi kuka take sosai, janyo ta sadiq yayi jikin shi yana lalashi a hankali ta fara magana, "Mai kyau me yasa mutum baya samun abinda ya ke so a lokaci da yake so? ta fada tana qara rushewa da kuka" a hankali sadiq ya lalubo lips din ta ya fara mata hot kiss wanda shi kanshi bai san yana hakan ba, bai kyle ta ba har sai da ta tsaigai ta kuka. sannan ya sake ta yana maida numfashi. h'ada face nasu yayi guri guda yace "Fatuha please ki dai kuka? , dama shi rayuwa bai zama dole ma same duk a bind a make so, muyi hakuri jarabawa Che saga Allah ,insha Allah zai Bamu Sak'a mak'o Mai kyau , Dan h'aka muyi adu'a Allah yasa h'akan shine Mafi alheri a garemu , kuma ki Daina kukan h'aka domin Hana ta Dan min da hankali a duk sanda naji. d'aga kai tayi tare da kauda kanta dan gabaki daya kunya ta lulube ta. tashi tayi ta fita da sauri daga bedroom din, ko da ta fita jingina tayi da kofar tana maida numfashi a hankali ta daura hannuta saman lips din ta. ji tayi kamar an yaye mata baki'n cikin dake damun ta sannan ta fito da gudu d'aga part din haka shima bangaran sadiq h'aka yaji.

Bayan kowa ya gama h'ada kayan shi su ola suka wuce da su boot. ga baki d'aya fatuha jiki'n ta yayi susuku, h'aka sukayi mota 5 fatuha ta dade tana kallan gidan sannan suka bar harabar gidan tare da harbawa kan titi,

Bayan sun Isa family house dangi har sun fara cika, take jikin fatuha yayi sanyi dan tasan tabas ta rabu da sadiq har abada, h'aka shima bangaran sadiq hakan yake ji a Randa,

Bayan sun dan huta kowa ya aje kayan shi inda ake ajewa, aka kira mai lale ta fara yima amaran lale kafin ka ce mai qawayan amaran sun fara halara Zara da Nana har sun zo sai rawar kai suke zubawa. sallamar da akayi ne yasa fatuha juyowa cikin fara'a ,waza ta gani inba fatsima ba. da gudu ta ruga ta rungume ta na murna h'aka itama tuni daki'n ya dau shewa duk da fatuha ba jin dad'i take ba amma ganin fatsima ba qaramin dadi ya mata ba, hakan yasa ta fara walwala.

Bangaran basma ma haka qawayan ta duk sun hada yan gayu masu ji da aji sai shewa suke suna taya basma murnar samun handsome kamar captain sadiq .sai pics suke kamar ba gobe kowa ce ka duba face nata kasan cikin farin ciki take,

Angwayan ma friends nasu da suke qasashan waje har sun fara sauka, haka part din nasu ya cika tap duk wannan abunda ake sadiq na gefe ya zuba masu Na mujiya kamar ba abinda ke damon shi. sun san halin miskilan cin shi shiyasa ba kowa ya damu da h'aka ba sai Dr yakub

dak'e ta faman lura da shi dan yasan sarai ciwo ne ke cin shi kowane lokaci zai iya ta shi..

*_fan's kuyi h'akuri da wannan page din ba yawa, saboda ina schl shiyasa. amma insha Allah gobe zan maku page mai yawa_*

*Taku har kullun Salma mas'ud Nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

89_90

Shirye shirye suke sosai kasancewar yau ake kamu. da misalin karfe 4:00pm kowace ka gani shiryawa tak'e ciki'n ashobe. Fatuha da ke zaune cikin toilet tana sana'ar kuka knocking din kofar da akayi ne ya sata miqewa tana share hawayan ta, hanan dak'e baki'n kofar tace "Fatuha ki fito me make up ta zo har an gama ma basma ke ka dai ake jira?" to tace tare da yin sauri ta watsa ruwa ta fito,

Ko da ta fito shahararriyar me make up fandi ta zo fatuha kawai take zaman jira. tana daure da towel ta fito ta sauna tana shafe jikin ta da mai. Anuty bilki ce ta shigo da kayan da zasu sa

washe da baki ta aje kayan, a'a fatuha dama ba'a gama make up din ba d'aga kai fatuha tayi , ya kamata kuyi sauri ku shirya kar ku bata lokaci saboda da kun dawo zaku dinner to tace sannan Anuty bilki tasa kai fa fice. a hankali fandi ta fara tsantsara mata make up kafi'n ka ce me fatuha ta fito wasu maroon materials tasa gown mai Stone's masha Allah tasha kyau har ta gaji, ga head tasha ita kanta me make up ta yaba da irin kyan da fatuha tayi . su fatsima ne suka shigo sanye da ashoben su ash atamfa mai ratsin maroon suma sun sha head kun san a tare suka fito da basma kusan kaya colours daya suka sa har yan mata amaryar anko daya su kayi. motoci ne masu numfashi da tsada suka faka amaran suka shige ba a zame ko ina ba sai meenah event hadadan hall na party iyakar haduwa hall din ya hadu. kuma ya qayatar kasancewar kamun na mata zala ne shiyasa ba ango ko daya sai yan'mata da iyaye yan asharale ne suka fara buga ganga tuni hall ya dau sauti amaran zama su kayi ma zaunin su aka fara gudanar da shagulgula. can na hango su fatsina da nana da Zara anshige fili anata kwaso shoki haka suma qawayan basma biki yayi biki sai dai muce alhamdulillah .

Fatuha ko duk wannan bidirin da ak'e zuciyar ta naga muradi'n ranta, ji take kamar ta rushe da kuka kallan kowa take da ke farin ciki da walwala angel ta hango itama ba laifi ta saki jikin ta tana warwasawa,

Anci ansha inda aka raba turaru kan wuta da atamfofi masu tsada sosai aka raba kaya kamar ba'a so, sai kunsan yama liqis taro ya watse suka dawo gida,

Ko da suka dawo wanka amaran suka qara tare da dauro alwala suka gabarta da sallah magrib da isha, sannan amaran aka fara shirya su cikin wani wanka ni kai na har mamaki nake irin shirin da akayi ma bikin. lace suka sa blue mai ratsin dark blue mai shegen tsada ga make up da aka qara zuba masu sai kamshi suke yan matan amaraya ko pink lace suka sa mai ratsin white kowa ce tasha make up fatuha ko saboda tsabar kyau kasa gane ta kake ,dan ba qaramin kyau tayi ba kuma ga anuri da y'a sauko mata na amare. basma ma ba'a barta a baya ba tayi kyau bâ l'ai fi,

Shiryawa angwayan suke cikin getzner shad'a blue tasha aiki da dark blue zare ,duk wannan shirin da sadiq keyi jin shi yake susuku dan kwata kwata baya tare da walwalar shi , links yasa ma hannun rigar shi sannan ya daura agogan shi hublot tare da zura takalmin shi black mesarath tuni ya fito yana sheqi da wani irin kyau sajan shi yayi lufluf ya kwantan can gashin shi ya leqo ta cikin wula .feshe jiki'n shi yayi da turare masu kamshi da sanyi dadi kusan shigar su iri daya da majeed shima ba'a barshi baya ba Dan yasha kyau har ya gaji, sai murmushi yake saki fararan haqoranshi na bayana , abokanan angwayan ma ba'a bar su abaya ba Dan suma sunsha kyau Khaleed sai rawar kai yake zuba wa haka shima Dr yakub ba'a bar shi a baya gayu su kayi na sosai ,

Cikin natsuwa suka fito suka shige moto cin su mais alfarma da tsada, dan a da'ko amaran ko da suka iso amaran sun shirya tsaf motoci aka fara shiga kowace amarya ta shige motar angwanta,

Murmushi majeed ya saki yana bin fatuha da wani irin kallo mai cike da so da kauna, a hankali ya kai hannu ya taba hannu ta tare da kallan lalan dake hannu ta yace, "My love lalan nan yayi kyau?" smile tayi wanda iya karshi laban ta tare da qara manewa karshan kofar tana tuna abin santa.

Kallo sadiq yabi basma da shi ba laifi ta mai kyau. yau ce rana ta farko daya fara ganin kyan ta ayanawa yayi a ranshi, tunda ya ga basma haka to ya fatuha zata kasan ce? wani irin kishi ne ya lulube shi tare da qunar zuciya juyowar da yayi ne su kayi ido hudu da basma smile ya sakar mata tare da kauda kai,

A dai-dai affcent center motocin suka faka lokacin har wasu sun halara tun daga bakin hall din kana jiyo irin sautin dake tashi ,wajen y'a hadi bâ karya, ga wasu kujeru sa ak zagaye haldi'n farere Tass, jerawa yan'matan amarya su kayi shigar farrar matériel sulayi sa baki'gwagwaro sa a la d'aura mais a k'ai, Angwayen KO bakin Sweet suka sa y'a sa farar taklmi m'asha Allah shigar ta su yayi kya, amaran suka shiga tsakiya sadiq sai bin fatuha yake da kallo bugun zuciyar shi na daduwa, ita kanta fatuha ta qasan ido take kallan sadiq tare da jin kishin shi,

A natse suka shigo hall din, nan tale wajen y'a gwarare da shewa da ihu, tuni aka canza salan kida da sauti majeed hannu sa na maqale dana fatuha yadda ya shige mata kamar zai maida ta ciki .sadiq ya cika tap dan har ya fara ganin jiri riqe hannu basma yayi dan ba yadda zaiyi dan baya so ya bata ma qanshi rai .ko bai so basma so na aure ba yana sonta a matsayin ta na kanwar shi , ko da suka shigi gurin zama suka yi aka fara gudanar da shakali, can na hango su Anuty Raheenat anata kai kawo anzu shagali😜 ashe abin ba ita ka dai bace har da yan Real Hausa fulani writers. can na hango Fulani da Anuty Rahama nalele suna rab a ma mutane kayan motsa a baki, nima dai ba'a barni a baya ba Dan na Shiga a dama dani shoki kawai ake kwasowa.

A hankali majeed ya matso daf da kunan fatuha yace, "My love yanzu fa gobe kin zama tawa ko? yana magana yana wasa da yan yatsunta" sadiq dak'e gefe yana kallan su baki'n ciki na cin shi, dafe kirjin shi yayi domin yafara yi ma sa nauyi , a hankali ya miqe ya bar guri tunda ya fito d'aga hall din jiri ke di barshi, KO gaban sa baya gani. Sa kyar y'a isa inda yayi parking fin motarsa ya ya daura hannu shi kenan ya ji an riqe hannun. waigowa yayi su kayi 4 eye's da Dr yakub girgiza kai Dr yakub yayi yace sa...!! be ida rufe baki'n shinba sadiq ya fadi jikin shi sumame rudewa Dr yakub yayi yasa sadiq a mota ya bar harabar gurin da gudu.

MC yaba amarya da ango damar su yanka cake ,saukowa sukayi a hankali daga sama. majeed ya yanka yaba fatuha a baki hall din ya dau ihu sadiq aka kira da basma amma ba ango ba alama haka MC ya rinqa kira ango ganin abin kunyar dak'e shirin faruwa yasa Khaleed hawa a matsayin ango yaba basma cake a matsayin sadiq tuni hall ya dau tafi, basma iyakar cika ta cika bata taba jin bacin rai ba irin na yau, yaune ta tabatar da sadiq be Santa kuma ba zai taba Santa ba tunda har ya iya wulaqantata gaban bainar jama'a. idanuwan ta ne tap da qwalla, tana tausayawa kantada Irina rayuwar sa zatayi a gidan SadiQ. haka akayi turo kusan duk abinda ango zaima amarya Khaleed ne yayi ma basma.

Ko da fatuha ta juya bata ga sadiq ba tuni idanuwan ta suka kawo ruwa. dama shi take gani tana jin sanyi a ranta .

Ko da Dr yakub yaja mota basu zame ko ina ba sai asibitin shi ,suna shiga aka turo gadan daukar marasa lafiya sadiq da yanzu idanuwan shi sun fara budewa haka yake ganin asibitin na juyamai oxygen ne manne a hanci shi numfashin shi sai sama sama yake Dr yakub ko har ya fara matsar kwalla. emergency aka wuce da shi doctor sun Dade a kanshi Dr yakub ma kasa shiga yayi sai zarya da yake a baki'n kofar kusan 1 hour suka dauka sannan aka fito da sadiq sanye da oxygen a hancin shi daki aka bashi tare da samai life sport machine sai qarin jini da ake mai a hankali Dr yakub ya qaraso gaban shi tare da yin kneel down gaban gadan sadiq, hawaye ne kemai zarya a hankali ya kai hannu ya shafa sumar kan sadiq yace "Friend why me yasa kake bama kanka punishment haka? why sadiq ya ida zancan hawaye masu zafi na gangaro mai wayar shi ce dake ringing ciki aljihu ya tsuro tare da kallan suna dake maqale a screen din majeed kashe wayar yayi gabaki daya tare da janyo wayar sadiq ya kashe sannan ya dau kayan sadiq da aka cire mai yaba daya daga cikin ma'aikatan asubitin su wanke.

Bayan ankamala dinner kowa ya dau hanyar zuwa masaukin shi majeed sai kiran Layin sadiq yake baya Shiga dana Dr yakub. hakura yayi da Kiran tare da maida wayar aljihu.

Bangaran basma ko kuka take sosai tare da taqaicin amincewa da auran sadiq ,Khaleed sai bata hakuri yake tare da ganin rashin kyautawar sadiq ya rasa dalilin da zai mata irin wannan cin fuskar bayan tana qanwar shi kuma matar da zai aura, shi a ganin duk wanda yasa mu basma a matsayin mata ya mure ya rasa me yasa sadiq ke nuna rashin ko in kulla a kanta da wannan tunanin suka qaraso gida ko Godiya bata mai ba ta shige gida da sauri tare da tsananta kukanta.

Motar su fatuha na fakawa majeed ya fara jero mata kalaman soyayya tare da jan ta a jiki, ganin zai wuce Gona da iri yasa fatuha saki'n kuka lalashin ta majeed ya Shiga yi tare da yimata pack ko saurara shi ba tayi ba ta bale murfin motar ta fita da sauri.

Bangaran sadiq ko bashi ya tashi ba sai wajan 2:00am na dare a hankali yake ware sexy eye's ball's din shi da wani irin ishin ruwa ya tashi. Dr yakub da ko rintsawa baiyi ba ya miqe da sauri ya qaraso wajan shi cikin cool voice sadiq yace "Ruwa" da sauri Dr yakub ya bude fridge ya dauko rubar ruwa ya bashi ko da ya sha ruwan miqewa yayi yana qoqarin cire jini da ake qaramai riqe, hannu Dr yakub yayi yace, "Captain me kake shirin aika tawa? ya fada bakin shi na rawa" kallan shi sadiq yayi yace so nake na tafi gida bana so majeed ya gane bani da lafiya ya ida zancan yana cire Karin jinin wasu hawaye ne masu zafi suka zubu ma Dr yakub yace, "Sadiq wai me yasa kake so ka raya rayuwar wani ka bata taka? why sadiq Dr yakub ya fada yana jijiga sadiq" kuka sadiq ya Saki tare da cewa "Bazan taba bari majeed ya mutu saboda bakin ciki na ba nafi san farin cikin majeed a kan na kowa a duniya bani da dan uwa sama da majeed saboda haka ban taba bari saboda ni ya rasa rayuwar shi sadiq ya ida zancan yana kuka mai tsuma zuciyar mai saurare" a hankali ya ida cire kayan asibiti tare da zura kayan shi wayar shi ya dauka tare da kunna ta Dr yakub mutuwar tsaye yayi yana bin sadiq da kallo tabas yanzu yasan me sadiq yake nufi so yake ya rasa rayuwar shi ya zamamar dole ya kawo karshan abunan ko saurarashi sadiq beyi ba saima car key daya dauka tare da fita yana ingisawa.....

*_Muje zuwa fan's_*🤪

*Kuyi hakuyi Sa wannan bâ yawa*

*_taku har kullun salma mas'ud nadabo_*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

91_92

A hankali yayi parking motar shi tare da yi mata key. harabar gidan tsif ba motsin kowa sai motoci birjik kamar wanjan saida mota. a hankali ya cigaba da takawa duk da yana jin jikin shi kuka kuka ya fara ji sama sama hakan ne ya sasa tsayawa tare da kallan agogo hannu shi mamaki ne ya lulube sadiq a hankali ya fara bin inda kukan ke fita fatuha ce zaune sama resting chair tana rai ra kuka. qarasowa yayi gaban ta firgigit ta daga a dan tsorace ganin sadiq ne yasa ta fada jikin shi tare da sakin wani kukan, daurewa yayi tare da zamewa ya janyo ta suka zauna a hankali yake shafa mata bayanta ba wanda yace ma dan uwan shi komai ,sun dau kusan 5 minutes a haka fatuha ce ta dako tana kallan sadiq ciki'n sanyin murya tace 'Uncle" ya naji jikin ka zafi? dan smile sadiq yayi yace "Nima haka naji jikin nawa" kallan shi take cike da tanbayoyi amma sai ta kasa tare da komawa tayi lamo a fafadan qirjin shi kunsan a haka suka zauna har bacci ya dauke fatuha idanuwan sadiq biyu yana kallan fatuha har sai da ya fara jin kiran sallah asuba sannan ya tashe ta.   sannan yace "Dear tashi asuba tayi?" qarayin lamo tayi a jikin shi shafa gashin kanta yayi yace "Fatuha" a hankali ta ware eye's ball's din ta, tace "Na'am" tashi mu shiga gida jiki ba qwari ta tashi har tayi gaba ta tsaya tare da cewa "Yau ne zan rasa farin ciki na! yaune mafarki na zai rushe" wasu hawaye ne masu zafi suka sulalo mata tace, "Yanzu duk wani rayuwa da mukayi zata zama tarihi mai kyau? ina ma fatan alheri Allah ya baku zaman lafiya da basma tana ida zancan ta fashe da kuka mai ban tausayi" a hankali sadiq ya janyo ta jikin shi ya rungume shima hawaye na mai anbaliya cikin sanyi murya sadiq yace "Fatuha ki kasance mai biyaya a daki'n mijin ki? majeed na sonki please karki bari majeed yayi kuka dake dai-dai da rana daya? duk wanda yayi hakuri a rayuwa zai ga ribar haka ya ida zancan yana share hawayan shi tare da sakar ma fatuha lalausan murmushi"  itama shi ta mai tare da shigewa cikin gida.

Duk inda ka wuce had'a had'a ake na shagali abinci ke ta yawo da kayan motsa  baki, kaji ko har ture su ake da naman rago yan'matan amarya na zaune a dak'i sai shirya fatuha ake saboda wudil za'a wuce da ita sai an daura aure aje dako ta. tunda ake mata make up take kallan agogo tana irga mintinan da suka rage ta zama malaqi majeed. hawaye ne tap da idanuwan ta bayan angama make up din ta zura kayan ta atamfa mai ratsin green pink brown masha Allah kayan sun mata kyau tasha danqareriyar sarqa ta gold da yan hannu sai sheqi take.  Anuty bilki ce ta leqo tace, "Fatuha ku fito ga moto cin da zasu kai mu wudil?" gaban tane ya yanke ya Fadi dan har wani jiri take gani a haka su fatsima suka sata tsakiya aka lulube ta anata zuba guda, mota suka shige driver ya jasu suka har ba kan titi.

Wanka angwayan kawai suke suna shiryawa Khaleed ne ya kalli sadiq tare da aika mai harara tare da cewa "Wai ina kaje jiya?" bala mai harara sadiq yayi yace "Ina ruwan ka da inda

naje? kai dai wallahi ka fiye sa ido? irin kune ana ruwa kuna irgawa" dariya majeed yayi yace "Kai dai tashi kayi wanka kaji baby ga kayan ka can tun dazu na aje ma ina so yau ka kasance cikin farin ciki kamar yadda kowane ango keyi majeed ya ida zancan yana zura kayan shi" a hankali sadiq ya miqe ya shiga toilet majeed .ya bishi da kallo tare da ida shiryawa tunda sadiq ya shiga toilet yake kuka kamar qaramin yaro sai da yayi san ransa sannan yayi wanka ya fito. ko da ya fito Dr yakub ne ka dai daki'n kallan shi sadiq yayi tare da kauda kai ya cigaba goge jikin shi da qaramin towel, sai da ya gama shafe jikin shi da lotion mai kamshi da sanyi dadi sannan Dr yakub ya balo magani ya miqawa sadiq dan bata fuska sadiq yayi yace "Wannan fa?" daure fuska Dr yakub yayi yace "Magani mana" bai ida rufe baki'n shi ba akq turo kofa aka shigo .murmushi sadiq ya saki tare da qarasawa ya rungume jawad zame jiki yayi tare da bata fuska yace, "Sai yauma zaka zo?" smile jawad yayi yace "Sorry baby tun jiya na zo kuma na zo nemanka aka ce ba kanan" dan lagwabe kai yayi tare da cewa "Toh shikenan, ina Anuty shukura?" tana wajan mom ok hadadiyar fara shada ya janyo white getzner  tasha aiki ta gaji malin malin  su jawad ne suka taimaka mai ya shirya tuni ya fito yayi kyau bayan sun gama shiryawa suka fita,

Zaunawa sadiq yayi tare da kallan agogo dak'e manne a bago'n daki'n.   kusan karfe 1:30pm saura minti talatin a daura auran su. hak'a ya rinqa dane zuciyar shi yana bata hakuri.

Suna Isa wudil  gida ya dau gud'a baba jinmai ta fito da sauri tana cewa "Ladingo amaryar fa ta iso ?" inna washe da bak'i ta bude masauki da su fatuha zasu sauka kusan tare suka shigo. Anuty bilki na riqe da ita masaukin suka sauka nan aka fara jera masu kayan motsa baki, yan'matan amaryar ko alwala suka fara daurawa suna sallah kasancewa azahar tayi haka itama fatuha ta gabatar da sallah sannan suka zauna aka fara gudanar da biki. gwago ce ta aiko a kira fatsima tashi tayi ta fita har Nana zata bita sai kuma ta dawo ta zauna ko da fatsima ta Isa gidan su shima cike yake da baqi ,babban abinda ya daura mata kai har da dangin baban ta, to ko suma biki'n fatuha suka zo? watsar da zancan tayi tare da shigewa daki inda gwago take washe da baki gwago ta tarbi fatsima ta fara mata magana duk yadda naso naji me ake cewa na kasa ji. hakan yasa ni da Anuty Raheenat muka bar gun jiki a sabule lol.

Duk inda ka waiga a cikin masallaci Sheikh Isyaka Rabi'u mosque ya cika da manyan mutune. saboda daurin auren, sadiq na hango ciki'n din bin jama'a, a Nata mai Allah ya sanya alheri duk wannan abu Dr yakub na lura da yanayin shi majeed ma sai murmushi yake saki daka ganshi kasan yana cikin farin ciki. haka shima Khaleed dan yasha kyau har ya gaji kamar ango gyara lasfika da kayine yasa gaban sadiq ya yanke ya Fadi .take wani irin zufa ta fara karyo mai da bugun zuciya, tabas yasan ana daurawa ya zama gawa wani irin jiri ya fara gani da kyar ya fara barin cikin taro ga wani irin tari  da yake don tado masa.  A hankali yake takawa dan yanzu ya fara yin nisa da masallacin,

Cikin masallaci ko *_MALAM JAURO   YA BADA  DIYAR SHI KAN  SADAKI NAIRA  DUBU

DARI GA DAN ALHAJI IBRAHIM WATO SADIQ IBRAHIM, MALAM ALIYU YA MIQA DIYAR shi KAN NAIRA DUBU DARI WATO FATIMA ALIYU GA DAN ALHAJI KHABIR WATO ABDULMAJEED KHABIR, TARE DIYAR shi BASMA YA MIQA TA GA DAN ALHAJI SANI WATO KHALEED KAN SADAKI NAIRA DUBU DARI -* kowa na masallaci mamaki ne ya lulube shi. sadiq wanda fitowar shikenan majeed ya biyo shi tare da cewa "Baby?" waigowa yayi tare da buda baki zai ce majeed jiri ya debe shi ya fadi qasa sumame" da sauri majeed ya qaraso tare da sakin kuka yana cewa "Duk laifi nane hawaye namai zarya" Dr yakub da kusan tare suka iso wurin yace "Ba kuka za kayi ba? muyi sauri mu kai shi asibiti" jikin majeed na rawa ya bud'e murfin mota yana kuka ganin ba zai iya tuqinba yasa doctor yakub ya amsa. car key din suka bar harabar masallaci da gudu kuka majeed yake yana cewa "Ban taba tunanin abin ya kai haka ba? am so sorry sadiq ka yafemin sai sanbatu yake a haka suka iso asibitin" sai da aka wuce dashi emergency sannan majeed ya zame jikin bango tare da sakin kuka. wayar shi ya curo cikin aljihu ya danna number umma bugu daya zuwa biyu ta dauka kuka majeed ya saki yana cewa "Umma saboda ni ina ji ina gani baby zai rasa ransa? Ya fadi hakan tare da sakin kuka" ita kanta umma ta tausayawa sadiq.

Kafin ka ce me, asibitin ya cika da yan'uwa. majeed na ganin abba ya fada jikin shi yana kuka kamar qaramin yaro yace "Shikenan abba baki'n ciki na zai kashe baby,?" a hankali abba ke shafa bayan shi tare da zaunar da shi d'aya d'aga ciki'n kujerin dak'e gurin. ajiyar zuciya kawai majeed ke saki ciki'n sanyi murya abba yace "Ba laifin ka bane majeed kaji? har da laifin sadiq da yayi nauyin baki ya kasa fad'a? ko yanzu da ku kayi saurin aka sauya daurin auran? indai fatuha tace bata san sa dole ya sake ta" kuka majeed ya saki tare da cewa a?"Abba wallahi da kunne na naji irin son da suke ma juna su? abba dan Allah a taimaki rayuwar baby ? ya ida zancan yana qara saki'n kuka" haka abba ya rinqa lalashin shi har yayi shuru, ammi sai da ta matse kwalla saboda tausayi , sai yanzu suka san abinda ke damun sadiq.

Abba biza yasa aka mai dan a fitar da shi waje saboda a wannan qaran ciwon yayi tsanani. dan yafi buqatar amai aiki gagawa tare da samun qwararin likito ci.

Su baffa na Isa wudil ya sanar da su an daura auran, fatuha wani irin kuka fatuha ta saki dan yanzu ta tabatar da ta zama malaqin majeed kuka take kamar ranta zai fita. lalashin ta su Anuty bilki suka shigayi da kyar aka samu fatuha ta shirya. ko da ta shirya daki'n baffa aka kaita ya mata nasiha sosai duk wannan nasihar da baffa ke ma fatuha kuka take har da sesheqa abun gwanin ban tausayi. a haka aka tataro ta aka sata mota taci kuka sosai sai anjiyar zuciya da take ta saki ,dan ko fatsima bata nema ba.

Bangaran fatsima ko su gwago sun gyara ta sosai duk da bata jin Son majeed amma a yadda ya mata bayani da yadda su gwago suka mata hakan yasa ta fara jin son sa dan tayima kanta alqawarin bashi farin ciki, haka suka shige motoci amaran aka harba da su kan titi ,

Tunda fatuha ta ga an iso kano ta qara saki'n kuka mai cin rai, sosai take kuka kamar ranta zai fita. suna isowa family house aka bude mata murfin kofar luuuu ta fadi jikin Anuty bilki sumamiya...

*Taku har Kullu salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏽

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

📘 *REAL HAUSA FULANI WRITER'S FORUM*🐄
★We are the best ★

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=H-

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFUROM.COM

93_94

Daukar fatuha akayi aka maida ta mota tare ja suka bar harabar gidan hannan sai matsar kwalla take basu zame ko ina ba sai asibitin da aka kai sadiq suna shiga lokaci majeed na qoqarin fita kamewa yayi yana bin su da kallo kamar gunki ganin fatuha yasasa bin bayan su wasu hawaye masu zafi namai zarya duk wannan abun da ya faru saboda shine shiga da fatuha emergency akayi

Bayan yan mintuci aka fito da ita dakin da aka aje sadiq aka aje ta kafin anjima jirgin su ya tashi har yanzu kwance yake bai san halin da ake ciki ba,

A hankali fatuha ta fara ware eye's ball's din ta tana bin dakin da kallo yunqurin tashi tayi ta

kasa da yar ta iya miqewa ta juyo ganin sadiq kwance  kefan ta ya sata cire drip din dake hannu ta matsa kusa da shi kuka tasa ganin halin da yake ciki a hankali ta fara cewa mai kyau meya same ka duk tabi ta rude sai fama kuka take har sautin kukan ta ya fara fita waje mom da shigowar su asibitin kenan suka shige dakin a tare kuka fatuha take tana cewa mai kyau ka tashi wallahi na rasa ka mutuwa zanyi Allah bana iya zaman aure da majeed please ka tashi ta ida zancan tana kuka mai cin rai mom ce ta janyo ta, ta rungume tana shafa bayan ta shhhh ya Isa haka fatuha ki kwantar da hankalin kinji indai mai kyau ne ya zama naki  dagowa tayi tana kallan mom da mamaki murmushi ta sakar mata tace yanzu ba kuka ya kamata kiyi ba kulla da mijin ki ya kamata kiyi idan kun dawo  kunji bayani gabaki daya wani lalausan murmushi fatuha ta saki majeed dake gefe smile ya mata sai ji tayi duk kunya ta kamata da sauri take qoqarin ta fita daga dakin basma ce ta tare da ina zaki ki kibar mijin ki, ko kin mata kema baki da lafiya kina buqatar kullawa harara wasa ta aikawa basma gaba ki daya dakin ka fashe da dariya Khaleed dake gefe ne yaja basma suka wuce gida dan ta samu hutu kafin anjima akaita dakin shi kusan a tare suka fito da majeed yana qoqarin bude mota, motar jawad ta tsaye shida shukara suka fito tare da fatima sai matsar kwalla take qarasawa majeed yayi tare da cewa a'a sai ku fito min da mata ba tanbayar izini harara jawad ya kai tare da cewa kai dai wallahi ka raina mutane ya kaimai duka ya goce yana dariya janyo fatima yayi jikin shi cikin cool voice yace my wife me ya saki kuka haka kina so ki bata min kwalliyar ki dan murmushi fatima tayi tare da rufe face nata lol su fatsima anqaro wulaqanci😜

Bayan an gama shirya komai flight din su sadiq ya tashi sai London suna isa london babba asibiti suka sauka kusan amaran tare suka tafi saboda suma honeymoon za suyi a chan Khaleed sai zuba ma basma soyayya yake haka shima majeed haka fatima ko sai kunya yake bata ko da ka wuce da sadiq asibiti emergency suka wuce da shi saboda yana buqar aikin nan kusa fatuha ta kasa zaune ta kasa tsaye sai addu'a take fatima ce ta dafata tace fatuha ya kamata ko wani abu ne ki dama cikin ki insha Allah lafiya lau sadiq zai fito haka basma da fatima suka rinqa bata baki sannan ta ci abinci, bayan ta kamala cin abincin duk da ba wani ci tayi ba su fatima suka mata sallama akan zasu wuce masaukin su, su huta anjima su dawo haka ko akayi fatuha ta dawo ta zauna haka shima majeed yana asibitin dan ba da shi suka koma masauki ba, sai kun san yama likis aka fito da saki tashi fatuha tayi tabi ganda har aka bashi dakin sannan doctor ya nemi ganin majeed magunguna ya bashi tare da mai congrat an gama aiki lafiya kowani lokaci yana iya tashi bakin majeed har kunne tare da hamdala da gode wa Allah ko da ya dawo albishirin da yayi ma fatuha kenan tare da curo wayar shi ya bama su mom albishir sannan suka shaidamai suma gobe zasu iso fita yayi ya bar dakin tare da shaida ma fatuha tare zasu dawo da su basma to ta ce mai tare da shigewa toilet dan ta dauro alwala.

Bayan ta gabatar da sallah tana qoqarin linke daduma sadiq ya fara motsawa kusa da shi ta matsa ta tsaya a hankali ya fara bude sexy eye's ball's din shi ya sauke su kan fatuha kallan ta yake kamar wanda bai taba ganin ta ba tare da fara bin asibitin da kallo, cikin sanyin murya yace ruwan, ruwa ta tsiyayo mai a glass cup ya kafa kai ya shanye tare da lumshe ido ya ware su yace fatuha na'am tace tana qoqarin taba sumar shi riqe hannu ta yayi tare da cewa ina mijin ki miya kawo kinan bai ida rufe bakin shi ba majeed yace akwai wani mijin ne bayan kai ya ida

zancan yana qarasowa gaban gadan, kallo sadiq ya bi da shi mai cike da mamaki daga mai gira majeed yayi yace karfa kayi mamaki da kai aka daura aure badani ba Ni ga matata fatima ce ta shigo tana smile basma ta biyo bayan ta tana jingine da qafadar Khaleed mamakine ya lulube sadiq Khaleed yace karfa kayi mamaki dama over taking kamin yanzu kuma na dau abita ya ida zancan yana dariyar shaqiyanci ai sai ka miqe yanzu tunda an daura da fatuha rife fuska fatuha tayi tana qoqarin barin gun riqe hannuta sadiq yayi tare da sakin smile yace kun fiye sa ido ya fada cikin cool voice saboda har yanzu be jin shi yadda yake ba amma jin wannan labari ba qaramin dadi ya mai ba sai kallan juna suke shi da fatuha, haka suka dinga raha suna bama Sadiq kulawa har ya fara jin ya warke, kiran sallah magrib ne yasa su ka fita tare da matan su dan su dauro alwala a masaukin su kasancewa masaukin ba nisa da asibiti suna fita fatuha ta tashi tana qoqarin itama shiga toilet din riqe ta sadiq yayi tare da janyo ta fado saman fadadan qirjin shi a hankali ya hada bakin su guri guda ya fara kissing nata sun dau minti suna a haka sannan ya sake ta tare da hada face nasu guri daya yana wasa da yan yatsun hannuta a hankali ya bude Baki yace my wife smile fatuha tayi tare da lumshe ido cikin cool voice sadiq yace fatuha bani da abinda zance sai dai Na gude ma Allah daya baki ni ban taba tunanin zan shiga wuni hali saboda rashin ki ba hannu fatuha sadiq ya janyo tare da daurashi saitin zuciyar shi yace fatuha ke ce rayuwa ta idan babuke babu ni bana jin zan iya rayuwa babu ke I love u form the bottel of my heart ya ida zancan yana langwabe kai yace please ki ce kina so na please ya ida zancan kamar qaramin yaro rungeme shi fatuha tayi tana hawayan farin cikin zame jikin ta ta yi tana qoqarin ta shi riqe ta sadiq yayi yace baki ce komai ba rufe fuska tayi tare da saurin shigewa toilet jingina nayi jikin kofar tana sauke ajiyar zuciya tana smile cike da farin ciki ta gabatar da alwala ta fito har ta fito sadiq Na binta da kallo ta gabatar da sallah tana idar wa majeed ya shigo da take away ya aje tare da shafa kan sadiq pack ya mai tare da sakin lalausan murmushi yace please for give me bros lumshe ido sadiq yayi yace mention not tare da laqace mai hanci dariya sukayi lokaci daya sannan majeed yace ai saika miqe ka warke tunda ga muradin ranka kusa da kai ya ida zancan yana kashe ma sadiq ido duka sadiq ya kai mai na wasa ya goce tare da qarasowa saitin kunnan shi ya mashi wata magana dariya suka saki a tare majeed ya fita da sauri yana cewa mu dai asuba ta gari dariya sadiq yake har da yar kwalla pack fatuha tamai tace mai kyau me yace ma haka har ya saka wannan dariyar smile yayi yace zaki Sani amma not now amma very soon zaki ji ya fada yana kashe mata ido murmushi tayi tare da janyo lafiyayan abinci ta fara feeding nashi yana amsa.

Ko da majeed ya koma masaukin su fatima Na wanka cikin toilet daure da qaramin towel ta fito ganin shi zaune saman bed yasata yan noqe noqe ta fara shirin duk kunya ta isheta shima rage kayan jikin shi yayi ya wuce toilet ya watsa ruwa tare da dauro alwala ya fito,

Shiryawa tayi cikin pink night dress masu kyau masha Allah ta yi kyau sosai Kuma kayan sun hauta saman bed ta hau tare da shigewa cikin blanket tayi lamo ko qala majeed be ce mata ba shima ya shirya sai da ya gama shirin shi yace fatima a hankali ta dago yace mata tashi ki ci abinci dan smile tayi tace Na koshi ai naci abinci a asibiti ai wannan daban ne dana asibiti ki tashi mana ya ida zancan yana langwabe kai ba musu fatima ta tashi zaune tare da zama saman carpet kaza ce lafiyayan majeed ya bude tasha rumo ta gaji a hankali majeed. ya rinqa

feeding din fatima tana amsa sai da suka ci suka koshi sannan ya dauke komai tare da bata umarni ta dauro alwala, brush tayi tare da dauro alwala haka shima majeed tare da ja masu sallah raka'a biyu suka godewa Allah, bayan sun idar majeed ya kama kanta ya mata addu'a sannan ya dauke ta kamar baby sai kunya take ji ya daura ta zaman bed kissing nata ya fara cikin salo yana shin shin kamshi turaran ta ganin zasu wuce gona da iri ya Sani fita jiki a sabule har ina tuntube saboda harara da majeed ya wurgo min😒

Ko da naje part din su basma shima kulle yake jiki asabule na dawo parlour ina wurga ido😒

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* Realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

95_96

*_this page is for you Anuty khadiya hamu nadabo tare da daukacin mosayan wannan novel ina son ku irin sosai din nan_*❣❤🤸🏽‍♀️

Washe gari ko da fatuha tana gama wanka, ta taimakawa sadiq ya tashi shima ya shiga toilet. sanye da towel ya fito yana goge jikin shi da qaramin towel, lalausan murmushi ya sakarwa fatuha wanda ke zaune saman kujera a hankali ya qaraso kusa da ita tare da yi mata pack

lumshe ido tayi tare da ware su  tace "Uncle ina kwana?" lakace mata hanci yayi yace "Ina kwana sweetheart? rungume ta yayi a jikin shi suna jin bugun zuciyar junan su" lamo fatuha tayi a fafadan qirjin shi tace "Uncle?" dan bata fuska sadiq yayi yace "Sweetheart bana san wannan sunan? Kawai kice my love " kallan shi fatuha take cike da so tace "to mikake so nace?" ki zabi wani suna mai dadi a part form uncle smile tayi tare da cewa to habibi na smile sadiq ya saki tare da cewa please qara fada naji maimaitawa tayi tana qoqarin zame jikin ta riqeta sadiq yayi yace "Ina zaki baki gama shirya ni ba?" zaro ido fatuha tayi tana rufe fuskarta" janyo ta ya kumayi jikin shi yace "My love yau fa ke zaki min komai ko mai bana iya shafawa?" rufe ido fatuha tayi tace "Um ni dai..." bata ida zancan ba ya hada baki'n su gori guda yana mata French kiss me cike da salo tuni jikin fatuha ya fara mutuwa dan saki'n ta yayi yana kallan ta. lumshe ido fatuha tayi a hankali ya hura mata iskar bakin shi mai sanyi ware ido tayi tana kallan sadiq tare da janyo lotion ta fara bin ko ina na jikin shi tana shafa mai riqe hannu ta yayi yace "My love ni gaskiya na warke yau zamu koma gida?"  dariya fatuha tayi tare da taba goshinshi tace har yanzu da sauran zazabi. dariya sadiq ya saki yana mata cakulkuli tana gantsarewa da dariya.

Ko da na leqa masaukin su fatsima😂 zaune take saman bed tana ta sheqa kuka. majeed da yanzu ya fito yana goge jiki'n shi da qaramin towel lagwabe kai majeed yayi tare da qarasowa kusa  da ita cikin cool voice yace "Please kiyi hakuri kukan ya isa haka mana my love? tun jiya kike abu daya har kin sama kanki ciwo kai ya ida zancan yana janyo ta jikin shi" zamewa tayi tace "Ban qara yadda da kai wallahi? ta ida zancan tana qara rushewa da kuka, ni ka matsa ka ban guri" smile majeed yayi tare da dago da face nata please my love kiyi hakuri bazan sake ba. Kuma fa kowa da kika gani da haka ta fara, kuma har da ke kin fiye dadi da yawa shiyasa nayi baji ba gani. but am so sorry ya ida zancan yana langwabe kai murgada mai baki  fatima tayi tare da qoqarin kwantawa , yace "Please ki tashi ki sha magani?" bata musamai ba ta miqe ta amshi magani tana gama sha ta koma ta kwanta shima yana gama shirin shi,ya kwanta tare da janyo jikin shi.

Kuka take har da shishiqa, Khaleed ne ya ce "Please sweetyna kiyi hakuri mana tun jiya fa kike kuka nan gashi har da safe please ki daura ki ci wani abu please? ko ruwan tea ne" kuka basma ta kuma saki tace "Ni ka kyaleni? ni da ka so ka kashe ni jiya? Ta ida zancan tana kuka lalashin ta Khaleed ya shiga yi da kyar ya samu ta sha ruwan tea sannan ya balo mata gani ta sha lol amare ansha jiki😂🤣 fatuha nan nan tafe itama😂😜.

Kiran sallah azahar ne ya tashe su daga bacci, majeed ya taimaka ma Fatima ta dauro alwala  . shima yayi tare da jansu sallah suna idarwa ya mata pack tare da cewa " Sweety na bari naje asibiti na duba lafiyar sadiq? to tace mai tare da tashi itama zata bishi" langwabe kai majeed yayi yace "My love ki zauna gida ki samu hutu"  to ta ce tare da komawa ta kwanta.

Yana fitowa ya h'adu da Khaleed shima zai fita. tare suka fice zuwa asibiti cikin sallama suka

shigo lokaci fatuha na feeding din sadiq lunch, murmushi ta saki tare da tanbayar su ina su fatima? kallan juna su kayi a tare su uku suka kashe ma juna ido. gyaran murya majeed yayi yace "Suna gida suna sauke gajiyar tafiya lol 😂" wata dariya sadiq ya guntse, sa kai tayi ta fita.

Da misalin karfe 4:00pm jirgin su mom ya sauka London basu zame ko ina ba sai asibiti, lokaci suma su fatima sun zo kuga murna ba'a magana haka mom ta rinqa nan da su ita da umma haka su abba ba wani ban ban ci a tsaka nin suru , sai tsantsan soyayya. inda sadiq ya dak'e shi ya gaji da zaman asibiti? hakuri aka bashi tare da cewa sai ya warke sosai.

Kwanan su mom biyu aka sallami sadiq d'aga asibiti, tare suka dawo Nigeria da yama likis driver din sadiq ne suka zo da yaran shi su ola suka dauke su sai gida. suna isa gida majeed ya dau fatima sai gida haka shima Khaleed.

Angel tana ganin sun dawo tare da albishir murna ba'a magana, haka ta rinqa rungume su tana masu pack tare da basu chocolate saboda abin ya mata yadda take so. mom kuma ta haura upstairs ita da abba ya rage d'aga fatuha sai sadiq itama dak'i ta wuce, sadiq kuma ya wuce masallaci sallah ta gabatar tare da watsa ruwa night dress din ta zura tana shafe jikin ta da lotion a hankali taji an bude kofar daki'n, waigowa tayi sukayi ido 4 da sadiq murmushi ta sakar mai tana cigaba da feshe jikin ta da turare. a hankali ya qaraso tare da rungume ta ta baya yana shinshina kamshin turaran jikin ta wani irin fisgar shi yake, take nan jikin shi ya fara mutuwa cikin cool voice din shi yace dai-dai saitin kunnan ta "My love yau fa ba anan gidan zamu kwana ba? a gidan mu zamu kwana" bata fuska fatuha tayi tana qoqarin zame jikin ta kissing nata ya fara ko ina tuni tayi laqwas. cikin sanyin murya yace "Kin taba ganin amarya tayi amarci a gidan su? so kike mom ta Kore mu ko? ya ida zancan yana daukar ta kamar baby" lafewa tayi a fadadan qirjin shi gashin ta ya baje mai a fuska bai zame da ita ko ina ba sai gaban motar shi....

*Lol har kun baza kunne .....Hhhhhh muje zuwa*😂😜

_kuyi hakuri da wannan page din am sick that is why Insha Allah ina jin garas zan muku page me dan yawa._

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERSFORUM.COM

97_98

Suna isowa hadadan gidan su parking Sadiq yayi a parking space tare da zagayuwa ya dauki fatuha kamar baby sai shagwaba take zuba mai,

Bai dire ta ko ina sai bedroom din shi, tare da yi mata pack a goshi sannan ya shige toilet, daki'n fatuha tabi da kallo tana mamakin irin qayatuwar daki'n da tsaruwar gidan. pics din su na su uku ta h'ango manne a bangwan daki'n. sai wanda t'ake ita ka dai da wanda su kayi tare da sadiq suna dariya abin ba qaramin qayatarwa yayi ba,

Sanye da bathrobe ya fito yana goge jikin shi da qaramin towel, gaban dressing mirror ya tsaya yana shafa ma jiki'n shi lotion mai kamshi tare da feshe jikin shi da body spray mai kamshi da sanyin dadi. fatuha d'ake zaune saman bed sai qarewa halittarsa kallo take tare da qara ganin tsatsan kyan sadiq, lalai sadiq ya dace da akira shi da handsome. a hankali ya qarasa wardrobe ya ciro night dress din shi sababi white ya saka sannan ya juyo yana kallan fatuha killing smile din shi ya mata tare da d'aga gira yace "Wannan kallan fa my love?" murmushi fatuha tayi tare da rufe face nata, shi ma SadiQ murmushi yayi tare da fita. kitchen ya shiga tare da dako ledar kaza da juice masu sanyi sannan ya dawo bedroom,

A hankali ya qaraso kusa da fatuha yace cikin cool voice din shi "My love tashi ki sama cikin ki wani abu kin ji? nasan ba kiyi wani dinner ba" tashi tayi suka dawo saman carpet sadiq ya bude kaza ( *d'aga gani zatayi d'adi nima har sai da miyau na ya tsinke*😋lol) a hankali ya shiga feeding nata tana ci shima yana ci ,sai da yaga ta koshi sannan ya bata juice mai sanyi Tasha.

Bayan sun kamala ci sadiq ya dauk'e ta sai toilet, brush ya mata yana mata tana zuba mai shagwaba ala dole itama sai tamai ,haka shima ya bata ta mashi tare da dauro alwala suka

gabatar da sallah raka'a biyu suna mai gode wa Allah da ya cika masu burin su, waigowa sadiq yayi ya dafa kan  fatuha ya mata addu'a sannan ya dauke ta k'amar baby ya dire ta saman bed. nan ya fara mata cakulkuli dariya tak'e kyakyatawa sosai sai da yaga harwani shidewa takeyi saboda dariya shine yasa ya kyale ta. yana kallan face nata mirginawa yayi tare da lumshe ido yana kallan p.o.p, a hankali fatuha ta mirginu tare da lafewa saman fadadn qirjin shi ta wani qanqame shi tana maida numfashi, hannu sadiq yasa ya kashe  fitilar d'akin, a hankali ya fara shafa ta yana yi mata tafiyar tsutsa  wani irin d'adi fatuha take ji tak'e nan jikin ta ya fara mutuwa saboda rikitattun sakwonin da sadiq yake aika mata,  kissing nata ya fara ko ta ko ina  a hankali ya lalubu lips nata ya fara mata French kiss  mai rikitarwa, ganin zasu Lola  ya sani qoqarin fita ashe Anuty Raheenat na rabe wai sai taga yadda za'a kashe arna😉 tasa keyar ta nayi  muka fice baki'n kofa muka tsaya , jin wata rikitata qara yasa ni tsale na koma parlour  Anuty Raheenat tace "Gobe akwai gashi😆".

*Asuba ta gari*

Kuka fatuha take ta sheqawa ,a hankali Sadiq ya miqa hannu ya dauke ta kuka ta kuma samai tana cewa " Ni ka kyale no? cikin dashashiyar muryata" zama sadiq yayi  tare da sa hannu yana shafa mata kai yace "Am sorry" kuka ta  saki saboda tuna  azabar da tasha. daukar ta kawai Sadiq yayi sai tsala tsale take ya sake ta be dire ta ko ina ba sai cikin ruwan dumi. miqewa tayi tana qoqarin fita ya mai data kuka ta saka mai tace "Dama har yanzu mai kyau ba ka dena cin zali ba? Kuma wallahi yau gida zan kwana?" sadiq bai ce mata komai ba sai ma tausayi  da take bashi, dan ba qaramar dirza yayi  mata ba ko a hakan ba ko shi yayi ba kawai ya tausaya mata ne. da kanshi ya mata wanka sannan ya fito ya barta tayi wankan tsarki, ko da ya fito bedsheet  ya cire ya canza wani tare da qara gyara daki'n ko da fatuha ta gama wanka kuka ta qara saki saboda ta kasa fitowa, jin kukan yayi yawa yasa sadiq komawa toilet din zaune ya same ta, harara ta aika mai shikenan ka mai dani musaka ta ida zancan tana rushewa da kuka. abin dariya yaso ya bama sadiq daukar ta yayi  sai saman bed. taimaka mata ta shirya tare da zura hijab, shima a gurguje ya shige toilet yayi wanka yana fitowa jalabiya ya zura tare da jansu sallah bayan sun idar  ya maida ta bed. a hankali ya janyo ta jiki'n shi ya rungume  ya fara cewa "Fatuha Allah ya sa maki albarka bani da baki'n da zan iya gode maki my wife? kin sani farin ciki mara musaltuwa kin kore min duk wata damuwa my love? naji dadi da kika kilace min kan ki har wannan lokaci? nayi maki alqawarin zan baki farin cikin har qarshan rayuwa fatuha" wani irin dadine ya lulube fatuha tare da jin Son mijinta na qara narke mata a zuciya. lamo tayi a jikin shi tana sauke numfashi a hankali y d'ago da face nata yayi mata pack am sorry my wife, nasan na wahalar dak'e amma ai be ida zancan ba fatuha ta hada bakin su guri guda tana mai French kiss. take ta qara rikitashi da salon ta ganin zai zarce tasa mai kuka, dariya yayi tare da ja mata hanci yace "Matsoraciya kawai" naji din ba komai kuma gida zaka mai dani wallahi" lalai kam kwarankwatsi ba inda zaki ya fada yana kallan fatuha, dariya suka saki a tare yace "My love akwai drama?"  ida zancan yana laka ce mata hanci qara matse ta yayi suka shige blanket suka koma bacci.

Basu tashi ba sai kusan shadaya.  a hankali sadiq ya zame jikin shi tare da shiga toilet, ya qara hadawa fatuha ruwan dimi daukar ta yayi ya kaita toilet yana dire ta ta bude ido tare da lumshe su, da wani kunyar shi take ji a wannan lokaci. ruwan dadi ya mata taji dama dama, Sannan ya mai dota bedroom shima ya koma yayi wanka ko da ya fito ta shirya cikin riga da sket na atamfa dinkin ya mata kyau sosai ga make up tasha wani lalausan smile Sadiq ya saki tare da qarasuwa ya rungume ta baya ciki cool voice yace "My love kinyi kyau?" murmushi tayi tace "Thanks" lotion ta janyo tare da shafa mai ita da kanta ta zaba mai kaya wani hadadan yadi mai tsada ta curo mai milk da ratsin brown mara kauri ya sha diki'n da dark brown zare taimaka mai tayi yasa tuni suka fito sukayi kyau.  knocking din kofar da ake ne ya sa sadiq qoqarin fita kusan a tare suka fito da fatuha parlour ta bi da kallo wani irin kyau ya mata gidan kamar ba'a qasar Nigeria 🇳🇬 take ba,

A hankali ya bude kofar baba jinmai ce riqe da kuloli ,murmushi sadiq ya saki tare da gaishe ta angel ce ta fada jikin shi tare da rungume shi tace "Daddy?" dariya sadiq ya saki ya cabe ta, qarasa shigowa baba jinmai tayi ta aje kuloli, fatuha qarasowa tayi ta gaida baba jinmai ta amsa angel sakowa tayi daga jikin daddy ta rungume fatuha smile fatuha tayi tace "I miss u angel tare da yi mata pack a kumatu"

Parlour angel ta dawo tace "Daddy ya kunna mata kallo"   kunna mata yayi  shima ya zauna kusa da ita baba jinmai ko  jan fatuha daki tayi tare da bata sakwan mom na kayan tsimi da turaru  ka  masu kamshi da shegyan tsada. Godiya fatuha ta rinqa jera mata suka fita a tare, murmushi baba jinmai tayi tace "Jidda taso mu tafi ko? bata fuska fatuha da angel su kayi lokaci daya tace " A barta anan munyi missing nata ni da baban ta ko? ta fada tana kallan sadiq" murmushi yayi tare da daga mata gira yana jin dadi yadda fatuha ke gwada ma angel so da kauna. baba jinma saki'n baki tayi tace "Alalai ni zaku ma shaqiyanci to ai shikenan ni na wuce Allah ya bada zaman lafiya" har baki'n kofa fatuha ta rako ta Sannan ta dawo parlour hannu jidda ta janyo tace "Zo muje kiyi break nasan ba kiyi ba" tashi su kayi a tare taja mata kujera Sadiq yayi ta zauna shima ya zauna Sannan angel ta zauna, saving din su fatuha tayi a hankali sadiq ya fara feeding din fatuha itama tana feeding nashi da angel sai murna suke suna jin dadi cike da so da kauna ida sadiq ya zage yana gwada masu so".

*Agurguje*

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin jin dadi,  fatuha ce tsaye gaban dressing mirror sanye da uniform kasancewar yanzu ta koma  school, yanzu haka tana SS3 kuma ita ce Head girl tana shirya sadiq cikin uniform nashi smile  yayi tare da yi mata pack yace "I love u" "love u more habibina" briefcase din sadiq ta dauka tare da school bag din ta suna  fitowa angel suka samu zaune saman dining area ta fara break gaishe su tayi tare da yi masu pack suma kujera suka ja suka fara break. bayan sun kamala fatuha ta kira yar tsohuwar me aikinta tace ta kulla da gidan Sannan karta dafa abinci sai ta dawo zata daura to tace mata tare da yi masu Allah ya kiyaye hanya. ta koma gida mota suka shige sadiq ya ja su be sauke su ko ina ba sai harabar makaranta yana parking angel ta bude kofa ta fita fatuha na qoqarin fita ya riqe ta, murmushi ta

saki a hankali ya janyo ta jikin shi yayi kissing na ta lumshe ido tayi tare da ware su a kan sadiq tace "Habibina zanyi missing naka?" nima haka my love, Sannan fatuha ta bale murfin motar ta fita,

Tana Shiga class su Zara suka dau shewa kai Head girl kina wuta wallahi, harara ta aika masu wallahi na kusa maganin ku hehe lalaima wata dariyar shaqiyanci Zara tayi tace "kwanan naga wani sheqi kike me sirin?" littafin hannu ta fatuha ta gefa ma Zara dariya suka sa zakiyi bayani wallahi ganin uncle ya shigo yasa su natsuwa aka cigaba da gabatar da darasi, kasancewa yau juma'a karfe 12:30pm suka tashi drive ne ya zo daukar su direct gida ya dire su

Wanka suka yi sannan fatuha ta shirya cikin 3 quarter pink tasa t-shirt milk ba qaramin kyau fatuha tayi ba ,sai gashinta da ta sharce ya kwanto har gadan bayan ta fitowa tayi tare da shiga kitchen, tuwon shinkafa ta daura miyar agushi taji naman rago kamshi sai tashi yake Sannan ta ahada juice din mangworo dan ba qaramin dadi yake mata ba. kwana biyu nan bayan ta kamala ta dawo dining ta jera Sannan ta koma bed ta qara sheqa wanka ta fita ta shirya cikin gown din ta maroon mai Stone's diki'n ya hauta sosai parking din gashi ta tayi jin a shigone ya sata waigowa angel ce tsaye baki'n kofa, murmushi tayi tace "Mom kinyi kyau" murmushi fatuha tayi langwabe kai angel tayi tace mom ina so naje gidan mami yau ne birthday din Jamal smile fatuha tayi tace "To shikenan amma sai kin fara lunch" dan shagwabe fuska tayi tace "Please mom kin san fa nice best friend tare zamuyi komai" ok naji ina zuwa wata hadadiyar gown ta curo daga wardrobe tare da gift tace gashi wannan gown din taki ce ita zaki sa ki tafi wani irin tsale angel tayi ta rungume fatuha tana mata pack thanks mom, Sannan ta zame jikin ta dariya fatuha tayi tare da lakace mata hanci tace "Wannan gift din kuma na Jamal ne Godiya ta mata tare da rugawa daki ta shirya girgiza kai fatuha tayi ta cigaba da abinda take. rungume ta baya akayi lumshe ido tayi tace " Habibina" ajiyar zuciya sadiq ya saki yace "My love" gabaki daya make up din ta gigitani kinyi kyau smile tayi tare da juyowa suna facing juna a hankali ya kai hannu ya warware parking din....

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏼‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opare_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www.Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.COM

99_100

1 *Month letter*

Rayuwa ta cigaba da tafiya ciki'n jin dadi, inda sadiq ya samu qarin girma dan yanzu h'aka abuja ya koma da aiki sai weekend yake dawowa kano. fatuha kuwa shirye shirye SSCE suke angel kuma JSSCE, sosai suke samu kulawa wajan sadiq inda yake fifita son su dana kowa, ya ware masu guri na musanman a zuciyar shi h'aka ita fatuha sosai take bashi kulawa da nunamai tsantsa soyayya.

Bangaran su fatima majeed ya sama mata makaranta su fatuha ta fara tun daga jss1 sosai tak'e maida hankali dan ganin taci ma burin ta,

Basma kuwa Khaleed ya sama mata admission a BUK tana karanta english, sosai take samun kulawa wajan Khaleed.

Dr yakub kuwa sai soyayya suke zubawa shi da hanan har manya sun shiga maganar.

Yauma kamar kullun wainar flower tak'e soyawa wadda kwana biyun nan ta zamar mata jiki, dan ko yini bata iyayi bata ci ba, har wata yar kiba tayi da haske komai na jikin ta ya ciko da ka ganta kasan tana jin dadi. rungume ta da akayi ne yasata saki'n murmushi tare da waigowa sadiq ne sanye da kaki'n shi hannu sa na riqe da qugunta, kallan shi tak'e cike da so tace, "Habibina yaushe ka dawo?" pack sadiq ya mata yace "Yanzu nan ji nayi bana iya hakuri rashin ganin ki har sati? gaskayi sweetheart daukarki zanyi mu koma tare?" smile fatuha tayi tare da cewa "Bari na kashe gas din nan to" kallan wainar yayi tare da cewa "Miqiqe da wannan abun?" ci tace ataqaice tana qoqarin tura wani cikin baki'n ta dan bata iya hakuri. bin ta da kallo sadiq yayi tare da cewa "Yaushe kika fara cin wannan dear?" d'aga kai sama tayi tace um na dan kwana biyu" ok yace tare da daukar ta suka haura upstairs cakulkuli ya shiga yi mata sai dariya

tak'e zubawa dan tsagaitawa yayi yana kallan face nata yace "Ina Angel?" shafa gefen face nashi Fatuha tayi tace "Tana wanjan grandma dazu da baba jinmai ta zo shine ta bita suka tafi" ok yace tare da fara kiss nata ko ta ko ina French kiss ya fara mata yana aika mata da sakwanin shi masu zafi h'aka ita fatuha ganin zasu lola duniyar ma aurata naja masu kofa na fece.

A tare suka shige toilet sukayi wanka, dauk'e da ita sadiq ya fito yana mata cakulkuli tana dariya tace "Habibina sokake ciki na ya qule ko? ta ida zancan tana mai da numfashi" lakace mata hanci sadiq yayi tare da dire ta saman sofa ya janyo lotion yana shafa mata itama tana shafa mai Sannan suka shirya cikin jeans n t-shirts iri daya jeans blue rigar red da ratsin dark blue n white wani irin kyau suka zuba masha Allah,

Parlour suka fito a tare, suka wuce dining area lafiyayan chicken and begetable stew tayi tare da cuscus da miyar kwai , tun kafi sadiq ya fara ci ya lumshe ido saboda kamshi dadi dama gashi fatuha ba baya ba wajan iya abinci saving nashi ta gama yi Sannan ta fara feeding din shi yana ci yana jin dadi gefe ga natural lemun kankana amsar cokalin yayi tare da kai mata abinci baki ta amsa tana ci zuciyar ta na tashi da gudu ta haura sama tana kakarin amai. binta sadiq yayi a baya toilet ta shige ta rinqa kwara amai kamar zata amayo yan cikin ta gabaki d'aya sadiq ya rude sai tanbayar ta yake lafiya? wanke mata fuska yayi tare da kuskure mata bak'i ya d'auke ta lamo tayi a jikin shi tana sauke ajiyar zuciya ba abinda ke mata dadi kamar turaran d'ake jikin shi kamar karya sauke ta. saman bed ya dire ta tare da komawa toilet ya wanke inda tayi aman tare da wanke toilet din ya fito gefan bed ya dawo ya zauna yana taba goshin ta. sweetheart sannu mirginuwa tayi ta lafe jikin shi tana shinshinar kamshin turaran shi tayi lamo, haka ya rinqa zuba mata sannu tare da ciro wayar shi ya kira Dr yakub ko mintin 10 ba'ayi ba yazo, sadiq yamai iso har bedroom din tana kwance sai sanyi take ji tana qudidine cikin blanket, sannu Dr yakub ya mata tare da yan gwaje gwaje tanbayar ta yayi yace me dame ke damun ki kamar mai dame kike ji, cikin sanyin murya Fatuha tace Zazabi ciwo kai da yawan tashin zuciya" rubuce rubuce Dr yakub yayi tare da bata wata yar gwal yace "Ta shiga toilet tayi fitsari a cikin ta" ta kawo mai a hankali ta tashi da shiga toilet sadiq dai na gefe sai sannu yake mata, ko 5 minutes batayi ba ta fito amsar gwalbar yayi tare da sata cikin jakar aikin shi ita kuma Fatuha ta koma ta kwanta smile yayi yana kallan sadiq yace Insha Allah zata Samu sauki indai abinda nake tunani ne sai dai muce Allah ya raba lafiya, amma for now sai mun fara yin test din tukun na" murmushi ne ya subuce ma sadiq tare da fatan Allah yasa abinda shima yake tunanine .

Har baki'n mota ya raka Dr yakub Sannan ya juyo gida, ko da ya dawo kwance ya same ta yadda ya barta. saman bed din shima ya hau tare da taba goshin ta cikin shagwaba tace "Habibina?" na'am sweetheart lumshe ido tayi tace "Zanci irin wannan abincin dana fara ci randa na zo birni?" kallan ta sadiq ya shiga yi yau kusan shekara nawa shi yanzu aka tare shi da mindiga be iya tuna me akayi ranar. cikin sanyin murya sadiq yace "Sweetheart kiyi hakuri ki fadi wani abun amma wannan bana iya tuna wa ko min akayi? ko kina iya tunawa sai a maki?"

d'aga kai tayi yace "To fadi min" shinkafa da miya da kosulo da farfesun yan'ciki to sadiq ya ce mata tare da yi mata pack ya fita,

Kitchen ya shiga ya sami baba asabe na ta goge shi, gaishe ta yayi a taqaice tare da fada mata abinda zata ma fatuha to tace mai jiki na bari ta fara aiki ,shi kuma ya koma bedroom din sai zuba mashi shagwaba take, ko da baba asabe ta gama ta kai dining area ta jera, dauko Fatuha sadiq yayi ya kawota tare da daura saman cinyar shi ya fara saving nata a hankali ya nufo da cokalin bakin ta tunkan ya kai bakin ta zuciyar ta fara tashi da sauri ta miqe riqe ta sadiq yayi yana kuma tanbayar ta kafin ya ida magana ta wanke shi da amai langwabe kai sadiq yayi yace "Sorry my wife" kuka ta saka mai lalashita ya shiga yi tare da daukar ta suka koma bedroom be dire ta ko ina ba sai cikin toilet, wanka su kayi a tare Sannan yasa bathrobe tare da nadu Fatuha ciki'n towel sai kuka tak'e mai yana lalashin ta kwantar da ita yayi yana qoqari dako lotion wayar shi ta hau ruri a hankali ya kai hannu ya dauka suna Dr yakub ne ya baya na a jikin scream din cikin sauri ya dauka tare da karawa kunne, hello Dr yakub tare da cewa albishirin ka dan tsaki sadiq yaja tare da cewa me kuma hakan ina fama da Mara lafiya kana kirana ka min irin wannan kidding din toh shikenan tunda baka San sanin maganin dan. smile sadiq yayi yace "Goro" yauwa ko kai fa amma fa sai ka bani Goran albishir to sadiq yace tare da qaguwa yaji mi Dr yakub zaice dariyar shaqiyanci Dr yayi yace angwan qauri kasha kamshi Dr ya fada yana dariyar shaqiyanci ina fama congrat madam nada juna biyu na wata 1, wani irin lalausan murmushi sadiq ya zaki yace "Wai da gaske kake?" yace eh mana, gaskiya naji dadi wannan albishiri, toh nima a bani goran albishir dariya sadiq ya saki tare da cewa na dau nauyin tafiyar ku zuwa honeymoon kowace qasa kuke so a duniya tare da Baku kudin kashe wa .wata irin dariya Dr yakub ya fashe da ita yace "Wai da gaske kake?" yace eh mana ana daura maku aure da hanan zaka ji alat sallama su kayi tare da kashe wayar juyowa sadiq yayi tare da sakar wa fatuha da lalausan murmushi itama smile tayi lotion ya shafa mata tare da samata kaya Sannan shima ya shirya kallan ta yake cike da so tare da daura hannu shi saman cikin ta yace "My love yanzu nan akwai baby na ko," kallan sa Fatuha take tace "Wanne baby kuma?" yace ko baki so ki haihune um ya fada yana kallan ta kuka ta saki tare da tashi tace Allah bana so yanzu ya zanyi da exam da ciki tun yanzu yana bani wahala bale kuma inna fara exam kuka ta saki tana cewa Allah ban so a kai kasuwa janyo ta sadiq yayi jikin shi yace "Fatuha yanzu jinane baki so? ya fada yana kallan ta" ni ban ce bana son jinin ka ba? amma ai matsamin zeyi shikenan haka zan rinqa shiga cikin su Nana da ciki ta ida zancan tana kuka kalli ka gani ko fa yau cikin ya hanani cin abinci, yi hakuri Fatuha ai duk wannan abun na dan lokaci ne. tsale tayi ta dire ita bata so sai dai a zubar har ta kai ga ran sadiq ya fara baci qoqarin fita yayi d'aga dak'i tare da cewa gobe zai auro wanda zata iya zama da cikin shi koma a inane kuka fatuha tasa tana cewa Allah ba mai shigo min gida ni ka dai ke da kai wallahi, ta ida zancan tana qara sakin kuka. abinma dariya yaso ba sadiq ganin duk tabi ta rude yasa sadiq yace mata ya fasa amma sai in zata zauna da cikin shi? amincewa tayi tare da juya mai baya tana qara sautin kukan ta,

Janyo ta sadiq yayi yana lalashin ta lamo tayi a jikin shi, cikin cool voice yace "My love mi zaki ci?" cikin shagwaba tace "Danwake" bata fuska sadiq yayi yace gaskiya babyna ba zaici mai da yaji ba, kuka ta fara shirin samai ganin ba yadda zaiyi haka ya fada ma baba asabe tayi

mata dan wake ba laifi taci dan wakyan sosai da akayi har da side plate.

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya inda fatuha ke samun kulawa sai dai cikin mai laulayi ne sosai .kusan a tare suke laulayi da su fatima amma sai dai duk ta fiso ga wani shegyan kwadayi da ya samata angel ko da taji mom na da ciki murna ba'a magana mom za tayi mata qani ko qanwa ta samu abokiyar fira.

Shirye shirye ake sosai na biki'n hanan dan yau duk kusan sun halara family house saboda yau ne za'ayi kamu, bayan sun gama exam din maths a school driver ya zo daukar fatuha be zame da ita ko ina ba sai family house. a gajiye likis ta dawo yana sauke ta tashigo gida umma ce ta tare ta, tare da hada mata ruwan wanka ta shiga toilet ta fito kasan cewar ansan yadda cikin ta yake farfesun kifi mom ta mata mai dadi tana fitowa ta iske kayanta saman bed after dress ce ta zura Sannan ta fito parlour tana fitowa ta samu su fatima suna ta kwasar suma nasu farfesun, kwabe fuska tayi tana kallan mom da itama kallan ta take dariya daki'n ya dauka mom ta janyo ta tare da bude mata kola ta fara feeding nata tana amsa sai janta suke ta fiye raki harara da rinqa aika masu mom tace taje tayi din kuma din ai kawai shuru kukayi da bakwa rakin kuma raki ba'a Sani sai ranar juyewa ammi dariya tayi tace kai hauwa kina fama da surikan nan naki wallahi, ya zanyi ammi ,komai cikin walwala da jin dadi da soyayya suke samu inda gidan maza jan nasu ya zama kamar gidan iyayan su dan yanzu sunfi mazan ma samun qugun zama har qorafi mazan keyi saboda banbanci da ake masu anfifita Matan a Kansu musanman yanzu da suke da juna biyu..

*Taku har kullun Salma mas'ud nadabo*
*CAPTAIN SADIQ*
👮🏽‍♂️

*Writing by*
*Salma mas'ud nadabo*

*Edit by*
*Raheenat*

http/mobile.Facebook.com/Real-Hausa-fulani-writers-forum
RHFWF-173984973194167/?refid=52red=opera_speed_dial_&yn=H-R

*Email* realhausafulaniwritersforum@gmail.com

*Facebook* www. Facebook.com/REALHAUSAFULANIWRITERFORUM.COM

101_102

*_Godiya ta musanman gare ku REAL-HAUSA-FULANI-WRITERS-FORUM wannan shafin naku ne, ana mugun tare irin sosai din anan Allah ya bar zuminci da qarin hada kanmu._*

Qoqari'n sa rigar ashoben tak'e da mami ta dinka masu, amma sket din ya kasa shiga saboda hips din ta da ya qaru. lagwabe kai tayi ji take kamar tayi kuka jin an bude kofa ya sata waigowa ganin sadiq ne tsaye, kuka ta fara reramai qarasowa yayi da sauri tare da dagowa da face nata "My wife me ya saki kuka?" um, wani kukan ta qara saki tace, "Habibina ashobe na ya kasa shiga? ta tun dazu nake jan sket din yaki shiga ta ida zan tana samai kuka" janyo ta jiki'n shi yayi tare da zaunar da ita saman bed yace "Wannan ne matsala?" d'aga kai tayi alama eh, toh shikenan bani kayan na gani amsar kayan sadiq yayi ya duba Allah ya taimake ta akwai space zaunawa yayi ya warware skeet din da rigar Sannan ya miqa mata tasa maqale qafa tayi ita bata iya sa kayan hannu ta nauyi yake mata, lakace mata hanci sadiq yayi yace, "My love yau baby na rigima ya saki ko?" turo baki tayi gaba cike da shagwaba kiss nata sadiq ya fara ko ta ko ina ganin ze zarce yasata samai kuka. smile yayi tare da cewa sorry Sannan ya samata kayan shima shiryawa yayi cikin manya kaya Sannan ya jata suka fito ko da suka fito lokaci su fatima sun shirya ita ka dai suke jira ta fito, tana fitowa fatima tace "Sai muje ko? ta ida zancan tana aika mata harar wasa" murguda mata bak'i tayi Sannan suka fice sadiq kuma ya wuce wajan angwayan saboda kamun ba maza.

Suna shigewa mota fatima tace "Ke h'aka ake? d'aga shiga sa kaya saiki maqale da miji" kam mikika daukan to nayi din ta fada tana aika fatima hararar wasa. dariya suka kwashe da ita a tare suka ce kin tuna san da muke zuwa gonar mai gari? dariya suka kuma saki tare da kallan juna suka yi tare da cewa Allah mun gode maka bamu taba tunanin ganin a haka ba rungeme juna sukayi tare da hade bakin su suka ce Allah ya bar mana zumincin mu har ya'ya da jikoki ameen. Fatsima harara ta aika mata ke mijina ya hana fadi wannan suna, dariya sukayi tare da cewa sannu mai miji a h'aka suka Isa wajan kamun kasancewar sune Maya Mayan qawayan amarya hada hada kawai suke biki yayi biki su Zara da Nana ma sai da suka zo ansha biki sosai sai kusan yama likis suka dawo, gidan mami suka wuce direct.

Cikin sallama suka shigo angel d'ake zaune da friends nata ta qaraso tare da rungume fatuha tace "Mom a I miss u?" miss u more dear, kin manta da mamanki tunda biki ya kama ko? to ai gashi nan ni na biyo ki bana iya hakuri kimin nisa fatuha ta fada tana shafa kanta smile tayi sannan ta koma cikin friends din ta.

Shirye-shirye ake na zuwa dinner ,ciki'n wata material lace green n black yan'matan amarya, amarya kuma na sanye da black lace mai ratsin white sosai sun fito sunyi kyau musanman da suka sha make up, cikin hadadi motaci akazo kwasarsu. fatuha ko motar sadiq ta shige wani irin lalausan murmushi ya sakarma tare da taba hannu ta yana murzawa a hankali cikin salo, yace "My wife kin sha kyau?" smile fatuha tayi tace na gode, shima yasha kyau har ya gaji yana sanye da shada milk tasha aikin hannu, ga kamshi turaran shi dake wani fisgarta, murmushi ta sakar mai me cike da sakwanni Sannan ya ja motar hannu sa daya na maqale dana fatuha.

Hall ya cika maqil anata gudanar da biki, inda abun ya zama abin sha'awa tare da birgewa musanman fatuha da Sadiq dan sadiq baya iya boye irin San da yake ma fatuha koma a inane nuna mata so yake. h'aka aka gudanar da biki inda Dr yakub yasha kyau shida amaryar shi suka gaji  sai dai mu ce Allah ya bad'a zaman lafiya.

Da misalin karfe 10:00pm taro ya watse sadiq ya wuce da fatuha gida, maqale qafa tayi ita baza ta koma gida ba ya maida ta gidan mami? cikin yan'mata amarya fir sadiq yaki saurarata haka ta cika tap kamar ta fashe, yana kunna hancin motar shi mai gadi ya bude masu geta Sannan sadiq ya shiga tare da yin parking a parking space. kashe motar yayi tare da bude murfin motar fatuha ko zaune tayi tana qoqarin fara rai ra mai kuka daukar ta yayi kamar baby ya shiga da ita gida sai rigima tak'e zuba mai.

*Washe gari*

H'aka aka daura auran Dr yakub da hannu akan sadaki naira dubu dari, sai washe bak'i yake da ka ganshi kasan yana farin cikin, ana kamala daura auran Dr yakub yaji alat account din shi kallaan sadiq yayi tare da sakar mai murmushi sannan ya mai godiya,  bayan an kamala biki ango ya dau amaryar sa sai airport inda hanan ke ta zuba kuka.

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin jin dad'i inda sadiq ke bama fatuha kulawa sosai ga exam suna tayi, alhamdulillah exam din ta zo mata da sauki sai dai har cikin ta ya dan fito.

Murna suke sosai na ganin cewa yau sun gama paper. sosai fatuha ke jin dad'i a gaskiya bata da abinda zata ce ma mai kyau ya gama mata komai a rayuwa, ko da ta fito sadiq ne ya zo daukar ta, kasancewar Saturday ne ya zo weekend gida cike da farin ciki ta qarasa gaban motar tare da bale murfin motar ta shiga. su Zara ko d'aga mata hannu su kayi tare da yimata

alqawarin sai sun zo ranar suna,

Kallan ta sadiq yak'e cike da so a hankali yak'e driver din ciki'n natsuwa har suka Isa gida, shi da kanshi ya bude mata murfin mota wata hadadiyar mota ta hango Lexus Toyota parke a harabar tsakar gidan su, kallan sadiq tayi tace "Habibina munyi baqine?" d'aga mata kai yayi tare da janta suka shige tana shiga gida ya dai ihu wasu kyalkyali suka fara zubowa a jikin ta. da flowers kallan sadiq take da mamaki pack ya mata tare da cewa happy birthday my wife🎂, janta yayi gaban cake shida angel dan kusan ita ta h'ada komai ,sai smile fatuha tak'e tare suka hada hannu suka yanka cake din parlour ya dau tafi, gutsuro cake din sadiq yayi ya bata a baki itama ta amsa ta bashi Sannan angel ta bata itama ta ba angel, pics sukayi sosai yan'uwa da abokan arziqi suka bata gift da yawa  daukarta sadiq yayi tare da maido ta harabar gida a je ta qasa yayi tare da rungume ta, ta baya tana facing din motar yace "Rufe idanuwan ki ga wani abu?" lumshe ido tayi sadiq yace ta bude tana budewa taga car key wani irin sakewa tayi tana kallan shi juyowa tayi tare da rungume shi tasa kukan farin cikin. shafa ta yake ta baya a hankali tare da zame jikin shi yasa hannu ya goge mata hawayan dariya ta saki tare da yimai pack  ta ko ina. dariya su majeed suka saki shi da fatima, murfi motar ta bude sai farin ciki tak'e  Sannan suka dawo gida sadiq ya mata alqawarin kafi ta tafi university zai koya mata driven.

*Bayan kwana* 2

Shirya kaya fatuha tak'e cikin trolley yanzu ciki'n ta ze kai 4 month, sadiq ne ya janyo ta tare da zaunar da ita shi ya cigaba da had'a kayan, sai murna take kasancewar wudil zasu d'aga nan su wuce abuja, bayan ya gama kamala h'ada kayan cikin trolley  Sannan ya janyo trolley  din parlour tare da kiran Sunday  amsar kayan yayi ya kai boot Sannan sadiq ya leqa bedroom din angel itama ta gama hada na ta kayan. smile tayi tare da yima sadiq pack ta miqa mai trolley din, amsa sadiq yayi yace "Angel kin sa komai ko? Dan karki manta wani abu" d'aga kai tayi tace "Yes daddy good girl in zaki fito ki kashe AC da komai na bedroom din" ok tace tare da nufar AC zata kashe sadiq ya fita tare da ba Sunday ya kai boot komai sun gama hadawa fatuha na sanye da atamfa an mata dinkin bubu mai kyau sai dauri da tasha tayi kyau har ta gaji ga wani haske da ta qara , angel rike da wayar ta fita iPhone 6 tana  video call da Jamal tana sanye lace Riga da sket dan yanzu ta fara zama yan'mata kashe wayar tayi tare da biyo su mom suka fita a tare. sadiq yaja mota sai da suka fara zuwa wajan, mom haka ta hada masu tsaraba sosai tare da yi masu Allah ya kiyaye hanya ita da abba sanna suka fito tare da daukar hayar wudil,

Da misalin karfe 2:00pm suka Isa ciki'n murna fatuha ta shige gida ita da angel, da gudu angel ta fada jiki'n inna dariya inna ta saki tace "Yan'mata?" kwabe fuska fatuha tayi tace "Angel dan kin ga kin fini sauri ko shine kika rigani?" dariya sukayi a tare Sannan suka shige parlour haka inna ta rinqa nan da su sadiq ko tunda ya sauke su ya wuce gona wajan baffa ya taya shi aiki sai hana shi yake amma ya qiji bari sai yama liqis suka dawo.  gaishe da inna sadiq yayi sai zuba mai albarka take Sannan ya wuce masaukin shi waka kawai yayi yana tsane jikin shi

fatuha ta shigo da kulolin abinci ta aje mai Sannan ta amshi towel din tana gogemai jiki, janyo jikin shi sadiq yayi yana facing nata cike da so a hankali ya kai hannu kan cikinta yace "Ya babyna?" smile fatuha tayi tace "Yana lafiya lau" da gaske? d'aga mai kai tayi rage tsawan shi yayi tare da kasa kunne sai tin cikin yana murmushi saboda baby sai motsi yake pack yama cikin tare da miqewa  fatuha ta taimaka mai ya shirya Sannan tayi feeding nashi tuwo shinkafa miyar kuka tasha manshanu da naman rago sosai yaji d'adi abincin.

Angel ko sai zuba ma inna surutu tak'e tana biye mata, jin tak'e kamar jikar ta h'aka itama angel saki'n jiki take da inna.

Qoqarin fita fatuha tak'e Sadiq ya riqe ta tare da langwabe kai my love, shafa gefan face nashi tayi tace "Na'am" shagwabe fuska sadiq yayi ce "Please ki kwana anan?" zaro ido waje fatuha tayi tace "Tap ba ruwana nama ji da wannan kunyar ta nuna cikin ta" dariya sadiq yayi tare da hade face nasu guru guda yace "Ai na halal ne ko kin mata?" lumshe ido tayi a hankali sadiq ya lalubu baki'n ta ya fara mata France kiss sun Dade a haka Sannan ya sake ta yana maida numfashi ,smile fatuha tayi tace I love u, Sannan ta fita da sauri , barbaza gashin kanshi sadiq yayi tare da furzar da iska bakin shi yace always loving u fatuha Sannan ya kwanta.

Kwanan su fatuha biyu a wudil hada kayan su suke zasu wuce, fatuha ji take kamar karsu tafi h'aka dai ta gama hada kayan inna sai samu albarka take tare da yi masu addu'a samun zaman lafiya mai daurewa, sadiq ko albishir ya masu daya biya masu kujera makka murna wajan fatuha ba'a magana haka ta rinqa zuba ma sadiq godiya haka su baffa da inna sannan ya fido kudi masu yawa ya aje masu da kyar ya samu baffa ya amsa, Sannan itama fatuha ta baje masu tsaraba Lace's da atamfa da shada da ta siya masu sosai su inna sun ji dadi Sannan suka dau hanyar abuja fatuha har da har kwallata ita da angel,

Sai wurin dare suka iso abuja gidan ya hadu fadin tsaruwar gidan ma bata lokaci ne, dan yafi na kano ko ina na gidan yaran sadiq ne sojoji da yawa kamar a barak h'aka suka shigo da kayan su kasancewar sunci abinci a hanya sallah kawai su kayi angel ta shige dakin da sadiq ya gwada mata a matsayin nata daki'n ya hadu dan yafi nata na kano kyau,

Haka suma daki'n su fatuha ya hadu iya kar haduwa, har kauyanci sai da fatuha tayima sadiq dariya kawai yake mata saboda komai tayi birgeshi take.

*Washe gari*

Bayan sun kamala komai sadiq yaje da su yawo sosai sun sha yawo inda sadiq keta kulla da fatuha yana bata kayan Gina jik,i wanda zasu taimaka mata ta haihu lafiya.

3 *month letters*

Sosai ciki'n fatuha ya girma dan har mom ta ce sadiq ya maido ta kano saboda cikin yanzu wata na takwas,da yake ba yadda sadiq ya iya dan baya so tayi nisa da shi.

Shi da kanshi ya h'ada masu kaya Sannan ya kai masu boot itama fatuha ji take za tayi missing nashi Sannan suka dau hanyar kano, suna Isa kano gidan mom ya wuce da su lokacin itama fatima ta dawo gida ita da basma saboda mom ta ce baza su je gida ba a wajan ta zasu haihu har suyi arba'in. dadi ta ji ganin su sai damuwar ta ta ragu kwana sadiq daya ya juya abuja cike da kewar fatuha.

Akwana a tashi ba wuya wajan Allah, su fatuha yau da naquda suka tashi majeed mom ta kira tare da driver ya wuce da su asibiti, labour aka wuce da su su uku sun Dade suna naquda, ko da sadiq ya iso gari d'aga airport asibiti kawai ya wuce yana Isa lokacin yayi dai dai da haihuwa fatuha ta silibo baby boy din ta Fatima ma boy ta Haifa, basma baby girl masha Allah yaran masu kyau, musanman fatuha gaba ki daya baby sadiq ya d'ako h'aka suka rinqa murna kankace mi asibiti ya cika,

A hankali sadiq ya qaraso tare da daukar baby yana kalla smile yayi tare da kallan fatuha kiss din hannu ta Sadiq yayi yace "Thank u my wife da kika bani wannan farin cikin". Angel ma murna ba'a magana kwana su d'aya aka sallame su family house aka wuce da su,

Sosai suke samu kulawa tare da wanka da shan abubuwa masu gina jiki, ranar suna anyi shagali ba dan k'adan ba, inda dan fatuha yaci sunan abba Ibrahim ana kiranshi da aslam , Dan majeed yaci su baba khabir ana kiran shi da Walid, diyar Khaleed taci suna Khadija ana kiranta da Nana,

Suna yayi suna inda aka dinga narka kudi kamar ba'a so, anyi ciye ciye da lashe lashe Sannan taro ya watse kowa ya tafi gida cike da farin ciki aka bar masu jego,

Mom sosai ta zage tana gyaran ya'yan nata inda suke ta shan gyara jikin da tsimi wani irin kyau sukayi ga wani sheqi da suke ta zubawa. baby's kuwa sunyi wayau gasu yan duma duma saboda suna samun ruwan nono sosai kullan angel na maqale da aslam sai fatuha zata bashi mama Sannan angel ke bata shi ,dan wani irin Son duniya ta daura mashi, bata da lokaci kowa sai na aslam.

Sanye da qaramin towel ta fita d'aga bathroom tana goge gashin ta da qaramin towel ,gaban dressing mirror ta tsaya tare da janyo lotion , sadiq ta hango ta cikin mirror wani irin lalausan murmushi ta sakar mai a hankali ya qaraso tare da rungume ta tabaya yana shinshi na kamshi jikin ta lumshe ido fatuha tayi tana amsar sakwanin sadiq, qoqarin cire towel di'n yake ta riqe tana kallan shi ,lumshe ido yayi yace, "Please" shiru tayi bata ce komai ba, daukar ta kawai yayi ya daura saman bed ya fara aika mata sakwani da zafi zafi gani zasu Lola yasa na silalewa na fice.

Shiryawa tak'e cikin atamfa riga da sket cike da shagwaba tace "Habibina gaskiya ka tashi ka fita bana so mom ta zo ta gan ka? tana ganin ka zata gane ta ida zancan tana parking din gashinta" smile sadiq yayi tare da rungume ta ta baya yace "Um my love baza ta gane komai ba kinji?" da gaske daga mata kai sadiq yayi alamar eh tare da Ciro wasu takadu gada aljihu shi ya miqamata ,wani irin tsale fatuha tayi tare da qara qaqame shi ba ko mai bane sai admission na north west university,

Da sauri fatuha ta fita tana kwalawa mom kira, fitowa tayi d'aga kitchen ta ce na'am fatuha fadawa tayi jikin mom tare da nuna mata admission murna mom ta tayata tare da yima sadiq godiya sosa keya yayi angel itama fitowa tayi riqe da aslam amsarsa sadiq yayi yana mashi wasa, haka su fatima suka rinqa taya fatuha murna.

3 *years letters*

Sosai fatuha ke maida hankali a karatun ta tana karanta law yanzu haka tana level 2, aslam yayi wayau sosai dan har tafiya yana yi ba ida baya zuwa zai kai year 2 ga surutu tsiya komai ya gani sai ya tanka angel kuma na SS2 an fara zama yan'mata.

Yauma kamar kullun a gajiye ta dawo d'aga makaranta tun safe taje school sai 5:00pm suka gama lectures ,ga wani irin kasala da take ji aslam ne ya rugo da gudu d'aga jikin baba asabe ya fada jikin fatuha, daga shi sama tayi tana chabe shi yana dariya zaunawa tayi Saman three star tare da gaida baba asabe amsawa tayi tare da shigewa kitchen aslam zama yayi saman cinyar ta yana zuba mata surutu, cakulkuli ta shiga yimai yana dariya tsagaitawa tayi tace "Ina yaya ?", daga kai yayi cikin tsamin murya yace yaya na bacci ok fatuha tace tare da tasha ta shige bedroom bata zame ko ina ba sai toilet ta sheqa wanka ta fita tare da gabatar da salolin da ake bin ta. turo kofar da akayi ne ya sata smile angel ce tsaye bakin kofar sanye da jean n t-shirt tace mom sannu da dawowa, yauwa fatuha tace qarasowa tayi tace mom ki zo muyi lunch tun dazu na dawo d'aga school naqi cin komai sai kin dawo, murmushi fatuha tayi tace " Karki qara barin kanki da yunwa kinji angel?" d'aga kai tayi tare da cewa ai nasha fresh milk ok muje dining area suka wuce lafiyayan doya ce da miya tasha Kaji da naman rago sai kamshi ke tashi sosai fatuha taci abinci dan wani irin San doya take kwanan kusan kullu sai ta ci ga wani ci

da take yanzu kamar runbu da san bacci har mamaki kanta take, bayan su kamal suka dawo parlour suna kallo  aslam sai wasa yake da kayan parlour komai ya gani abin wasa ne da an hana shi sai kuka yace zai fada ma daddy , yanzu ma haka bana yake fatuha ta janyo shi tana mai fada kuka ya sa mata kamar ta daura mai wuka sadiq da shigowar shi yanzu kenan harara ya aika ma fatuha tare da daukar aslam ya wuce da shi, tabe baki  fatuha tayi tare da bin bayan shi ko kallan ta beyi ba sai wasa da yake ma aslam yana dariya miqa hannu tayi ya bata aslam din harara ya kuma aika mata  yace "Baki shi zanyi ki ida kasheshi ko?" mi ya  ida zancan yana qara rungume aslam dariya fatuha tayi tace "Dama ka bani shi saboda yanzu zai fara daura ma headache" hmm  kya Mayi baya ni na kama ki kina dukar min da janyo ta Sadiq yayi yana kai mata naushin wasa shi da aslam dariya take sosai rungume sadiq tayi a hankali yake shafa bayan ta yace I miss u zame jikin ta tayi tare da kashe mai ido ta dauki Islam ta maida shi parlour tare da dawowa taimaka ma sadiq tayi ya cire kayan shi suka shige toilet maqale da jun,a suka fito suna ta zuba soyayya.

4 *Years letter*

Wata kyayakwar yarinya ce wadda baza ta wuce  4 years  ba ta shigo parlour tana kuka ta fada jikin sadiq manne yake da farin glass a face nashi yana sanye da English wears ga wani kyau ya qara da girma. cikin shasheqar kuka tace "Daddy kaga yaya aslam ya amshe min baby wasa na? daukar ta yayi yana lalashi sorry little mom" fatuha ce ta fita sanye da green lace taci kyau har ta gaji tace "Wai me yasa aslam be jin magana ne?  zai shigo gidan ya same ni ai ?"sorry dear, yar yarin yar da ke jiki sadiq sunan ta kausar amma ana kiran ta da little mom saboda sunan margayiya kausar aka saka mata sosai fatuha ke ji da ita saboda ita da kanta tasa sadiq yasa sunan. Yanzu haka sun koma abuja da zama fatuha ta gama karatun ta aiki take angel kuma na university .

Kasancewar lokacin lunch yayi kowa ya halara a dining area suna lunch suna dariya sadiq ne ya curo wayar shi dake aljihu yace selfy su duka suka matso tare da saki murmushi happy family life.

*Tamatubihamdulillah*

*_A nan na kawo karshan wannan littafi nawa captain sadiq, ina mai miqa godiya ga dinbin masoyan wannan littafi._*

*Abinda muka fada dai-dai da wanda bamu fada dai-dai Allah ka yafe  mana.*

*_Ina godiya irin sosai din nan ga Anuty  Raheenat da ta bani goyan baya wajan rubuta wannan labarin tare, Damin good editing dan ya qayatar da masoya wannan novel,  ina miqo godiya ta irin sosai din nan muna mugun tare._*

*_Gamai buqatar littafi na ga number ta kamar h'aka_* 07063683025

*Gargadi: Ni Salma Nadabo ban amince kowa yayi anfani da littafina Captain SadiQ tako wacce Si ga, duk wadda tayi\Kayi na bar mutum da rabill izati dan haka a kiyaye.*

*Taku har kullun salma mas'ud nadabo*